[
*YARIMA FUDHAL*

*©FIDDAUSI S.A*
(QURRATUL-AYN)

01

BISMILLAHIR RAHMANIR RAHIM.......!

DUKKAN YABO DA GODIYA SUN TABBATA GA ALLAH MAD'AUKA KIN SARKI MAI KOWA MAI KOMAI.

INA ROK'O AGARESHI YANDA YA BANI IKON FARA LITTAFIN NAN LAFIYA, YA BANI IKON KAMMALA SHI LAFIYA AMIN.

TSOKACI

WANNAN LITTAFIN K'AGAGGEN LABARI NE BANYI SHI DANCIN FUSKAR WANI KO WATA BA, FATANA KAWAI AL'UMMA SU AMFANA DA DARASIN DAYAKE CIKIN SA.

BANYAR DA WANI KO WATA YA JUYAMIN LITTAFINA TA KO WACCE SIGA BA DUK WANDA YA JUYAMIN LITTAFI KO YA CIRE SUNANA ZAN BARSHI DA ALLAH KAWAI.

*********************************

**

Gida ne tamfatsetse mai dogayen katangu da suka sha zane mai d'aukan hankalin wanda yake kallo,  hakanne zai baka tabbacin cewa gidan sarauta ne.

Haka kuma girman gidan zai baka mamaki kai kace gari ne guda.

Gidan na d'auke da b'angare guda bakwai, banda filin shamaki da k'afa bata iya kaiwa k'arshen sa.

Soron fada shine soro na biyu a cikin gidan, sai kuma soraye uku da za ka sake wuce wa da zai sa da ka da farfajiyar gidan, a nan ne za ka ga b'angare har guda shida. B'angaren Mai Martaba sai b'angaren Mai Babban d'aki, sannan wajen Matan sarki guda biyu, sannan b'angaren yaransa, sai can ciki kuma b'angaren bayi ne tare da ma'aikatan gidan.

Sai kuma b'angaren kwara-kwaren sarki daban sannan kicin a can k'arshen gidan, sai shamakin doki da shamakin tsakar gida.

°°°°

Gidan ya hargitse baki d'aya, jama'ar gidan sai kai kawo suke daga tsakar gida zuwa sauran sassa na gidan.

Hakan ne zai tabbatar maka da wani muhimmin abu ne yake shirin faruwa a cikin gidan.

"Allah ya taimaki  sarki ina mik'o gaisuwa, Yarima Fudhal na kan hanya duk kan jama'ar gari kowa na marhabin da dawowar sa".

Murmushi sarki ya yi wanda ba'a iya ganin sa sabida rawaninsa daya rufe rabin fuskarsa, amma duk wanda ya kalli fuskarsa zai san ya yi farin ciki da jin wannan maganar.

Fadawa suka hau fad'in' "Sarki ya amsa gaisuwa kuma ya yi farinciki  da kyakkyawan albishir d'in ka".

Waziri Salmanu ya d'an rusuna gaban sarkin shi ma yana mik'a tasa gaisuwar tare da fad'in' "dole kowa yayi farin ciki ya mai Martaba, domin yau kimanin shekaru goma sha biyar kenan rabon Yarima Fudhal da k'asar nan, gashi kuma yau zai dawo k'asarsa cikin k'oshin lafiya tare

da nasarori masu tarin yawa".

Shi ma Fadawa suka amsa masa da' "Sarki ya amshi gaisuwarka ya kai babban waziri ".

Haka dai kowa ya dinga kawo gaisuwarsa  Fadawan sarki na amsa masa.

Sarki ya cika da murna da farin ciki ji yake kamar yajawo goben yaga Yarima kuma d'a mafi soyuwa a gareshi.

Mai Martaba Sarki Ubaiyd kenan, ya gaji sarautan a wajen mahaifinsa sarki Salmanu. Shi kad'ai ne d'a a wajen mahaifin nasa bashi da wa ba shi da k'ani. Shiyasa yakeji da iyalinsa sosai musamman Yarima Fudhal wanda yake ganin shi ne magaji a bayan sa.

Sai dai wani abu dake b'atawa mutane rai da Sarkin kuma basu da ikon magana akai shine.

Sarki Ubaiyd ya tsani a fad'i laifin yaransa, shi a ganin sa komai sukayi dai-dai ne.

Domin 'ya'yan sarki ne kuma jikokin sarki 'ya'yan masu fad'a aji a cikin k'asar, a ganinsa kome suke so suyi kuma komai sukai dai-dai ne.

Abin da mutane suka kasa fahimta kenan rashin 'ya'ya da yawane ya sa shi yin hakan, ko kuwa son nunawa duniya yaransa sunfi kowa ne?.

••••••••••••••

Mai Babban d'aki Hajiya Marka mahaifiya ce ga mai martaba sunanta na gaskiya Hauwa'u.

Mace ce kamila mai son addini ga faram-faram da son jama'a, ga kuma uwa uba fad'a aji in dai taja layi a gidan ko sarkin k'aryarsa ya tsallaka balle kuma sauran al'ummar gidan.

Fulani Bingel itace uwar gida a cikin gidan mace mai alkunya da addini da son mutane, tana girmama dukkan mutumin daya girmama ta ba tada wulak'anci ko kad'an gata da son ado.
Yaran ta uku, mata biyu an aurar dasu Sadiya da Sa'idah  sai autan su Yarima Fudhal.

Sai Fulani Sokoto mace ce fara doguwa mafad'aciya ce tak'in k'arawa. Gata makira tasan luggar tuggu kala-kala, duk bayin gidan suna tsoron ta ainun, domin sarki yana yarda da maganarta d'ari bisa d'ari.

Tana da yara biyu Mace da Namiji Jalil da Jalilah su kad'ai ne yaranta a gidan.

Sai uwar Soro babar kwarkawara ce ta sarki, Sauran kwara-kwaran sarki guda biyu duk babu wadda ta tab'a haihuwa a cikinsu.

************

Kishingid'e take bisa kushin tasha ado kamar babu gobe sark'ar gwal ce dank'areriya a wuyanta hatta warwaro da 'yankunne zuwa zobuna duk na gwal ne. Tana sanye da wani dank'areren less fari da ta d'ora alkyabba bak'a akai.

Gefe guda farantin kayan marmari ne ajiye sai bayi uku mata zaune a gabanta suna mata hira jefi-jefi.

Jakadiyya ce ta shigo da sallamarta ta zub'e bisa carpet tana gaishe ta.

Fulani bingel ta amsa fuskarta cike da annuri tana duban jakadiyya da kanta yake k'asa.

Jakadiyya ta cigaba da magana ba tare da ta d'ago kanta ba'

"Gani Gare ki, naji ance kina nemana ?".

Fulani ta sake fad'ad'a murmushinta, kafin ta bud'e baki ta fara magana' "Inaso a shirya dukkan abinda ya dace domin tarbar Auta na, sannan a canja masa bayi wad'anda ki ka amince dasu".

"Angama ya shugaba ta".

Daga haka Jakadiyya tamik'e ta fice, ta nufi b'angaren bayi domin cika umarnin Fulani Bingel.

Nan da nan ta gama bawa kowa aikin sa, an gyare b'angaren su Yarima tsaf.

An kuma gyare masa d'akinsa duk da cewar baya nan amma d'akin fes domin kullum ne sai an share an goge shi.

"Yanzu Mama wannan Yayan namu na dawowa Sarki zai daina bi takanmu fa, baya nan ma ya aka cika bare kuma ya dawo".

Cewar Jalil kenan yana kishingid'e a gefan mahaifiyarsu.

Yaro d'an kwalisa kenan mai shekara ashirin da bakwai a duniya. Jalila dake kwance kan cinyarta taci gaba da fad'in' "ai ina jin ma mance zai yi muma 'ya'yansa ne, gaskiya Fulani ta cuce mu wallahi da take k'ok'arin rabamu da mahafinmu".

Fulani sokoto ta d'an tab'e baki tare da murmushi tana shafa kan d'iyar ta ta.

"Haba dai ita d'in me?, ai ko tana yawo da guraye k'aryarta ta rabaku da mahaifinku ku dai ku zuba ido ba ga ni ba?".

Sallamar d'aya daga cikin bayin gidan ne ya katse su daga tattaunawar da suke.

Baiwar ta fad'i gaban Fulani sokoto tayi gasuwa tana fad'in'
"Da girman kujerar ki uwar magajin gobe, hak'ika na jiyo wani batu mafi girma!".

Fulani sokoto ta mik'ar da Jalila da ke kwance bisa cinyarta tana duban Baiwar ta ta domin jin batun da tazo mata dashi.

"Ina jinki Ladidi".

"A gafarce ni Uwar Magajin gobe, albishir mafi muni ne ke tafe da ni, Fulani Bingel ta saka Jakadiyya ta canjawa Yarima Fudhal bayi,
bayan duk mun gama shirin mu a kan tsofaffin bayin nasa".

Fulani Sokoto rik'e kai kawai tayi ba tare da ta iya cewa komai ba tsabar takaici, ta yiwa Ladidi nuni da hannu akan ta tashi tafita, nan da nan Ladidi ta mik'e ta fice jiki na b'ari.

"Yanzu Mama meye abin yi?".

Jalila ke tambayar Fulani Sokoto da k'yar ta iya bud'e baki ta ba ta amsar.

"Zan yi tunani akan haka".

Ta mik'e tayi cikin d'akinta ta barsu nan cikin falon na ta.

*****

Jakadiyya ta sa aka jere mata 'yan matan bayin gidan kaf ta gama duba su duk ciki ba su yi mata ba kuma bata amince dasu ba, hakan yasa tace musu kawai su cigaba da aikinsu, ita kuma ta koma b'angaren Fulani Bingel.

Da shigarta ta fad'i a gabanta tana fad'in.

"Ayi hak'uri a gafarce ni na duba duk kan bayin babu wanda su ka yi, da za'a bani dama zuwa gobe da k'arfe bakwai sai a sake d'iban sabbin Bayi kafin zuwan Yarima".

"An baki dama, kiyi duk kan abinda ya dace".

"Nagode kwarai da gaske". Jakadiyya ta mik'e ta fice.

*UNGUWAR KWARI*

Unguwace da mutane da dama su ke mata ik'irari da unguwar talakawa.
Domin a ganin su babu unguwar da ta kai yawan miskinai da gajiyayyu a cikin fad'in garin kamar Unguwar Kwari.

Unguwace mara tsarin gidaje ga tarkacen bola kala-kala a cikin unguwar layi-layi, gidajen duk na k'asa mara sa kyan gani.

Amma duk da katutun talaucin da ya yiwa unguwar yawa hakan bai hana a samu wad'anda suke neman nakansu da guminsu ba. Duk da wasu jama'a nawa unguwar lak'ani da unguwar k'azamai hakan bai sa an rasa masu tsafta cikin su ba sabida ba duka aka taru aka zama d'aya ba.

Gidane na k'asa wanda katangarsa iya rabi ce kana iya hango dukkan abinda mutanan gidan suke yi a tsakar gidan.

Gidan na d'auke da d'akuna biyu kacal, sai kicin da wani kwarab'abb'an band'aki da yasha tsimmokara kala-laka domin kariya.

Gidan tsaf dashi an share shi tas ko ba tabarma sai mutum ya zauna duk da turb'ayace a k'asan.

Wata 'yar dattijuwar mata ce zaune bisa ledar buhu a tsakar gidan da sanda a gefanta.

Idanuwanta a rufe wanda shine zai baka tabbacin makauniya ce, magana take yi cikin d'aga murya'
"Aynu! Ke Aynu!! wai mai kike yi a cikin d'akin ne haka?".

Dattijuwar ke ta b'ab'atu bakin k'ofar d'akin da take zaune.

Gidan shiru kai kace sambatu take babu kowa a gidan, can aka d'ago yagaggen zaninda a ke rufe k'ofar d'akin da shi da sunan labule.

Wata 'yar budurwa ce da shekarunta ba zasu wuce goma sha biyar zuwa da shida ba ta fito da ga cikin d'akin. Tana sanye da wata kod'add'iyar atamfa da ba za ka iya tan-tance kalar taba bare ganin zananta, hijabin jikinta bak'ine amma ya zama ja tsabar dad'ewa da gajiyar wanki da rana.

Fuskarta watsai bak'ace amma ba can ba, tana da manyan idanuwa da gashin ido dana gira zara-zara, sumarta har kusan girarta hakan ne zai saka kasan tanada yawan gashi sai pink lips d'inta, duk da bak'ace. Amma leb'anta pink a tak'aice dai kallo d'aya ba zai sa ka fahimci kyawunta ba.

Wato dai tana da wani sihirtaccen kyawu na ban mamaki da ba kowa ke iya sanin hakan ba.

"Gani Ummata ina shiryawa ne fa, mai zan siyo miki?". Tayi maganar cike da shagwab'a.

Murmushi Umman tata tayi, tana mai mik'o mata wata duk'unk'unanniyar Naira hamsin  "Ungo Aynu maza je ki kisiyo mana garin kwaki da sugar musha, nasan baki karya ba ko?".

"Ehh Ummana bari in je in dawo to".

"To ki dawo lafiya akula da hanya".

"Amin". Aynu ta amsa tana mai sanya wani talitsattsan silifas da k'iris ya rage ya hudo k'asa ta sanya ta fice tana 'yan wak'e-wak'enta.

Awaje taci karo da wani mutum dake jingine jikin wani icen dalbejiya, bai da k'afa d'aya sai guda d'aya yana
dogarawa da sanda.

Durk'usawa tayi har k'asa na ji tana fad'in' "ina kwana Baba?".

"Lafiya k'alau Aynu, kin tashi lafiya?".

"Lafiya k'alau Baba, Ummata ta aikeni ne".

"Ki dawo lafiya a kula da hanya". Cewar Baban nata kenan. Ta mik'e ta ci gaba da tafiya abinta.
[07/07, 16:13] Nana Sales Aliyu Fbk Mai Quratu Group: *YARIMA FUDHAL*

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

©FIDDAUSI  S.A (QURRATUL-AYN)

02

Mintuna kad'an da fitar ta sai gata ta dawo hannunta rik'e da leda bak'a k'arama, da sallamarta ta shigo cikin gidan Ummanta dake zaune bakin k'ofa kamar yanda ta fita ta barta ita ce ta amsa mata sallamar tana fad'in.

"Har kin dawo Aynu ?".

"Ehh Ummata kinsan shagon Malami babu nisa ai".

"To dauko kwano ki jik'a sai ki d'ibarwa Babanki ki d'ibi naki".

"To Ummata".

Ta amsa tana mai shiga cikin d'akin na su, sai gata ta dawo hannunta rik'e da babban kwano da kofuna guda uku.

Ta juye garin a cikin kwanon taje ta zuba ruwan da ta d'ebo tun asuba dake basu da ruwa sai asuba famfon unguwarsu yake zuwa.

Ta d'auraye garin sannan ta sake zuba ruwa ta dawo ta zauna ta dauki sugar ta sanya a ciki ta juya, ta zubawa Ummanta ta mik'a mata sannan ta sake zuba wani ta d'auka ta kaiwa Babanta d'akinsa yana kwance ta shiga da sallamarta yamik'e ya zauna yana amsa mata sallama.

Durk'usawa tayi ta ajiye masa kofin garin tana fad'in.

"Baba gashi inji Umma".

"To sannun ki nagode sosai Allah muku Albarka !".

"Amin".

Ta amsa tare da mik'ewa ta dawo tsakar gidan inda Ummanta take ta zauna gefan ta tare da janyo ragowar garin ta hau sha.

YAMMACIN RANAR

Da yamma sai da ta kammala komai da zatayi a gidan, sannan tayi shirin islamiyya tayiwa Ummanta sallama ta tafi.

"Assalamu alaikum mutana nan gidan nan?".

Wata mata 'yar dattijuwa take ta kwad'a sallama cikin gida.

"Amin wa'alaikissalam Tasalla kece a gidan namu?, Bismillah shigo".

Umma ta amsawa matar sallama tana daga cikin d'aki.

Matar ta shiga d'akin ta zauna bisa 'yar guntuwar katifar dake yashe tsakar d'akin da bata da maraba da tabarma.

Suka gaisa da Umma tamik'awa Umma bak'ar ledar da ta shigo da ita tana fad'in.

"Gashi Umman Aynu dama abinci ne na kawo muku".

"Amma kuwa mungode Allah ya saka da alkhairi kamar kinsan tun safe Aynu ba taci komai ba wallahi, yarinyar nabani tausayi sosai k'arama da ita amma tana fuskantar gararin rayuwa !?".

"Haba Umman Aynu !, kada kice haka mana !, ko wanne bawa da irin jarabtarsa arayuwa, barema yau ina tafe da kyaky-kyawan albishir gareku ina kyauta ta zaton wasu matsololin naku zasu kau".

"To Allah yasa Tasallah wanne albishir ne haka?".

"Wato gidan Sarkin da Zainabu tawa take aiki zasu d'auki sababbin ma'aikata shine nake ganin mai zai hana Aynu taje ko Allah zai saka a dace".

Umman tad'an jin jina kai kafin tace.

"Anya kuma?, nifa kin san bana son abin da zai saka inyi nesa da Aynu ko kad'an".

"Ki yarje mata tayi aikin nan domin zaku samu alkhairi aciki, duk wannan abincin da ki kaga ina kawo muku daga gidan Zainabu ke zuwa dashi, bayan haka kuma ga kud'in da ake biya duk wata".

"To zan duba ingani Allah yasa a dace".

Cewar Umma kenan, Tasallah ta dubeta karo na biyu.

"Bawai zaki duba ba amincewa zakiyi domin nasan Babanta bashi da matsala akan hakan !, nazo miki da wannan maganar ne sabida ina da yak'inin zaku samu sauk'in rayuwar data tsananta a gare ku ne".

Tayi shiru domin taji ko Umma za tace wani abu, jin da tayi ba tace komai ba yasa ta cigaba da magana.

"Sannan aiki a gidan ya dan ganta da b'an garen da kake aiki, kinga Zainabu Fulani Bingel takewa aiki albashinta dubu goma sha biyar ne, wad'anda ke aiki b'angaren Fulani Sokoto suna d'aukan Dubu goma, to kinga ko dubu goman ne ina laifi a wajen wanda baya dashi?".

"Kinsan Jakadiyyar gidan Yayar Babar muce, shi ya sa ban ji komai ba nakai Zainabu aiki gidan sabida tana da kirki wallahi baza tab'a bari wata b'araka ta b'ullo ta gefen suba".

"Hakane Tasallah !, bari Aynu tazo sai muyi maganar, mu ko b'angaren dubu goman ta samu Allah yasa masu albarka".

"Amin, haka ya kamata kice ai".

Nan suka cigaba da tattau nawa kafin Tasallah tayiwa Umma sallama tana fad'in.

"Idan ta amince zatayi ki turota da safe kamar shida da rabi domin anaso bakwai tayi musu acan".

"Insha Allah zatazo kin san Aynu akwai himmar sammako ai".

Suka sanya dariya ta fice daga gidan, tabar Umma nan zaune tana tunani.

Batafi mintuna talatin da tafiya ba Aynu tayi sallama da sauri ta shigo gidan ta ajiye jakarta tayi maza tad'auki buta ta shig e band'aki mintuna biyar tafito ta shiga cikin d'akin ta tadda Ummanta zaune tana lazimi, Aynu ta zauna gefanta tana fad'in.

"Sannu da gida Ummata".

"Yauwa Aynu kin dawo lafiya ko?, fatan anyi karatu da yawa?".

"Lafiya k'alau Ummata, nayi karatu sosai kuwa".

"Masha Allah a dage sosai".

"Insha Allahu Ummata".

"Duba cikin kwanun da ke can rufe akwai abinci ki d'auka kici".

"To Ummata".

Tamik'e ta dauko ta zauna har tasa hannu zata fara ci sai kuma ta dubi Ummanta ta da tambayar.

"Umma kinci abincin kuwa?".

"Ehh naci 'yar gidan Umma, har Babanki shima yaci wannan nakine kici abinki".

Aynu tasa hannu ta ci gaba da cin abincin ta.

"Ummata waye da aikin ladan nan haka?".

"Kema ko ba'a fad'ab ba kinsan wace ai, Tasallah ce Babar Zainabu ta kawo mana d'azu".

"Amma Umma babu abinda zamuce da Maman Zainab sai dai Allah yasaka mata kawai".

"Amin dai, yauwa inkin gama inason magana da ke".

"To Ummata nagama ai, bari in wanko hannuna".

Tafice daga cikin d'akin hannunta rik'e da kwanun data gama cin abincin.
[07/07, 16:15] Nana Sales Aliyu Fbk Mai Quratu Group: *YARIMA FUDHAL*

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

FIDDDAUSI S.A (QURRATUL-AYN)©

03

Notes...............kuyi hak'uri nayi mistake a page 1 MAI BABBAN D'AKI ita ce mahaifiiyar Sarki, UWAR SORO babbar kwarkwara ce, Zakuga nasake post nashi na gyara ne.

***                ***             ***

Ta wanko hannunta ta dawo ta zauna kusa da Ummanta, Ummanta ta kamo hannunta tarik'e kafin ta fara magana.

"Aynu !, kiyi hak'uri abisa yanda kika tsinci kanki a rayuwa, ki sani komai yake faruwa da bawa haka Allah yatsara masa tun kafin zuwansa duniya, nasan ke mai hak'uri ce Aynu, ina rok'anki ki k'ara akan wanda kikeyi, domin bahaushe na cewa mahak'urci mawadaci, nasan wata rana sai labari".

Ta danyi ajiyar zuciya na wani lokaci, kafin taci gaba da magana.

"Mahaifinki shine ya hanamin fita neman na kaina, a cewarsa bazanyi bara ba, kamar yanda shima bazaiyi ba, amma kuma duk wani hanyar samunsa ta kulle, gashi ni bana da ido bare inyi koda sana'ar k'arfice a gida, yau Tasallah tazomin da batun idan mun amince zata kaiki gidan sarki aiki, ana samun abinci sannan da albashi duk wata".

Murmushi ne ya sub'ucewa Aynu duk da 'yar kwallar dake saman idonta, tarik'e hannun mahaifiyarta ta k'am tana fad'in.

"Amma kun amince ko Ummata?, dannima ba nason bara wallahi gara nayi ko wanne aiki indai za'a biyani mu amfana".

Ummanta itama murmushin tayi.

"Ya zamuyi Aynu?, ai dole mu amince sabida bamu da wani zab'i daya wuce amincewar tamu".

"Kai amma naji dad'i Ummata kinga yanzu zamu samu kud'i mud'inka kaya musayi ta barma da katifa da takalmi, sannan kuma ga abinci, yanzu bamu ba yunwa ko Umma?".

"Uhmmm Aynu kenan, sarkin buri arayuwa Allah dai ya warware mana !".

"Amin Ummata".

Daga haka suka cigaba da hira, Ummanta tanayi mata nasiha akan ta kula da kanta tayi biyayya kada tayi abinda za'a tsa neta ko ta b'atawa wani rai, sannan ta gargad'e ta akan ta zama mai hak'uri a duk inda tasamu kanta.

WASHE GARI....!

Washe gari tun asuba Aynu ta tashi tayi sallah tad'ebo ruwa ta cika gidan, tayi dukkan aikace-aikacen data saba kullum, tazo ta zauna gaban Ummanta ta gaisheta taje ta gaida Babanta ta dawo ta zauna tana jiran gari yad'anyi haske ta fita, domin babu agogo a gidan nasu.

A nanma  nasihar Ummanta tayi ta mata, kafin tayi mata sallama ta lek'a d'akin Baban nata tayi masa sallama shima ya biyota da addu'a ta fice daga gidan.

Yau wani nishad'i ta keji arayuwarta domin ita dama burinta na rayuwa bai wuce yanda zata taimaki iyayenta ba, wad'anda sukai d'awainiya da ita tun tana cikin ciki, duk da gararin rayuwa da taulacin dasuke fama dashi amma hakan bai hana musu ganin sun kyautata mata ba, sai taci kafin suci, sai ta sha suke sha, intayi kuka suyi kuka idan tayi farin ciki suyi farin ciki, ba dan yanda rayuwa ta juyewa mahaifinta ba tasan bazai tab'a bari taje wani guri aikatau ba, tasan iyayenta sun sota arayuwa to itama meyesa ba zata kyautata musu ba?.

Haka ta isa gidan Babah Tasallah tana sak'e-sak'e cikin ranta, da sallamarta ta shiga gidan, Zainabu dake shara ta amsa mata sallamar tana fad'in.

"Uwar 'yan sammako k'arfe shidda fa? Amma har kinzo!".

Aynu tayi murmushi ta bata amsa da fad'in.

"Amma aikin san da zafi-zafi akan daki k'arfe".

"Da gaskiyarki 'yar gidan Umma".

Babah Tasallah ta fad'a tana mai fitowa daga d'akinta, Aynu ta d'urk'usa ta gaisheta ta amsa fuskarta fal murmushi tana tambayarta ya ta baro Ummanta ta, Aynu ta bata amsa da.

"Lafiya k'alau take, tace ma agaishe da ke".

"Ina amsawa, shiga d'akin ki zauna kafin da rabin tayi".

Aynu ta shiga ta zauna, Zainabu ta gama shara ta kawo musu abin kari koko da k'osan da Babah Tasallah tayi tun asuba,  suka karya dan kada su tafi da yunwa.

6:30.

Shida da rabi dai-dai suka isa gidan Sarkin tun awaje Aynu ta saki baki tana kallon girman gidan da tsaruwarsa, sabida ita ba ta yowa nan haka, to mema zai kawota tunda ita dai bayawo take ba, Zainabu ma tayi nacin suzo tak'i zuwa sai yau da aiki yakawota.

Bata k'ara tsinkewa da al'amarin gidan ba sai da suka shiga soron fad'a anan ta sha kallo kafin su wuce zuwa ciki gidan, nan kuwa mutuwar tsaye takusa yi, aranta tana fad'in.

"Dama akwai masu irin arzik'inan aduniya?, Allah yabasu kud'i da mulki amma basu damu da talakawansu ba".

"Ke Aynu!, me kike kallo ne? ki nutsufa, duk abinda kika ga munayi kema kiyi".

Cewar Zainabu kenan tana mai tab'ota, domin taga tad'daga kai sama tasaki baki tana kallo.

Wajen Jakadiyya suka wuce kai tsaye, suka gaisheta anan suka tadda 'yan mata guda hud'u a tare da ita, 'yan matan suka hauyiwa Aynu wani kallom gani-gani kamar sun ga kashi, ita dai hankalinta yana ga kallo, bama tasan sunayi ba.

"Ga yarinyar da nake fad'amiki, 'yar gidan Malam Nasiru gurgu ce".

Babah Tasallah ta gabatar da ita wajen jakadiyya.

Jakadiyya ta k'arewa Aynu kallo kafin tace.

"Allah sarki ! Yarinya k'arama da ita kuwa, Allah yasa dai ta samu domin mutum uku ake buk'ata kuma kinga ga guda hud'u sun zo tun d'azu, ban zaci zaki kawo taba domin kina k'ila wa k'ala akan zuwan nata, amma dai bari inkaisu wajen Fulani Bingel itace zata zab'a".

Babah Tasallah tace.

"Amin dai insha Allahu zata samu".

Aynu kuwa jin ance Allah yasa ta samu tuni 'ya'yan hanjin cikinta suka murd'a gabanta yahau bugun sha uku-uku.

Jakadiyya dai ta d'ebesu su biyar suna binta abaya har b'an garen Fulani Bingel, Aynu har tuntub'e take tsabar kallo.

Suna shiga Jakadiyya ta zub'e gaban Fulani, suma sukayi yanda tayi suka kwashi gaisuwa, Aynu ta d'ago kai tana duban Fulani mace kyakykaywa mai haiba tasha ado da wani light blue d'in leshi dayasha adon stone...., jitayi an mintsineta ta gefanta dayake tana kusa da Jakadiyya

tajuyo taga dukkansu kowa kansa ak'asa itama ta duk'ar da nata.

"An samo guda biyar duk da uku ake da buk'ata sai a azab'a ko?".

Fulani ta gyad'a kai, tare da bada umarnin duk su mik'e tsaye, ba musu suka mik'e kansu duk a k'asa, ta bisu d'aya bayan d'aya da kallo, kafin tace ta gefan Aynu tayi gefe, sannan ta kuma zab'ar wata guda d'aya, yarage saura mutum d'aya ke nan?.

Jikin Aynu sai rawa yake ta tsananta addu'a sosai Allah yasa azab'e ta cikon ta ukun, domim sungama sa rai akan wannan aikin.

Cikin ikon Allah akace Aynu ta koma cikin mutum biyun da aka fara zab'a, tuni ta saki wata nan-nauyar ajiyar zuciyar.

"Wad'an nan ukun sunyi, biyun ki kai su kicin suyi aiki acan, ku kuma koware kanku".

Ko wacce ta tsaya ita kad'ai aka nuna ta farko.

"Kece zaki dinga kula da abincinsa, wannan kuma ta kula da sharan falo da goge-goge, sai ke !".

Akayi nuni da Aynu, gabanta yafad'i, tana jiran taji mai za'ace.

"Wannan yarinyace shiyasa nazab'eta, ke zaki dinga kula da gyaran d'akin kwanansa, ki kuma tsaftace band'aki ko da yaushe, sai kije ki basu kayan da zasu saka ku jira zuwan Yarima domin yana hanya anje tarbarsa".

Jakadiyya tazube agaban Fulani tana fad'in.

"Angama Fulani".

Muma muka zube tare dayin yanda tayi, muka mik'e da baya da baya muka fice, ashe wai ba'a juya musu baya sai mutum yaje bakin k'ofa, araina nace ikon Allah wani abun sai gidan sarauta.

Da murnata muka isa inda mukabar su Babah Tasallah nasanar musu an d'aukeni, suma sunyi farin ciki sosai, Babah Tasallah tayiwa Jakadiyya sallama ta tafi gida, mu kuma akayi wani d'aki damu.

Muna shiga nan naga abin mamaki, d'akine ciki da falo shak'are da kaya kala biyu pink da blue sai kace a shago, nan akace mu d'auki blue set biyu  tare da abin wuya murjani da abin hannunsa da 'yan kunne.

Jakadiyya tabarmu cikin d'akin muka sanya kayan, kayan kuwa da Jakadiyya ta nunawa kowa yad'auka dai-dai jikinmu kamar angwada.

Muka fito d'as damu kowa duk inda muka wuce sai kallonmu ake, ban saniba kyau mukayi ake kallonmu ko akasin haka?.

Mai makon mu koma cikin gidan sai naga kowa yana fita waje anjeru tun daga bakin k'ofar shiga gidan har zuwa soron fada, ashe pink d'in unifoam na b'angaren Fulani Sokoto ne, b'angaren Fulani Bingel blue, sai naga maza sunyi nasu layin mata ma haka, Allah ya taimake ni na tsaya kusa da Zainabu, mintuna kad'an da tsayuwarmu aka buga wata uwar bindiga data sanya 'ya'yan hanjina kad'awa, na dank'e hannun Zainabu k'am, ita kuwa tana tamin dariya tana fad'in.

"Sarkin tsoron tsiya".

K'asa-k'asa take maganar da dariya.

Ana gama buga bindigar kuma sai ga jiniyar kwanon motoci tana tana kawo kai.
[07/07, 16:15] Nana Sales Aliyu Fbk Mai Quratu Group: *YARIMA FUDHAL*

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

FIDDAUSI S.A (QURRATUL-AYN)©.

04

•••

Sarki ne da muk'arrabansa suka fara sau kowa  fadawa suka ke wayesu suna yi musu kirari.

Babban abinda yabani Mamaki ya kuma d'auremin kai,  shine sauran fadawan da suke tsaye

bisa layi sai naga kowan ne  mutum ya kwanta bisa cikinsa, Sarkin yataka yabi takan bayansu, har sai da yashiga cikin fada, suka mik'e suka kewayeshi yazauna bisa karagarsa, sanna suka dawo suka tsaya jiran fitowar yarima.

Ya ziro k'afarsa guda d'aya sai da yad'au mintuna sama da biyar kafin ya sake ziro d'aya k'afar cike da izza da k'asaita yafito yanda mahaifinsa yayi shima haka yayi takan bayan bayin fada yabi.

Sai da yashiga soron fada shima sannan sauran 'yan uwansa mata masu aure da su Jalil da Jalila suka fito suma suka nufi fada, amma su bata kan mutane suka bi ba.

Ni kuwa abin ya tsaya min arai sosai, haka muka juya muka nufi cikin fadar zuciyata cike da wasi-wasi da ko kwanton al'amura na wannan masarauta, na fahimci wani abu guda d'aya ga masarautar tun yanzu, wato dai basu d'auki wani talaka abakin komai ba.

Sai da yarima yayi gaisuwa ga mahaifinsa Sarki Ubaiyd ya rungume d'an nasa cike da so da k'auna, kafin yamik'e yashige cikin gidan mu kuma mu da wasu mazan fada muka take masa baya.

Kai tsaye wajen Mai Baban d'aki muka nufa wato mahaifiyyar Sarkin kuma Kaka a wajensu Yarima, nan muka zube tsakar d'akin tana zaune abinta tasha irin shigarnan ta mutan da wadda suke kira da suna b'anti-b'anti, asa riga a d'aura zani har saman k'irji sannan a kawo wani zanin ad'aura k'asan wanan zanin, abun hannu da na wuyanta duka azurfa ce, mace mai fara'a, anan sun shafe kusan awa guda suna gaisawa cike da barkonci, kafin su fito su nufi b'angaren Fulani Sokoto.

Fuskarta wasai ta karb'esu, har da rungume Yarima wai sabida murna, muma kanmu dake sabbin zuwa ne mund'auka da gaske tana farin ciki da dawowarsa sab'anin yanda sauran mutan gidan suka sani.

Muka fito muka nufi b'angaren Fulani Bingel wato mahaifiyarsu Yarima Fudhal.

Muna shiga muka zube muka sake d'iban gaisuwa, ni kuwa da man nagaji da tsayuwa ina zama sai naji wata rahama ta ziyarce ni, musamman da naga sunyi kaman basu san muna wajen ba, araina nace.

"Ma huta ma wannan azaba har ina ?, da man haka aiki yake a gidan saraunata?".

Sun shafe kusan a wanni biyu suna gaisawa, suna hira cike da so da k'aunar tare da murnar dawowarsa lafiya, amma shi abin mamaki wayarsa ce a hanunsa yana danna-dannesa.

Sai idan sun tambayeshi abu ya basu amsa da ehh ko a'a, amsar bata wuce haka abin ya bani

mamaki sosai, na lura su basa damuwa darashin ko inkula d'insa, ko haka halinsa yake? Oho.

Mik'ewa yayi alamun yana buk'atar yaje ya huta sukayi sallama, mu kuma muka dafo masa baya muka fito.

Yana shiga part d'insa yayi kwanciyarsa bisa lallausan carpet d'in dake shinfid'e tsakar d'akin ya ta da kansa da kusun, Jakadiyya ta zube a gabansa tana fad'in.

"Fulani taba da umarnin canja maka bayi, gasu nan guda uku".

Ta nuna ta farko.

"Wannan sunanta Naja'atu, wannan kuma Saima".

Sannan ta nuna ni.

"Ita kuma wannan Aynu, sune zasu dunga kula da nan wajenka yanzu".

Idanmu da muke tsaye munyi magana to shima yayi magana, ko d'ago kai bai yiba bare ma yasan suwaye ke zaune awajen, kawai danna-dannenta yake abinsa a wayarsa mai kama da littafi danni banko tab'a ganin irin taba sai yau a hannun yarima.

Jakadiyya bata damu da amsawarsa ba ko rashin ta, ta dubemu tana fad'in.

"Ku biyoni muje".

Muka fice da sauri muka bi bayanta, kicin muka nufa kai tsaye aka mik'o mana tire guda uku manya ko wacce a cikinmu ta d'auki d'aya, Naja tad'auki mai kuloli manya, Saima ta d'auki mai k'ananun kuloli da flat -flat da kofuna akai, ni kuma aka bani mai kayan mar-mari aciki (Fruit).

Muka d'auka muka kai d'akin Yarima yana nan inda muka barshi, muka ajiye a gefensa Naja tad'auki flat ta zuba masa wani had'ad'dan farfeson kayan ciki, sannan ta zuba soyayyar hanta a cikin wani flat da ban, ta sake d'auko flat ta zuba masa da faf-fan naman kai, sannan ta koma gefe ta zauna.

Ita Kuma Saima a she duk kulolin data d'auko dambun nama ne aciki kala-kala ta zuba masa itama ta koma gefe.

Ni kuwa nayi diri-diri na rasa ya zanyi masa da kayan fruit d'in dana d'auko, na dubi su Naja naga ko kallon inda nake basuyi ba, na d'ago ka na dubi Yarima, da niyyar tambayarsa gabana yayi wani mummunar fad'uwa, sai a lokacin naga irin tsan-tsar kyawun da Allah ya zuba masa, domin duk shige da ficen da muke kai na ak'asa yake ban yarda ko kad'an na kalleshi ba.

Farine amma ba can ba mai matsakaicin tsayi ne, sumarsa bak'ace har zuwa sajensa da gashin baki, yana da manyan idanuwa mai cikar gashin girane daka ganshi zaka san ma'abocin son k'amshi da tsafta ne kuma masoyin son ado ne, zan iya cewa yafi kama da Fulani Bingel domin kamanninsa da ita sunfi fitowa fili mutum ne mai haiba da kwarjini sosai.

Da sauri na mai da kaina k'asa nafasa tambayar tasa, nima na koma gefe kamar yanda naga su Naja sunyi.

Mun shafe wajen mintuna talatin a zaune har zaman yafara gundura ta, sannan naga yamik'e ya zauna, yajawo flat d'in farfeson kayan ciki, Naja tamik'e da sauri ta d'auki Spoon ta mik'a masa yasaka cokalin a hankali ya d'ebi kad'an yakai bakinsa, ya hau taunawa kamar mai cin magani, ya ture gefe haka yayi ta bin farfesun ko wanne flat cokali d'aya ya keyi ya ture, kafin ya koma kan dambun daman shinema naga yad'anyi cokali uku zuwa hud'u, ya ture su gefe ya k'urawa kayan marmari ido na wani lokaci can yaja tsaki, sai jin kakausar muryarsa mukai ta daki kunnuwanmu .

"Wace takawo kayan fruit?, Je ku kiramin Jakadiyya".

Yayi maganar kamar mai koyan magana, kuma umarni da tambaya duk a lokaci guda, hanjin cikina naji yak'ulle cike da tsoro na k'arasa inda yake na durk'usar.

Mai makon yasake magana sai gani nayi yamik'e tsaye, ban zata ba sai ji nayi ya jefe ni da tire d'in kayan marmarin duk sukayi kaca-kaca afalon Allah yasoni babu wanda ya tab'a jikina, amma duk da haka na takure waje d'aya jikina nab'ari.

Jakadiyya ta shigo da saurinta ta durk'usa tana nema min afuwa, nima ganin yanda tayi yasa nima na durk'usa kanmu a k'asa muka fara neman yafiya.

Bai ce komai ba ya shige cikin d'akinsa kawai ya barmu nan zaune.

Cike da tsoro namik'e nahau tsince kayan marmarin, Jakadiyya tace insameta b'angaren Shamaki, suka fice ita dasu Saima suka barni, nan da nan na share wajen na gyare tsaf, sannan natafi filin shamaki.

Nan na iske sauran ma aikatan gidan wasu na aiki wasu na hirarsu ciki har da Jakadiyya, naje inda take na durk'usa ta dubeni kafin ta fara magana.

"Mai kika yiwa Yarima?".

Nan na bud'e baki na bata bayanin dukkan abin da yafaru, shiru tayi nad'an wani lokaci kafin ta cigaba da fad'in.

"Idan aka kai kayan marmari yayyan kawa ake a ajiye a gefen su, wani lokacin kuma a hannunki zaki rik'e kina yankowa kina mik'a masa yana ci, idan abinci ne zubawa zaki ki ajiye masa ki zauna gefe har saiya gama ci wannan aikin su Naja ne, sannan dole ki dinga zuwa da wuri kamar k'arfe bakwai na safe ki gyare ko ina na d'akinsa ki share, ki wanke toilet tsaf ki saka turare, idan ya shiga wanka kafin ya fito ki gyare gado da d'akin ki kunna turaren wuta, amma ke aikin ki uku ne wanke toilet d'innan da share cikin d'akin, sannan ki kai masa dukkan abin da yake da buk'ata ina fatan kin fahimce ni".

Kai kawai na gyad'a mata domin nakasa magana, ta mik'omin wata leda viva tana fad'in.

"Ingo naki abinci kije gida, gobe kizo da wuri".

"To nagode".

Nafad'a ina mai mik'ewa na baro shamaki na nufi d'akin da muka canja kaya na d'auko kayan dana cire tare da set gudan na unifoam d'inmu.

Zan fito daga gidan kenan muka gamu da Zainab zata tafi gida ita ma da murnarta ta tarye ni muka fito tana fad'in.

"Ashe baki tafi ba?, naga farkon zuwa ana tafiya da wuri?".

"Uhmm ke dai bari ! ai Allah ne ya tarfawa garina nono dan da tuni ankore ni".

"Subhnallah ! garin yaya?".

Zainab ta fad'a tana mai zaro ido waje.

Nan dai na bata labarin abin da ya faru, ta d'anyi shiru kafin tace.

"Sai kiyi hankali sosai da taka tsan-tsan, mancewa nayi wallahi inyi maki bayanin ayyukan gidan, amma yan zuma bari infad'a miki tun da Allah yarufa mana asiri ba'a kore kiba".

Muna tafe tana yimin bayani har muka iso dai-dai layin mu mukayi sallama na shige gida ita kuma ta wuce zuwa gidan su.

Ina shiga Ummata ta tarbe ni cike da murna nan na zauna inata zuba mata labarin gidan sarki, ita kuma ta nata gargad'ina inkula sosai inyi abinda ya kaini ka wai ban da sha shanci, har dai da taji batun b'angaren Yarima zan dinga yin aiki, taji kuma irin tsarin aikin nawa, nan dai tayi tamin nasiha ban sanar mata abin da ya faru ba ko kad'an nayi shiru da bakina a ganina ba abin da zan sanar mata bane.

Na dauko kwanuka na juye abincin dake cikin ledar sai naga dukkan abincin da muka kaiwa Yarima ne, nan muka baje muka kwashi gara cike da farin ciki har na mance rabon da tsokar nama ta shiga baki na, Baba na dawowa na kai masa nashi abinci yakarb'a yaci yana ta samin albarka.
[07/07, 16:16] Nana Sales Aliyu Fbk Mai Quratu Group: *YARIMA FUDHAL*

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

FIRDAUSI S.A (QURRATUL-AYN)©

05

*WASHE GARI*

Washe gari ma tun da na tashi da asuba ban koma ba, nan da nan nayi dukkan abin da na sabayi kullum sannan na d'umama mana ragowan abincin da nazo da shi jiya, naci na barwa su Ummata sauran.

6:30am

K'arfe shida da rabi agidansu Zainabu tamin, ko da nazo ta gama shiryawa itama tana jira na muka yiwa Babah Tasallah sallama muka tafi.

Muna isa gidan da Jakadiyya muka ci karo tana ta zirga-zirga, muka gaisheta ta amsa tana k'ara gargad'ina akan inkiyaye sosai nace.

"To insha Allah".

Muka wuce Zainabu tayi b'angaren Fulani Bingel ni kuma nayi b'an garensu Yarima da yake b'angaren Yarima Fudhal dana Jalil a had'e suke daga ciki ne aka rabasu amma k'ofar falon ko wanne d'aki tana kallon d'ayar.

Da sallamata na shiga falon babu kowa ciki sai k'arar fanka da Tv kawai ke tashi.

Na nemi guri na zauna ina kallon k'ofar cikin d'akin nasa zuciyata na bugu, innayi kamar in tashi in shiga sai inji na kasa, ahaka na shafe kusan mintuna talatin a zaune, da k'yar dai nayi k'arfin hali na mik'e na sanya kai cikin d'akin muryata k'asa-k'asa nayi sallama.

Wani sanyi da k'amshi ya doki hancina, na d'aga kai ina kallon d'akin naga d'akin nasa kamar ba a nigeria ba, kayan cikin d'akin nidai tun da nake ban tab'a ganin irin suba, ga wata uwar katifa gado guda yana kwance abinsa abin mamaaki sai naga idonsa biyu yana dai sana'ar tasa danna waya.

Na k'arasa na zube na gaishe da shi bai amsa min ba kamar yanda bai ko kalli inda nake ba, na mik'e da sauri na shege toilet na fara wanke shi domin ina tsoron insake yin wani laifin.

Na wanke tas na sanya turarukan toilet sannan nafito domim insanar dashi cewa na gama, bai kalle niba illa zubo dogwayen k'afa fuwansa da yayi bisa lallausan carpet d'in dake shimfid'e tsakar d'akin, daga shi sai boxer abinsa, ya sanya takalmin da nagani gefan katifar yashige toilet.

Abin ya bani mamaki sosai ta kalmi a kusa da katifa, nan dai na mik'e a gaggauce na gyara katifar tasa na share ko ina na goge, akan mudubin sama nasha mamaki sai kace wani mace, kayan shafe-shafe kala-kala duk ciki babu wanda na tab'ani haka nagama k'are masu kallo danni ba wani iya karatun kirki nayi ba bare in karanta.

Naso yin karatun boko arayuwata amma Allah bai yarjemin ba, iya kacina primari 5 na daina zuwa sabida halin rayuwa na talauci daya sanyamu agaba, islamiyya ce dai nake zuwa har yanzu sabida ita sun d'aukemin biyan ko wanne kud'i dan sun san halin da muke ciki suna tausayawa rayuwata ainun, gashi itama ina ina neman dai na zuwa sabida wannan aikin.

"Tab ! bazai yuyuba yau kam dole inje islamiyya, domin bazanyi biyu babu ba".

Na fad'a a fili ciki-ciki ina mai cigaba da gyara d'akin.

Ashe ma har yafito bansani ba ina can ina zancen zuci, sai da naji ana tab'a kwalaben kan mudubi sannan na lura da yafito, ban ko kalli inda yake ba na fice falo abina.

Saima na gani a falon tana shirya masa abin kari, muna had'a ido da ita ta jefeni da wata uwar harara, ni kuwa nad'auke kai na kamar ban san tana yiba, nayi zamana abina ina jiran umarnin Yarima.

Sai dai kuma naga ba'a gyara falon ba amma tajere masa abin kari.

"Meye zai dame ni ma tunda ba aikina bane?".

Nayi maganar cikin rai na, sai da muka shafe awa guda zaune sannan mukaji takun fitowar Yarima, muka mik'e tsaye kanmu a k'asa  ya tako cikin takun k'asaitar nasa k'amshinsa mai sanyi ya cika falon, ya nemi guri ya zauna ba tare daya ko dubi inda muke ba bare abincin da aka jere masa.

"Ohh ikon Allah ! ni dai tun da nake arayuwata ban tab'a ganin miskilin mutum irin Yarima ba, ko d'an yana tak'ama da mulki da kud'i ne oho".

A cikin raina nake ta zancen ni kad'ai, Saima naga ta matsa tahau jere masa abin kari kala-kala ni wani girkinma ko ganin irinsa ban tab'ayiba bare ince na ci.

Da katar da ita yayi da hannu ba tare da yayi magana ba.

Ina ganin haka 'ya'yan hanjina suka kad'a tsoro ya kamani ko wani laifin muka sakeyi.

"Kira Jakadiyya".

Abin da kawai ya furta kenan ya cigaba da aikin sa ko ince sana'ar tasa.

Da rawar jiki na fice na tafi neman Jakadiyya, wata mata Ladidi na tambaya tasanar min tana b'an garen Fulani Sokoto ai kuwa can d'in na nufa.

Ina shiga na zube na kwashi gaisuwa wajen Fulani Sokoto, wani kallo ta watsomin kafin tace da Jadiyya.

"Wannan kuma fa?".

"D'aya ce daga cikin ma aikatan Yarima".

"Cikinsu har da yarinya irin wannan ?".

"Ehh Yarinyarce suna fama da gararin talauci ne, tazo aikine domin su dunga samun abin da zasu ci".

Sai naga Fulani Sokoto tayi murmushin da bansan ko na mene neba, araina ina tunanin meye yasa zatayi wannan maganar akaina?.

"Meke tafe dake?".

Maganar Jakadiyya ta katse n i daga tunanin da nake, na bata amsa da fad'in.

"Yarima keson ganinki da gaggawa".

Ta mik'e tana yiwa Fulani Sokoto sallama nima nabiyo bayanta, a hanyarmu ta zuwa b'angarensu Yarima ta dube ni tana fad'in.

"Ki iya takunki da kowa a gidan nan, ki kame kanki kada ki soma shiga abin da ba ruwanki, sannan kiyi taka tsan-tsan da al'amuran b'angaren Fulani Sokoto".

Ni dai har tagama bayaninta ban fahimci komai ba, sabida tunani na yagama bani yau korata z'ayi kawai tuni na fara matsar kwalla.

Muna shiga ta zube a gabansa nima haka, Saima kuwa dama tana inda nabarta illa gani da nayi ta zubawa Yarima ido kamar zata cinyeshi

Bai ko kalli inda mukeba ya fara magana.

"Gaskiya wa 'yannan basu san aikin su ba, in da dama acanja wasu".

Jakadiyya ta russuna tana fad'in.

"Sunyi laifi ne ranka dad'e?".

Ya tsuna fuska yayi kafin ya bud'e baki a hankali yana magana.

"Ya za'a ajiyemin breakfast ba tare da anshare ba?".

"Ayi afuwa Magajin gobe, Kai kace a cire mutum d'aya, to laifi nawane aga farceni ban sanarwa Aynu gyaren falo ya dawo gare ta ba na mance ne wallahi".

Kai kawai ya gyad'a alamun ya gamsu, yamik'e ya fice daga d'akin ya barmu nan zaune, Jakadiyya ta dubeni.

"Aikin kine Aynu share falon nan ki goge sosai kisa turare domin Yarima ma'abocin son k'amshi ne, ki kiyaye da kyau".

"To ba damuwa".

Haka kawai nace, domin ko bata gayamin ba na fahimci irin so da k'aunar da yakewa dangin turare, ta mik'e ta fice daga d'akin ta barmu ni da Saima, ita ma Saiman bayan ta gama kwashe kwanukan abincin tafice abinta tana fad'in.

"Idan kin gama zaki iya zuwa ki juye abincin nan nakine, domin kece kalar yunwa".

Ta fice abinta nabi bayanta da kallo araina ina mai-maita kalmar.

"Kalar yunw? Kalar yunw?, Ehh gaskiya ni kalar yunwace kowa ya ganni zai san haka, to amma mai yasa zatacemin haka?, na d'auka duk wanda yazo aiki yazone domin nemana abin da zai ci ne ko?, ko kuma akwai masu zuwa aiki ne domin ra'ayi kawai?".

Ganin bani da amsa dukkan tambayoyi na, kuma babu mai amsamin yasa na hak'ura nahau yin aikin dake gabana, duk k'ok'arina yau in koma gida da wuri domin inje islamiyya.

"Mama kina nufin Yarima Fudhal zaki nema wa auren Gimbiya Safiyya?".

Cewar Jalil kenan dake zaune gefan mahaifiyyar tasa, murmushi tayi kafin ta bashi amsa.

"Ehh mana haka nake ganin shine mafita, bayan auren zan sanar maka shiri na na gaba".

"Amma fa ni nake son tafa kin sani Mama!".

"Kai fa sha-shane wallahi mutumin da ake nema masa hanyar sarauta mai zai yi da wata soyayya?".

"Nasani Mama amma gaskiya banjin zan iya hak'uri da sonta".

Murmushi tayi akaro na biyu kafin ta dube shi da takaici.

"Na zaci ko sanin kana sonta Gimbiya batayi ba?".

"Ehh amma aike nake nufi ki gayawa Mai Martaba anema min aurenta".

Fulani Sokoto dariya tayi mai sauti awan nan lokacin tana mai yiwa d'an nata kallon soko baka san abin da kake yi ba, amma a fili kuma cewa tayi.

"Amma kai dai baka da tunani ko kad'an Jalil taya Mai Martaba zaiyi maka aure ga yayan ka bai ko kawo maganar auren ba !, ka dai sake tunani amma ni maganata na gama".

Jalil yayi shiru yana duban Mahaifiyar tasa batare daya sake furta ko mai ba itama haka.

Yarima Jalil suna matuk'ar kama da Yarima Fudhal ban-ban cinsu kawai shekaru da kuma k'asumbar fuska, Yarima Jalil shekararsa ashirin da bakwai kuma shi baya tara k'asumba a fuskarsa illa siririn sajen da yayuwa fuskarsa k'awanya, yayin da Yarima Fudhal ke da shekaru talatin aduniya ma'abocin tara suma ne ta kai da kuma fuska da suke shan gyara ko yaushe wanda hakan bak'aramin kyau yake k'ara masa ba.

Mik'ewa yayi zai fice bata dubeshi ba take fad'in.

"Ka kiramin Ladidi".

"To".

Kawai yace ya fice daga d'akin, a hanyarsa ta zuwa b'angaren sane ya gamu da Ladidin ya bata umarnin taje mahaifiyarsa na kiranta, shi kuma ya shige b'angarensu.

Fitowa ta kenan daga falon Yarima na gama gyarawa zan tafi mukayi karo da shi yana shirin shiga d'akinsa, durk'usawa nayi na gaishe shi bai amsaba sai k'uramin ido da yayi yana bina da kallo, na mik'e na wuce abina domin tunanina shima miskilin ne irin Yarima Fudhal.

Har sai da nak'ule ya daina ganina sannan ya shige d'akin nasa yana sosa k'ewa fuskarsa cike da murmushi kona menene ? oho.

Yau ban jira Zainab ba sabida saurin da nake, naje na juye abincin da Yarima ya bari acikin Viva nayiwa Jakadiyya sallama na tafi gida.
[09/07, 00:23] Nana Sales Aliyu Fbk Mai Quratu Group: *YARIMA FUDHAL*

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

FIRDAUSI S.A (QURRATUL-AYN)©

06

Yauma kamar kullum haka na tadda shi kwance bisa katifarsa mai kama da gado ya lullub'e jikinsa da bargo mai taushi, hannunsa dake rik'e da waya kawai sune a waje yana danne-dannansa.

Naje na gaishe shi duk da baya amsawa amma hakan bai sa na dai na gaidashi ba sabida gudun yin laifi, na mik'e na wanke toilet na fito na sanar masa na gama.

Ya ziro k'afafuwansa ya saka takalmimsa yashige toilet batare daya kalli inda nake ba, ni kuwa na mik'e na kad'e ko ina na share na goge , na kalli agogo naga kusan awa guda kenan, araina nace.

"Wannan wane irin wanka ne?, mutum yayi awa guda a toilet kamar mai canja fata?".

A fili kuwa na furta.

"Ko da yake komai na masu sarauta da ban ne".

Jin motsin fitowarsa da nayi ne yasa na d'ebi tsin tsiya da abin mooping nayi falo, na cigaba da gyaran falon, na kusa gamawa sannan sai ga Saima ta shigo hannunta rik'e da tire bata ko kalli inda nake ba ta wuce inda Yarima ke cin abinci ta fara jere masa, ni kuwa na gaggauta tsaftace falon sabida kada ya fito yaga ban gamaba.

Allah kuwa ya taimakeni bai fito ba sai da na gama na d'auke komai sannan ya fito, shigar coat yayi fara har zuwa wando da agogon hannunsa da takalmi duk farare ne na fahimci dai baya son manyan kaya domin tun dawowarsa banga ya saka kayan nan k'asar ba.

Yaje ya zauna yana wani shan k'amshi, Saima ta jere masa dukkan nin abin da tasan zai buk'ata ta koma gefe ta zauna tana kallonsa, ni dai kaina ak'asa yake addu'a nake Allah ya rabamu dashi lafiya yau.

Cokali d'aya yayi na ruwan tea wayarsa dake hannunta tahau ringing ya d'aga yana mai sata

free, domin duk muna jin abin da ake cewa a waya r sai dai bana fahimtar abin da suke fad'i domin yaren turanci naji sunayi ni kuwa kun dai san banko k'arasa primari ba bare ince zan ji turanci, Saima ce dai naga tana ta murmushi kamar tana fahimtar wani abu da yake fad'a a wayar.

Yana kashe wayar yamik'e ya fice, Saima ta tattara kayan da sauri ta fice da su tabarni zaune a falon nayi ta gumi ina wani tunani na da ban, sai kawai ji nayi andafa ni ta baya firgigit na juya domin ganin waye?, domin tunanina ya bani Zainab ce.

Ina juyawa sai naga sab'anin tunani na a she Yarima Jalil ne, na durk'usa da sauri na gaishe shi duk da fad'uwar gaban da nake fuskanta awannan lokaci.

Amsawa yayi yana mai cigaba da kallo na, ni kuwa kaina na k'asa cike da tsoro na furta .

"Ko kana buk'atar wani abu ne?".

Kai kawai ya girgiza alamun a'a yana mai neman guri ya zauna yana fad'in.

"Ku nawa kuke yiwa Yarima aiki?".

"Mu biyu".

Na bashi amsa a gag-gauce, yad'an tab'e baki a hankali kafin yace.

"Kina jin dad'in aiki anan kuwa?".

"Ehh".

Na kuma bashi amsa.

Shiru ya gauraye d'akin na wani lokaci, nidai kaina yana k'asa Allah Allah nake insamu in fice daga d'akin, dan haka kawai nidai hankalina bai kwanta da al'amarin Yarima Jalil ba, ina cikin tunanin yanda zansamu in fice daga d'akin sai kawo jin hucin numfashinsa nayi a fuskata naja baya da sauri, bina yayi da kallo kafin yayi murmushi kawai ya fice daga d'akin, ajiyar zuciya na saki kafin in mik'e da sauri nima na fice daga d'akin har ina tun-tub'e.

A hanyata ta zuwa inda sauran ma'aikatan gidan ke zama insungama aiki naci karo da Zainab taa ganni duk a wani tsorace, jana tayi wani b'angare na gidan da ban tab'a sanin da shiba domin Zainab tasan ko ina a cikin gidan kuma kowa ya san ta.

Muka zauna ta rik'o hannunta tana tambayata.

"Lafiya Aynu?".

Nayi shiru nad'an lokaci ina kallon wani gefe na wajen, kafin na dawo da kallona kanta na fara bata labarin abin da yafaru.

Zainab ta zaro ido waje tana fad'in.

"Innalillahi wa'inna ilaihi raji'un, sai kinyi taka tsan-tsan da Yarima Jalil sosai wallahi".

"Kamar yaya?".

"Nasan baki san waye Yarima Jalil bako Aynu?".

Tad'an rage muryarta k'asa-k'asa.

"To Yarima Jalil ya wuce dukkan tunaninki, ya ksance mashayin giya kuma manemin mata a cikin gidan nan duk wacce aka kawo aiki indai ta burgeshi to wallahi duk hanyar da zai bi sai yabi domin ta zama yarinyarsa, ma aikata uku aka zubarwa cikinsa, kuma aka kulle bakinsu da kud'i kada su fad'a babu wanda yasan haka sai mahaifiyarsa sai kuma Jakadiyya, domin ita ce ma take sanarwa Babah Tasallah lokacin dana fara aiki a gidan nan, ko Mai Martaba kansa bai san muna nan halin Yarima Jalil ba".

Gumi ne ya ketomin ta gefan fuskata jin wannan bayani na Zainab nayi maza na goge ina fad'in.

"Ina hakan ma ba zata tab'a faruwa ba, babu dole sai in hak'ura da aikin".

Dariya Zainab tayi kafin tace.

"Kina hauka kenan?, ai barin aikin ki bai ta soba domin ko kinbar aikin sai ya binciko inda kike kuma sai ya biki".

"Wayyo Allah na to yanzu ya zanyi?".

Nace da Zainab cike da tsoro, domin kunsan halina akwai tsoro kamar farar kura.

Zainab tayi shiru kafin tace.

"Ki kwantar da hankalinki ko Ummanki kada ki fad'awa, tun da Allah yasa ba aikin dare kike ba, ko kad'an kada ki bashi fuska iya kaci gaisuwa bazai tab'a saki wani aiki ba tunda yasan ba b'angarensu ki kewa aiki ba kawai dai ki iya takun ki a gidan nan".

Shiru nayi ina duban Zainab kafin ince.

"Au dama akwai masu aikin dare ne?".

"Ehh akwai koni da farkon zuwana aikin dare na farayi sai da Jakadiyya tayi magana na dawo safe".

Aynu tayi ajiyar zuciya domin kalaman Zainab ya kwantar mata da hankali ya kuma bata kwarin gwiwa, har dai da taji batun bazai tab'a umartatta da wani aiki ba tunda ba'a b'angarensu take aiki ba taji dad'i sosai.

Nan sukayi ta hirarsu har Zainabu take sanarwa Aynu taji Yarima Fudhal yana fad'in zai fita shida abokansa sun shirya masa party na murnar kammala karatunsa lafiya.

Aynu tace "kaji illar wasu masu kud'inba, idan har murnar za'ayi da gaske mai zai hana ayi saukar al'qur'ani da walima".

"Kema dai kya fad'a kinsan bakowa yake son abin da za'a fad'i abin da Allah da Manzonsa suka ce ba, al'amuran yahudawa yafi rinjaye a zukatan yawancin mutanen mu nayanzu, duk da cewa ba duka aka taru aka zama d'aya ba".

"Haka ne, Allah dai yasa mu dace".

"Amin ya Allah".

Suka amsa baki d'ayansu da haka har lokacin ta shinsu yayi kowacce taje ta d'auki abincinta suka tafi gida.

*** ***

Filin wajen cike yake mak'il da jama'a maza da mata kowanne yana ji da kansa, domin kowa ka kalla a wajen za kasan kud'i ya zauna sabida daga d'an Alhaji da Hajiya sai d'an menister wane 'yayan 'yan kasuwanni da 'yan siyasa sune suka cika wajen bakajin komai sai tashin kid'an turawa kala-kala da wannan ya katse sa kaji wannan ya d'ora, dare ne amma tamkar rana haka wajen yake sabida hasken daya haske wajen wanda shine ya basu kwarin gwiwar yin harkokinsu hankalinsu kwance.

Filin wajen kansa abin mamaki ne banda irin cikar da yayi, jerin motoci goma ne sukai layi a harabar wajen duka bak'ak'e ta tsakiya ce kawai fara, jikin lambar motar kowacce anrubuta Emirs 1 har zuwa 10.

Baki d'aya gurin yarud'e da ihun kiran sunan YARIMA FUDHAL.

Cikin takun k'asaita yafito   kamar bazai iya  taka k'asa ba yana wani shan k'amshi yayi shiga irin tasu ta sarauta kowa ya ganshi yasan Yarima ne wanda akeji da shi a gida da kuma waje, sauran abokansa suka take masa baya.

Waje na musamman aka ware masa shi da abokansa, hankalin 'yan matan gurin nan kaf yayi kansa kowacce burinta tasamu shiga wajensa.

Bayan kowa ya natsa kuma aka buk'aci Yarima Fudhal yayanka cake, yamik'e fuskarsa cike da murmushi ya d'auki wuk'ar zai yanka, aka fara irga.

"One....two.....thr..".

K'arar motar dake shirin yin parking a wajence ta katse kowa, dukkan hankulan jama'ar gurin ya koma kan motar.

Domin mota ce da duk wajen babu wand ya halarci gurin da ita mota ce k'irar Perrari mota mafi kyau da tsada.

Kowa burinsa a wajen yaga waye ma mallakin wannan motar?.

A hankali ta ziro shantaleliyar k'afarta da tasha dogon takalmi mai tsini yana da igiyoye wanda sune suka taimaka wajen rik'e k'afa fuwanta, shigar dake jikinta kuwa guwn ce pink da tabi dukkan jikinta ta d'ame, daga gaban rigar  har zuwa k'asa yasha adon stone blue dark tayi rolling da mayafi k'arami shima blue.

Wayar dake hannunta ta d'orata bisa cinyarta X ce itama kalar takalminta blue, duk wannan bayanin da akefa bata fito da dukkan jikinta ba bare har mukai da ganin duskarta.

Ta shafe mintuna kusan biyar a haka kafin ta fito zuwa waje, anan ne fa dukkan nin mumfashin mutanen dake wajen ya kusa d'aukewa sabida kyakykyawar halittar da idanuwansu yayi tozali da ita, duk da bak'im glass d'in dake fuskarta daya rufe kusan rabin fuskarta, amma hakan bai hana ganin tsan-tsan kyawun halittar dake tattare da ita ba.

Cike da murmushi ta doso inda Yarima yake  tana wani taku tare da rangaji kamar bishiyar da iska ke kad'awa.

Nidai  tunani na banyi zaton zata iya taku da takalmin dake k'afar taba, amma sai naga tana tafiya kamar wadda tasanya silifas .

Bata tsaya ba sai da taje dai-dai inda Yarima Fudhal yake tsaye rik'e da wuk'ar yanka cake sannan ta tsaya jikinsu har yana gogar juna ta juyo tana k'arewa sauran mutanan wajen kallo kafin ta saka hannu ta cire glass d'in da yayiwa kusan rabin fuskarta k'awajen.

A fili na furta "SAIMA!".
[10/07, 20:09] Nana Sales Aliyu Fbk Mai Quratu Group: *YARIMA FUDHAL*

NWA®

FIRDAUSI S.A(QURRATUL-AYN)

07

A fili na furta "Saima !".

Amma Yarima Fudhal kuwa tsaya wa yayi yana dubanta cike da mamaki tare da tunanin inda ya tab'a ganin fuskarta.

A hankali ta dawo da kallonta kan fuskar Yarima da ya tsare ta da shanyayyun idanuwansa yana nazari a kanta sosai, tunaninsa ya tsaya adai-dai lokacin daya tuna yatab'a ganin mai kama da ita awani guri.

Idan zai iya tunawa lokacin daya ba da umarinin a kira wo masa Jakadiyya ranar da ba'ashare falo ba, a lokacin bai zaci da mutum zaune ba yad'auka dukansu suka fita yana ta danne-dannan wayarsa ya d'ago kai bai zata ba suka had'a ido tayi saurin sauke kanta k'asa shine ganin da zaice yayiwa mai kama da ita.

"Wacece ke!".

Bai san sanda ya samu kansa da jefa mata tambayar ba, bata bashi amsaba illa rik'o hannunsa dake rik'e da wuk'ar yan kan cake d'in da tayi ta fara irga, sai kawai gani yayi ta yanko cake ta nufi bakinsa da shi kau da kansa yayi gefe yana mai komawa inda yake a zaune ya zauna.

A dai-dai lokacin da aka k'ara sakin kid'a ana ciye-ciye da shaye-shaye, Saima ta koma kusa da shi ta zauna tana dubansa tare da zuk'ar lemon da ke rik'e hannunta, ta d'an basar kamar yanda taga yayi mata amma ta kasa jure shirun nasa ta gyara zama tana fad'in.

"Suna na Saima 'yar gidan Alhaji Buba 'yarsa tilo guda d'aya da akeji da ita tamkar kwai, nice first kuma nice last a gidanmu, bawai nazo wajen nan dan wani abu ba, nazone intayaka murnar dawowarka k'asarka lafiya sanna in sanar maka irin son da nake maka, sauran bayani zan baka numberta sai muyi magana a waya".

Duk zubar datake ko kallon inda take bai yi ba, shidai burinsa kawai ya fita daga kokwanton da zuciyarsa takeyi masa, aransa yana fad'in.

"To idan wannan 'yar gidan Alhaji Buban dana sani ce waccan kuma da take min aiki wacece?".

Babu amsa domin maganar aransa yake yinta bai ko yi k'ok'arin tambayarta ba, sai ji yayi ta zare wayarsa dake rik'e a hannunsa binta kawai yayi da kallo kafin ya mai da kansa kan al'ummar wajen, sai da ta sanya numberta a wayarsa ta d'auki tasa a tata wayar sannan ta ajiye masa wayar a gabansa ta mik'e ta shiga filin rawa.

'Yam matan dake wajen baki d'aya sun raina kansu, da had'uwa da kud'i irin na Saima, samari kuwa tuni sukayi ca a kanta kowa yana zuba mata kud'i, domin su sami shiga a wajen ta duk da sun saddak'ar ita d'in ta Yarima Fudhal ce.

Shidai Yarima bai ko taka inda ake rawar ba, har suka gama aka hau d'auke d'auken hotuna kuma.

11:30pm

Sai sha d'aya na dare aka tashi kowa ya nufi hanyar gidansu, Yarima ya dawo a gajiye wanka kawai yayi da sallah ya nemi makwancinsa ya kwanta, yana Allah Allah gari ya waye ya warwarewa zuciyarsa wasi-wasin da take ciki.

*** ** ***

7:30am.

Muryar Aynu ita ce tayi sanadiyyar ta shinsa daga dad-da d'an baccin da yake, domin da k'yar dama ya samu yayi sallar asuba ya koma, domin shi mutum ne da baya wasa da sallah ko kad'an, mik'a yayi tare da salati ya mik'e ya nufi toilet ba tare daya kula da gaishe shin da take ba, domin inda sabo yaci ace ta saba da halin Yarima.

Nan d nan sai gashi yafito falo Aynu ta cika da mamakin shirya warsa da wuri haka yau,

lokacin Saima na zaune ta gama jere masa abincin, zama yayi yana mai k'urawa Saima ido, sai dai wani abu daya rud'ar da shi akan Saiman jiya da wadda take masa aiki shine.

Wan nan bak'ace waccen kuwa farace sol kamar a tab'a fatarta jini ya zubo duk da manyan idanuwansu yazo d'aya, sannan kuma ta jiya tana da hip sab'anin wannan siririya.

"Ke ! mik'e tsaye".

Sukaji saukar muryarsa akunnu wansu da sauri suka mik'e duka, sai kuma ya tuna ai ta jiya ta sanya dogon takalmi ne bazai iya tan-tance tsayunsu ba.

"Mene sunanki?".

"Ay....".

Aynu tabud'e baki zatayi magana yakatseta da fad'in.

"Ba ke ba ".

Ba tare daya dubeta ba, domin idonsa na kafe kan Saima kawai.

Tayi shiru abinta tana kallon ikon Allah yau.

"Saima ".

Ta bashi amsa, sai yaji muryar Saiman jiya tafi siririya akan ta wannan, kai ya girgiza yana fad'in

"Sunan ne yazo d'aya tare da kama kenan?".

A fili yayi maganar yayin da Saima da Aynu suka dubi juna, Saima ta jefawa Aynu wata muguwar harara, Aynu kuwa ta mayar mata da murmushi.

Mik'ewa yayi ya fice ba tare daya bi takan abincin nasa bama.

Kai tsaye shashin mahaifiyarsa ya nufa, ya sameta tana bada umarnin wasu abubuwa a gidan neman guri yayi ya zauna yana mai gaishe da mahaifiyyar tasa yayin da ma aikanta suka gaishe da shi, bai amsa ba suka mik'e duk suka fice.

Sai yayi shiru kuma yana jujjuya wayarsa a hannunsa, kallonsa Fulani Bingel ta tsayayi tana karantar yanayinsa.

"Lafiya Magaji?".

A jiyar zuciya yayi kafin ya fara magana.

"Hajiya dama a kwai mutanen da zakiga basu san junaba basu had'a wani relation ba amma kuma kiga suna kama sosai?".

Fulani Bingel tad'anyi dariya tana fad'in.

"Magaji kenan ! to ai ko wanne mutum da kagani akwai copy d'insa bakwai a duniya, wani abune ya faru kake wan nan tambayar?".

"A'a babu komai".

Abin da yace kenan bai sake magana ba, yamik'e ya shiga b'an garen Kakarsa Mai Babban d'aki, anan yayi breakfast d'insa bai bar wajen taba sai k'arfe biyu da aka kira sallar azahar ya fito ya tafi masallaci, kafin ya dawo su Aynu tuni sun gama aikinsu sun nufi gida, ya shige d'akinsa ya kwanta abinsa.

***

BAYAN SATI GUDA !.

Sati guda kenan da had'uwar Saima da Yarima Fudhal kullum tana zuba ido taga kiransa a wayarta, amma girman kai da jiji da kai ya hana ta nemeshi ita, yayin da shi kuma yama mance da al'amuranta domin shi mutum ne da baya son sanya abu aransa domim yan zunnan sai abin ya nemi ya zame masa matsala tunda ya samu Mahaifiyarsa tayi masa bayanin ana samun copy d'in mutum bakwai aduniya shikenan domin dama kokwan tonsa ko ta zo aiki gidanne sabida wani nufi nata amma yanzu zuciyarsa ta bashi waccen Saiman daban wadda ke masa aiki daban.

B'angare guda kuma kwana uku kenan Aynu batazo aiki ba sabida Ummanta dake kwance babu lafiya, sai dai ta fad'awa Zainab ta sanar a gidan sarki kada aga bata zuwa, Jakadiyya tace babu komai taje ta sanarwa Yarima shima cewa yayi ba damuwa sannan ya ciro dubu biyar yace a bata su sai magani Jakadiyy da kanta ta kai musu gida domin macace mai kirki da rik'on gaskiya da amana.

A rana ta biyar ne Aynu taga jikin Mahaifiyar tata yayi sauk'i ta shirya tace zata koma aiki ta yima Ummanta sallama da Babanta ta tafi.

7:30am.

Bakwai da rabi na safe kamar yanda ta saba ta isa gidan, bayan taje ta gaishe da Jakadiyya ta gaida Fulani Bingel kai tsaye kuma b'angarensu Yarima ta nufa.

Tana shiga taga Naja ta fito daga d'akin Yarima Jalil da alamun rashin gaskiya a fuskarta, Aynu tayi kaman bata ganta ba ta wuce d'akin Yarima.

Kamar yanda ta saba batayi tunanin komai ba tasa kai cikin d'akin, yanda ta ganshi ne ya sata zubewa bisa gwiyoyinta ta runtse idonta k'am jikinta na faman b'ari kamar mazari.

Ta mudubi ya ga shigowarta a fili ya furta.

"Ohhh my God !".

Yana mai dafe goshinsa.
[17/07, 16:25] Nana Sales Aliyu Fbk Mai Quratu Group: *YARIMA FUDHAL*

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

FIRDAUSI S.A (QURRATUL-AYN).

SADAUKARWA:- Namesy ta Pheerdauceey Jeebour.

Amma wannan page naki ne SAFIYYA GALADANCHI Allah yabar zumunci.

08

"Ohhh my God !".

Ya fad'a yana mai dafe goshinsa.

Aynu kuwa tuni hawaye ya fara zarya a kan kuncinta harta saddak'ar yau aikinta yak'are a gidan.

"Wanne kuskure tayi da har ta shigo ta taddashi a wannan yanayin?".

Tayi tambayar cikin ranta.

"Sallama !, Ita ce kuskuren da nayi da a ce nayi sallama da ban shigo na same shi a haka ba, da yayi k'ok'arin kintsawa kafin shigo wata, ko ya da katar dani harya suturce jikinsa".

"Wayyo Allah na !".

Ta fad'a a fili kuma da k'arfi wanda har sai da Yarima Fudhal dake k'ok'arin suturce jikinsa ya juyo yana dubanta, wannan shine karo na farko da Yarima ya tab'a duban fuskar Aynu tun zuwanta gidan aiki, gabansa ya buga dammm, yayi saurin d'auke kai yana mai ci gaba da sanya rigarsa tare da tunanin yanda a kaima tazo ta taddashi a haka, aransa ya furta.

"Kuskure na ne !".

MINTUNA TALATIN DA SUKA WUCE

Kasancewar Aynu ta daina zuwa aiki kwana biyu sabida jinyar Ummanta, sai aikin wankin toilet da shara ya koma hannun Saima duka.

Yau ya tashi yajishi a gajiye ga kuma gumi da yaji yanayi duk da sanyin AC da ke d'akin amma hakan bai hana shi jin zafi ba, ha kan ne yasa ya nufi toilet domin watsa ruwa.

Sai dai Yarima nada wata al'ada guda d'aya, kasan cewarsa mai tsafta da kuma kyankyami shiyasa ko kad'an baya iya barin abu jik'ak'k'ema ajikinsa yana fitowa daga toilet yake wurgi da towel d'insa sannan ya nemi wani ya d'aura ko ya bari ya gama shafa mai da koma kafin ya suturce jikinsa, sabida ya san babu mai shigo masa d'aki sai da izininsa hakan ya kuma zame masa jiki sosai, to yauma a hakan ne Aynu ta shigo ta tadda shi.

Yana gama sanya rigar ya sake dawo da dubansa kan Aynu da jikinta ke ta tsuma tana jiran saukar duka ko wani mugun hukunci daga Yarima.

Zama yayi gefan katifarsa yana fad'in.

"Ke !, zo nan".

Aynu ta rarrafa da jan gwiwa ta k'arasa inda ta jiyo muryarsa idonta har lokacin a kulle bata bud'e ba, cike da tsoro ta haufad'in.

"Kayi hak'uri ka gafarce ni dan Allah !, wallahi tallahi banyi zaton zan tadda kai a haka ba Allah, dan Allah kada ka kore ni da wannan aikin muka dogara nasha wuya kafin in same shi amma....!".

Kuka ne yaci k'arfinta ba tare da ta iya k'arasa mganarba ta mak'ale a mak'oshinta.

Yarima kuwa murmushi yayi yana mai k'arewa halittarta kallo yayin da yakeji bugun zuciyarsa na k'aruwa sosai amma yana jin da d'in kallon nata sosai, musamman yanda take sarrafa leb'anta wajen magana, sai zara-zaran gashin idonta da suka jik'e da hawaye duk da bai ga idon nata ba.

"Bud'e idonki babu abin da zanyi miki".

Yayi maganar yana mai kafe idanuwansa bisa nata.

Aynu ta hau bud'e idonta kad'an-kad'an wai dan kada ta kuma ganinsa a yanda ta ganshi d'azu, tana gama bud'ewa sukayi ido biyu da shi, tayi saurin sauke idonta tana mai rissi nawa da fad'in

"Nagode sosai, Allah yak'ara girma".

"Amin".

Da sauri ta d'ago kai ta dubeshi sabida mamakin yau karo na farko tayi magana ya mayar mata, murmushi kawai ta ga yayi mata, ta d'auke kanta tana mai shigewa toilet din domin wankewa.

Mintuna kad'an ta fito ta taddashi a inda tabarshi illa wayarsa dake hannu yana daddan nawa, yanaji ta fito ya d'aga kai yana binta da kallo har ta zo ta durk'usa tana sanar masa ta gama.

Mik'ewa yayi ya fice bai ce da ita komai ba, yana fita Aynu tayi ajiyar zuciya domin ita kanta kallon da yake mata ya fara bata tsoro sosai, ji take aranta kamar hukuncin da zai yi mata yake shiryawa.

Ta gama komai ta fito falo ta taddashi zaune, amma wannan karan ya akiye wayar gefansa yana kallon ball a TV, gefe guda kuma Saima ce zaune Aynu na fitowa ta hau aika mata sak'on harara ita kuwa bama tasan tanayi ba, ta fara k'ok'arin gyara falon duk abin da ta keyi idon Yarima akanta shi kansa bai san dalilin da yasa yau d'aya yanajin dad'in kallon yarinyar sosai, komai takeyi a nutse cikin sanyi kuma hakan na burgeshi sosai.

Sai da ta gama komai yau duk yana zaune, sannan Saima tazo ta jere masa kayan Breakfast d'insa, yana ci yana faman kallom Aynu yayi mamakin irin abincin da yaci yau sosai, ya gama Saima takwashe kwanukan ta fice tabar Aynu nan zaune.

Zaman duk ya gun dureta ga kallon da Yarima Fudhal keta jifanta dashi domin lokaci-lokaci data d'ago kai sai sun had'a ido baki d'aya jinta take yau duk a takure sai take tayin data sanin zuwanta aikin ma yau baki d'aya.

"Mene sunanki?".

Taji tambayarsa ta jefi kunnuwanta, ta d'an gyara zama tana fad'in.

"AYNU".

"Aynu kuma?, ci kakken sunanki nakeson ji".

Ajiyar zuciya tad'anyi kafin ta bashi amsa.

"AYNUL-HAYAT".

Ta fad'a tana mai gyara zamanta da kyau domin ji tayi k'afafuwanta duk sunja jini sunyi wani iri babu dad'i sabida zaman d'urk'ushen da tayi.

"Aynul-hayat !".

Taji ya mai-maita cikin wata irin murya da ta sanya tsigar jikinta tashi, ta d'ago kai akaro na biyu ta dube shi shima ita d'in ya kafe da idanuwa ya jefe ta da murmushi kafin yace.

"Nice Name".

Tayi saurin sauke idonta yayin da bugun zuciyarta ya cigaba da k'aruwa, aranta tana fad'in.

"To me ya zauna yi yau ayanda nasan shi da yana gama cin abinci yake ficewa zuwa wajen Kakarsa ko Babarsu amma yau ya wani zauna ya tsare mutane".

A fili kuwa ita ma murmushin ta d'anyi duk da bai kai zuci ba.

"Beautiful smile".

Taji yak'ara fad'a ita ta d'auka ma waya yake da turawa dan bata fahimci mai yake fad'i ba.

Mik'ewa yayi ya shige bedroom d'insa mintuna kad'an sai gashi ya fito sanye da jeans bak'i da T.sheet blue yayi kyau sosai, yazo yad'an rage tsayinta akanta yana fad'in.

"Aynul-hayat !".

Taji gabanta ya fad'i, ta d'ago kai ba tare data amsa ba, shima bai da muba ya cigaba da fad'in.

"Yaushe kuke tafiya gida?".

"K'arfe biyu ko biyu da rabi".

"Ok".

Abin da yace kenan ya kama hanya ya fice ya barta nan zaune tana tunanin abubuwan da suke faruwa da ita yau.

"AYNU".

Ta sake jin muryarsa ta daki kunnuwanta ta juyo da sauri sai taga ashe Yarima Jalil ne tsaye bakin k'ofa ya nad'e hannuwansa bisa k'irjinsa yana jifanta da wani mugun murmushi.

Gaishe shi tayi ya amsa yana fad'in

"Mai yasa bakyason sakin jiki da ni, da zaran kin ganni sai kin tsora ta?".

"Babu komai".

"Da wani abu mana fad'i gaskiya dai?".

Ji yayi andafa kafad'arsa ta baya ya juya da sauri sai yaga ashe Yarima Fudhal ne ya kuwa had'e girar sama data k'asa, ya dubi Aynu yana fad'in.

"Ke...!, tashi ki fita".

Sum-sum Aynu ta fice dama neman hanyar fita ta keyi, Yarima Jalil kwafa yayi yana cijen lab'e yabar k'ofar d'akin, domin yasan yanzu kome zai yi Yarima Fudhal bazai kulashi ba  kuma ba zai tsaya suyi maganar arzik'iba tunda ya d'aure fuska.

Assalamu alaikum

Nagode sosai 'yan uwa da abokan arzik'i abisa addu'arku agareni Allah yabani lafiya sosai, masu inbox zuwa call da message ina godiya Ubangiji Allah yasaka da alkhairi amin.

Zaku cigaba da jina insha Allahu kamar ko yaushe.
[18/07, 18:08] Nana Sales Aliyu Fbk Mai Quratu Group: *YARIMA FUDHAL*

Na
FIRDAUSI S.A (QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

SADAUKARWA:-Namesy ta Pheerdauceey Jeebour.

Wannan page naki ne Tawan ta hannun damana HAFSAT M. ki morewa abinki.

09

Aynu na fita can baya taje ta samu waje babu kowa ta zauna abinta tana nazari a kan abubuwan da suka faru, a haka Zainab ta tadda ita.

Neman guri tayi kusa da Aynu ta zauna tana tambayarta  "lafiya kuwa?".

Aynu bata ji komai ba ta kwashe dukkan abin da ya faru ta sanar da ita sai dai ta b'oye abu guda bata fad'a mata ba, wato ganin da ta yiwa Yarima wanda aganinta  bai dace ta fad'awa kowa ba.

Zainab tace.

"Haba Aynu wannan d'an abin shine kuma abin da zai ta da hankalinki, ki kwantar da hankalinki wallahi babu abin da zai faru insha Allahu".

Nan dai tayi ta jan Aynu da hira har ta samu ta war-ware daga damuwar da take ciki, kafin su mik'e su koma ciki domin k'arasa ayyukansu, Zainabu tayi b'an garen Fulani Bingel ita kuma ta nufi b'an garensu Yarima.

***

"Ni kuwa mai Martaba dama akwai wata shawara da nakeson baka akan Magaji !".

Mai Martaba dake kishin gid'e kan kusun ya d'an sake gyara kwanciyarsa, Fulani Sokoto ta mik'o masa yan kakken tufa d'in da yake ci yakarb'a ya kai bakinsa yana fad'in.

"Ina jinki, wacce shawara ce wannan?".

"Kan batun auren Magaji da kake taso yayi shi kuma kaga har yanzu baice komai ba, wata k'ila baiga wacce yake so ba, shi ne nace mai zai hana anema masa auren Gimbiya Safiyya !".

Mai Martaba yayi shiru yana duban Fulani Sokoto cike fa nazari bisa maganar da tayi yanzu can ya gyad'a kai yana fad'in.

"Shawara mai kyau Safiyya 'yar Sarki Maina yarinyace mai tarbiya ai babu wanda zai ganta yace batayi masaba, gaskiya naji dad'i sosai akan wannan zab'in da kika yiwa d'an namu".

"Mai Martaba kenan ai nima d'ane a wajena inda abin da yafi hakama zanyi masa".

"Gaskiya ne aikuwa zamuje nema masa aurenta batare da b'ata lokaci ba".

Tuni wani sanyin dad'i ya ziyarci zuciyar Fulani Sokoto domin tarkonta ya kama, addu'arta d'aya Allah yasa kada ta samu matsala da Yarima Fudhal kuma?.

***

Kwance yake falo kan d'aya daga cikin kusun d'in dake falon rawar sanyi yake sosai amma ya kasa tashi ya nufi d'aki ko ya nemi abin da zai rufa dashi gashi wayarsa ma tana cikin d'akin, bai jin zai iya d'aga ko da dai-dai da yatsansa d'aya bare ya bud'e baki yayi magana.

A haka Aynu tayi sallama cikin falon ta taddashi, k'ara sawa tayi da zauri zuwa inda yake tana

tambayarsa lafiya? ganin da tayi jikinsa sai rawa yake yasa ta fahimci cewa sanyi yakeji.

Mik'ewa tayi ta nufi d'aki ta d'auko masa k'aton bargon da yake rufa dashi ta zo ta rufa masa sannan ta koma ta fara aikin ta mintuna kad'an da gama wankin toilet tana gyara cikin d'akin ta dinga jiyo kakarin amansa, ta fito zuwa falo taga yayi aman bisa carpet ne kawai amma ban da jikinsa .

"Ko inkirawo maka Yarima Jalil ne?".

Kai ya girgiza mata alamun a'a, Aynu tayi shiru tana dubansa shima ita d'in yake kallo.

"Ko a kira Hajiya?".

"Bana buk'atar kowa".

Abin da yace da ita kenan kawai, tayi shiru na tsawon lokaci kafin ta sake fad'in.

"To koma d'aki in gyara falon".

Dubanta ya tsayayi yana k'ok'arin bud'e bakinsa domin yin magana amma kuma maganar tak'i fita, a hankali ya dafa bango ya mik'e yana tafiya har ya isa d'akin toilet ya wuce ya watsa ruwa a daddafe tare da wanke baki ya fito ya sanya jallabiya ya kwanta.

Aynu ta gyare falon tas tasanya turare aranta tana jin tausayin Yarima domin tasan bak'aramin ciwo ne zai kwantar dashi har haka ba.

Lokaci-lokaci takan lek'a tayi masa sannu ta dawo ta cigaba da aikinta, sai da ta gama komai sannan ta koma ta tambayeshi koyana buk'atar wani abune?, Ruwan tea kawai ya buk'ata ta kawo masa.

Lokacin k'arfe bakwai da mintuna arba'in da yake tazo da wuri yau burinta bai wuce ta samu ta koma gida da wuriba sabida wani dalili nata.

Kitchent ta nufa ta sanar da buk'atar Yarima nan da nan aka mik'o mata flast da cofuna da sauran tarkacen kayan tea.

A gabansa ta ajiye ta zuba masa ruwan tea d'in kawai da sugar domin yace baya buk'atar komai da k'yar yamik'e ya karb'i tea d'in yana sha, ita kuma ta fice daga d'akin ta nufi wajen Fulani Bingel wato mahaifiyarsa domin ta sanar da ita halin da yake ciki.

Tare suka tawo da ita da sauran ma'aikatanta, sukayi masa sannu suka fice ni dama falo nayi zamana muna shigowa, Yarima Jalil ne ya shiga yayi masa sannu shima ya fito ya koma

d'akinsa, cikin k'ank'anin lokaci ciwon Yarima Fudhal ya bazu ko ina sai faman dubiya ake zuwa abin har ya bani mamaki, sai na tuna da ni kaina idan zamuyi wata nawa muna ciwo sai wanda ya zama dole yake zuwa dubamu, Allah sarki arayuwa idan a kace kud'i da mulki angama komai.

Fulani Bingel ta jima a tare da shi komai ta tambayeshi yana so sai yace A'a daga k'arshema cewa yayi baya buk'atar masu zuwa duba shi suna k'ara masa ciwo ne, mu dai muna zaune falo munyi jugum, can sai ga Fulani sokoto tazo duba shi sai da tak'are mana kallo tana wani yatsina sannan ta wuce ciki.

Tare suka fito da Fulani Bingel tana fad'in.

"Aynu ki kula dashi yace baya buk'atar kowa likita zai zo nan da anjima ya dubashi ".

"To angama Fulani".

Abin da nace kenan na koma na zauna, Fulani Sokoto ta bini da wani mugun kallo tana mai ficewa, suma sauran ma'aikatan suka takewa Fulani Bilgel baya suka fice, suka barni ni kad'ai zaune falo kamar wata mayya.

Har doctor yazo ya dubashi yayi masa allurai sannan ya kirani yayimin bayanin magun-gunansa da yanda za'a dinga bashi ya tafi, na nemi guri na zauna ina kallon yanda yake fitar da numfashi da kyar hucin zafin jikinsa kuwa ina daga inda nake ina jiyo zafin.

Ganin alamun yana magana nayi na k'arasa da sauri zuwa dai-dai kansa domin idan ba haka kayi ba ba zakaji mai yake cewa ba, sai ji nayi ya kamo hannuna yarik'e kam ya had'a da hannusa, har sai da naji zafin rik'on ga kuma zafin jikinsa, a haka na zauna ina kallon ikon Allah domin da nayi k'ok'arin janyewa zai hud'e ido yana girgiza kai alamun kar incire, araina nace.

"Sai kace wani k'aramin yaro, kome yake damunsa ma oho?".

A haka har bacci mai nauyi ya d'aukeshi sabida allurar da akai masa na samu na cire hannuna na dawo falo na zauna ina kallom TV films d'in india ne ake duk da bana fahimtar abin da suke cewa amma kallon yana min dad'i sosai, na jima a zaune sai ga Yarima Jalil ya shigo ya zauna na gaishe shi yana tambayar mai jiki nace.

"Yayi bacci ma".

Da haka yayi ta jana da hira jefi-jefi har na mance a tare da waye nake ga Yarima Jalil akwai ban dariya tuni na ware yana bani labaran abin dariya ina dariya, abin da yake burgeni dashi kenan ba ruwansa da girman kai illa abu biyun da sukaiwa rayuwarsa illa ban dasu na fahimci Yarima Jalil na da kirki sosai har yafi Yarima Fudhal ma anawa ganin kenan.

Ya gama bani wani labari ina cikin dariya sai ganin mutum kawai mukayi a kanmu kamar mala'ikan mutuwa haka muganshi a tsaye.

Yarima Jalil ya washe baki yana fad'in.

"Sannu broda ka tashi kenan, ya k'arfin jikin?".

Idan TV d'in dake d'akin tayi magana to shima yayi magana, nima na durk'usa inayi masa sannu wani kallo ya watsomin daya sanya hanjin cikina k'ullewa ba k'aramin k'ok'ari nayi ba wajen rik'e fitsarin da yayi shirin zubomin a wando.
[19/07, 17:42] Nana Sales Aliyu Fbk Mai Quratu Group: *YARIMA FUDHAL*

Na
FIRDAUSI S.A(QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

SADAUKARWA:- Namesy Pheerdauceey Jeeebour

Wannan page d'in naki ne FIRDAUSI SODANGI A cigaba da suburbud'a mana cakwakiyar KWAD'AYI MABUD'IN WAHALA muna tare da ke har zuwa inda al'kalamin ki zai tsaya.

10

Na mik'e tsam na koma waje guda na zauna ina jiran umarninsa.

"Sannu Broda Allah yak'ara lafiya".

Cewar Yarima Jalil kenan yana mai ficewa daga d'akin.

"Ke zo nan".

Na mik'e da sauri na k'arasa wajensa ya kafeni da sexy eyes d'insa da bana iya juran kallonsu, ya jima a haka kafin ya bud'e baki ya fara magana.

"Kada insake ganin ki tare da Jalil".

"To".

Na sake mik'ewa na nufi cikin d'akinsa na d'auko magun-gunansa na d'auko ruwa a robar faro na kawo na ajiye, ina mai b'alli maganin na mik'a masa ya karb'a yasha ya jawo kusun ya koma ya kwanta, sai lokacin na lura k'arfe biyu tayi ashe dubansa nayi ina fad'in.

"Zan iya tafiya?".

Bak'aramin k'arfin hali nayi ba wajen tambayarsa domin bansan amsan da zai bani ba.

Kai kawai ya d'agamin alamun ehh, na mik'e da sauri ina k'ara yi masa Allah sauwak'e na fice daga d'akin duk da ban juya ba amma nasan ni yake kallo.

Kitchen na nufa kai tsaye naje na juye abincin nayiwa Jakadiyya sallama na tafi gida, araina ina tunanin rashin zuwan Saima yau.

"Ko da yake jiki da jini a kace".

***

5:00pm

"Assalamu alaikum wai Aynu tazo".

Aynu dake shara tsakar gidan ta ajiye tsin-tsiyar tana tambayar.

"Waye ya aiko ka  Mallam?".

"Ya Sayyadi ne fa na Islamiyya !".

"Au kace ina zuwa".

Yaron da ta kira da Mallam ya fice domin isar da sak'onta.

Aynu ta shige d'aki ta d'auko hijab d'in islamiyyarta tana mai duban Ummanta.

"Umma bari inje wai Ya Sayyadinmu ke kira na".

"To sai kin dawo a kula dai da kyau".

"To Ummata".

Aynu ta sanya ta mutsats-tsan silifas d'inta ta fice.

Yana tsaye jikin bishiyar darbejiyar k'ofar gidan, fari ne d'an siriri mai doguwar fuska sai saje bak'i da yayiwa fuskarsa k'awanya da ka ganshi ka ga tsan-tsan bafulatani, yana sanye da jallabiya fara har k'asa da hula fara da ake kira tashi ka fiye naci.

Aynu ta k'arasa wajensa fuskarta cike da fara'a kamar yanda tasa take, ta d'an rissina ta gai dashi ya amsa yana fad'in.

"Malama Aynu kwana biyu na jiki shiru bakya zuwa makaranta?".

Aynu ta d'anyi murmushi tana mai gyara tsayuwarta tare da fad'in.

"Wallahi Ya Sayyadi aikin dana samu ne sai a hankali, ban cika da wowa gida da wuri ba".

"To ikon Allah adinga dai daurewa ana zuwa".

"Insha Allahu kuwa".

Zuwan Babanta dake shirin shiga gidan ya ka tsesu daga tattau nawar da suke, Ya Sayyadi ya durk'usa ya gaishe da Babanta cikin girmamawa, shima ya amsa fuskarsa fal farin ciki ya wuce ya barsu nan, yana shiga gida Ya Sayyadi yayi mata sallama ya tafi ita kuma ta koma cikin gidan.

Tana shiga taji Ummanta da Baban nata suna tattaunawa akan Ya Sayyadin ita dai bata tsaya taji mai suke fad'iba ta cigaba da aikinta ganin babu wanda ya sakota a zancen.

*** *** ***

Yaune ta kama ranar da za'a fara biyan su Aynu albashi, tun asuba ta tashi zuciyarta fes cike da nishad'i, nan da nan ta kammala komai nata na gidan kafin k'arfe bakwai da yake Zainab ta bata wani k'aramin agogo da shi take amfani, bakwai nayi taci abinci tayi komai ta kama hanyar zuwa gidansu Zainab domin su tafi tare.

Tana isa ta tadda itama ta gama shiryawa suka kama hanya.

Yau dai ta tadda Yarima Fudhal ya war-ware tsaf har ya tashi yayi wanka ya shirya yana zaune gefan katifarsa ta taddashi, ta durk'usa ta gaishe da shi ya amsa fuskarsa cike da fara'a, ta mik'e ta nufi toilet ta kama aikinta.

Tana fitowa ta cigaba da sauran gyare-gyarenta k'arfe takwas akai kiransu za'a bawa kowa kud'insa na aiki.

Su nasu b'an garen har k'ari suka samu daga dubu goma sha biyar zuwa a shirin ba k'aramin dad'ine ya rufe Aynu ba sosai tana tafe tana lissafin abubuwan da zasu siya sai ji tayi taci karo da mutum taja baya da sauri tare da d'ago kai sai taga ashe Yarima Fudhal ne, ya kuwa had'e fuska kamar bashi ne ta ganshi d'azu cikin fara'a ba.

"Bani kud'in !".

Yayi maganar babu alamun sassauci, jiki na b'ari ta mik'a masa yasake kallonta yana fad'in.

"Jeki kawomin breakfast".

Ba musu ta juya ta nufi kitchent domin cika umarninsa.

Haka tayi ta zaryar shirya masa breakfast sai da ta gama ta had'a mai komai ta mik'a masa sannan ta koma gefe tana jira ya gama, komai baya wuce cokali d'aya zuwa biyu yake ci ya gama ta kwashe kwanukan ta mayar ta dawo ta zauna kenan yace taje ta kawo masa fruit, haka ta sake mik'ewa taje ta kawo, ta kuma zauna a gefansa yana daga kishingid'e tana yankawa tana mik'a masa yana sha, musamman apple ta fahimci yana cinsa sosai.

Sai da ya gama ta kwashe ta mayar ta dawo ta zauna ta jira taji yace ga kud'inta ta tafi, amma taji shiru gashi tana jin nauyin tambayarsa sai dai ta dubeshi kaman zatai magana sai taji ta kasa.

Sun jima a haka kafin yamik'e ya shige cikin d'akinsa, ya barta nan zaune tana tufka da war-wara.

"Aynul-hayat !".

Taji ya kira sunanta ta amsa a hankali tana mai nufar d'akin nasa da sallamarta ta sanya kai d'akin.

"Zo nan".

Ya kuma kiranta ta k'arasa inda yake a zaune gefan katifa ta durk'usa tana kallon ikon Allah.

Kud'ine dank'am a gabansa tun daga dollar zuwa dubu-dubu d'ari biyar-biyar 'yan d'ari biyu har zuwa kan naira biyar kowanne bandir-bandir.

"D'ebi duk yanda ki keso".

Aynu ta saki baki tana dubansa, sai take ganin abin kamarma wasa yake mata.

"D'ebi mana".

Ta kai hannu kan 'yan goma ta d'auka, dariya ya d'anyi yana fad'in.

"Sarkin tsoro".

Karb'a yayi ya d'auki bandir d'in 'yan dubu ya mik'a mata, girgiza kai tayi alamu a'a, shiru yayi Yarima yana dubanta cike da mamaki fal cikin ransa.

"Kyauta tace a gareki karb'i".

"A'a nidai ka bani kad'an, sunmin yawa wad'annan".

Jujjuya kud'in yayi tayi na wani lokaci kafin yayi murmushi yace.

"To idan na k'ara miki goma akan naki zaki karb'a?".

Shiru tayi ba tare da ta ce dashi komai ba, ya irgo dubu talatin ya mik'a mata ta k'i karb'a.

"Idan baki karb'i wannan ba sai dai ki rasa kud'in naki duka".

Aynu ta dube shi da sauri ya gyad'a kai alamun da gaske yake, hannu biyu ta sanya ta karb'a tana yi masa godiya, yace baya buk'atar godiya nan da nan taja bakinta ta tsuke.

***

Aynu ce zaune gaban Ummanta tana faman lissafin abin da ya kamata su saya, Ummanta ta murmushi tayi tana fad'in.

"Aynu kenan !, to ai duk lissafin da kike kud'in ba zasu kai ba sai dai asayi abin da ya samu kawai".

"To Umma amma dai ya kamata musayi atamfa ko ta dubu d'aya da d'ari biyu ce, sai a asiyawa Baba yadi shi kuma ya d'inka, sauran sai mu sayi takalma da ta barma ko?".

"Uhmmm yanzu dai d'auki dubu biyu ki kaiwa mai shagon da muke karb'o sabulu, ki bashi dubu kud'insa ne da yake binmu, dubu d'ayan kuma ki siyo silifas ki sayo mana sabulun wanka da wanki tare da makilin".

"To Ummata".

Ta fad'a tana mai mik'ewa tare da d'aukan kud'in ta fice.

A hanya ta gamu da Ya Sayyadi suka gaisa yana fad'in.

"Ina zaki haka da rana tsaka?".

"Ummata ce ta aikeni".

"To masha Allahu muje in taka maki".

Haka suka tafi suna hira jefi-jefi har zuwa shagon tayo siyayyar suka dawo tare har k'ofar gida ya rakota sukai sallama ya tafi.

A ranar dai aka siyawa Aynu sabon hijab da atamfa  Daviva guda biyu suka sayi sabuwar tabarma da 'yan kwanuka da cofuna domin nasun duk sun lalace.

Aynu sai jinta take kamar sun shiga wata sabuwar rayuwa, jinta take kamar ba ita ba yau ita ce da sabon d'inki abin da sai dai abata kwance yau kuwa gashi ta d'inka da guminta.

"Alhamdulillahi, Alhamdulillahi ala kulli halin !".

Abin da take ta faman mai-mai tawa kenan cikin ranta cike da nishad'i da jin dad'i.

7:40am

Yau dai Saima ta rigata zuwa gidan, sabida yau ta makara sosai ko da ta gaishe da Yarika k'in amsawa yayi bata damu ba domin tasan halin sa, tayi dukkan abin da ta saba ta gama ta nemi guri ta zauna, har lokacin ko kallonta bai yiba gefe guda kuma ga Saima sai faman wani ciccika take tana batsewa da zaran sun had'a ido da Aynu ta jefe ta da harara.

"Zaku iya tafiya".

Suka ji muryarsa yana basu umarni, ko wacce tamik'e ta fice daga d'akin a hanyane Aynu ta dubi Saima tana fad'in.

"Kwana biyu bakya zuwa har anyi albashi....".

Bata k'arasa maganar ba Saima ta katseta da fad'in.

"Ke kud'in ya dama".

Ta wuce ta barta nan tsaye tana searching d'in maganar Saima.

"Me take nufi da ni kud'i ya dama?".

Kafin ta kai da bai wa kanta amsa sai ganin Yarima Jalil tayi a gabanta fuskarsa fal murmushi yake fad'in.

"Beauty kin b'uya !? ko da yake naga Yayan namu baya buk'atar ganinmu tare".

Aynu ta tsaya tana nubanshi dan ko kad'an bata fahimci inda maganarsa ta dosa ba.

"Zauna nan  magana za muyi da ke".

Yayi mata nuni bisa d'an da kalin dake kusa da su, Aynu ta zauna shima ya zauna gefe da ita kad'an.

"Kin san wani abu?".

"A'a sai ka fad'a".

"Wai me yasa Yarima baya son gani na da ke ne?".

"Nima ban sani ba gaskiya".

"Ok".

Shiru ne ya biyo baya na d'an wani lokaci, kafin yasake dubanta yana fad'in.

"D'an juyo nan".

Aynu ta zuyo tana dubansa, ya kai hannu gefan fuskarta yana fad'in.

"Wani abu ya b'ata beauty face d'inki bari in goge miki".

"Jalil.....!".

Suka ji muryar Yarima Fudhal akansu, Yarima Jalil ya sauke hannunsa yana fad'in.

"Sannu da fitowa Broda".

Bai ko dubeshi ba, illa kafe idanuwansa da suka fara rinewa daga fari zuwa ja akan Aynu da yayi, a hankali ya furta.

"Jeki k'arasa aikin ki".

Sum-sum Aynu ta wuce zuwa falon Yarima ita dai tasan ta gama aikin ta, may be wani aikin zai saka ta abin da ta raya aranta kenan.

Mintuna kad'an da zamanta ya shigo fuskarnan babu annuri neman guri yayi ya zauna yana fad'in.

"Had'amin tea".

Da rawar jiki ta mik'e ta zuba masa tea d'in tafa shashshe sosai, yace ka da ta sanya komai illa sugar nan da nan ta had'a ta mik'a masa yasa hannu ya karb'a, tana shirin mik'ewa taji ya jawo hannunta kafin ta ankara sai jin rad'ad'i da azabar zafin ruwan tea d'in tayi bisa hannunta wanda ya ratsa har cikin kwakwalwar kanta.
[20/07, 14:40] Nana Sales Aliyu Fbk Mai Quratu Group: *YARIMA FUDHAL*

Na
FIRDAUSI S.A(QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

SADAUKARWA :-Namesy Pheerdauceey Jeebour.

(RAZ) ku matso kusa wannan page d'in nakune AMRAH, ZAHRA, RABI'ATU....Allah yabar manaku ya k'ara donk'on zumunci da k'aunar juna Inayin ku irin sosai d'innan (Raz).

11

Har cikin kwakwalwar kanta ta jiyo rad'ad'i da zafi na ruwan tea d'in, ta kafe Yarima da idanuwa cike da kallon mamaki mai d'auke da tambayar me nayi maka?.

Shima Yarim ita ya kafe da idanuwa yana karantar yanayinta can ya kau da fuska gefe yana mai naushin hannunsa na hagu da hannun da mansa game da furzar da iska daga bakinsa mai zafi.

Aynu kuwa ta kasa magana illa hawaye dake zarya bisa kuncinta kawai tarik'e hannun da d'ayan da babu k'unar.

Yarima yayi k'asa da kansa ya dafe da hannu na d'an wani lokaci, kafin ya d'ago ya sake kafeta da ido a karo na biyu, tsaki ya d'anja kad'an yana mai sanya hannunsa ya kamo nata daya k'ona ya dubi hannun tare da duban fuskarta.

"Am so sorry...nayi hakanne domin ki fahimci irin k'unar da na keji a duk lokacin dana ganki da Jalil, why me yasa kika kasa fahimta har na kai da yi miki wannan hukuncin?".

Ita dai Aynu kallonsa kawai take domin ko kad'an bama ta fahimtar me yake fad'i, azaba ta isheta hawaye kawai take fitarwa domin kuka mai sauti ma k'in fita yayi daga bakin ta a wannan lokaci.

Kai hannu yayi kan fuskarta da niyan share mata hawayen sai kuma ya fasa, ya dubeta yana fad'in.

"Da zafi sosai ne?".

Kai ta kyad'a masa alamun ehh.

"Sannu yi hak'uri !".

Abin da yace da ita kenan yaja hannunta suka fito zuwa waje, haka yayi ta janta har suka isa b'angaren Fulani Bingel duk inda suka wuce sai a bisu da kallo amma kasancewar Yarima Fudhal ne kowa yasan babu wasa da sun had'a ido da mutum zaiyi k'asa da kansa yana gaishe shi.

Shi kuwa Yarima bai cika niba har sai da muka isa cikin falon mahaifiyarsa, Fulani Bingel na ganinmu ta mik'e tsaye tare da fad'in.

"Lafiya Magaji?".

"Hajiya kira doctor d'inki ".

Fulani Bingel ta bishi da kallon mamaki cike da tambaya.

"Mai ya faru da ita?".

Yarima neman guri yayi ya zauna ya dubi sauran masu aikin dake d'akin.

"Ku bamu waje".

Sum-sum ko wacce ta fice ya rage daga ni sai Yarima da Hajiyarsu.

Fulani dai ta kafeshi da idanuwa tana jiran amsar sa.

Yarima yad'an yatsina fuska kafin ya bata amsa da fad'in.

"K'onata nayi".

"Subhanallah ! garin yaya?".

Cewar Fulani kenan tana mai k'arasowa wajena, taga hannuna yayi jawur ta mai da dubanta kan Yarima.

"Akan me ka aikata wannan d'an yan aikin?".

"Hajiya ita ta jama kanta fa !, na gaya mata bana son ganinta da Jalil ba ta ji ne yarinyar !".

"To dan baka son ganin ta da Jalil sai kayi mata wannan mugun hukuncin ?, mai yasa bazaka fad'amin ba ko kayi mata hukunci dai-dai misali".

"Abin da nake ji araina ne !, shine na gwada mata taji yanda nakeji ko tafi fahimta".

Fulani Bingel sakar baki tayi tana duban sa cike da mamaki ko mamakin me take yi oho?, sai dai ta kalleni ta kalleshi.

Ajiyar zuciya tayi tana fad'in.

"Mai zai hana ka kira likitanka?".

"Haba dai Hajiya Namiji ne fa?".

"Dan namiji ne bazai duba taba".

"Ina ! A'a gaskiya ki taimake ni dai ki kira likitarki dan Allah Hajiya kinji?".

Ya k'arashe maganar kamar zaiyi kuka, ni dai ina zaune ina jin ikon Allah tun da nake da Yarima yaune karo na farko da yayi doguwar magana kuma duk a kaina, ga shi kuma babu ko kunya ko nauyi ko shakka bare jin tsoro yana sanarwa mahaifiyarsa da kansa ya k'ona ni !, nidai sai na nemi hawaye na rasa tsabar mamaki da al'amarin Yarima Fudhal.

Hajiyarsa girgiza kai kawai tayi tana dubana ta d'auki waya bugu d'aya tayiwa likitan bayanin abin da yake faruwa, muna ji likitan ta amsa da cewar ga tanan zuwa da yake wayar a free ta sanya ta.

Hajiya ta ajiye wayar tana kallon Yarima da yayi ta gumi yana kallonta, ta jima tana nazarin Yarima Fudhal ba tare da tace komai ba, haka shima bai kuma fad'in komai ba, baka jin k'arar komai a d'akin sai k'arar A.C da ajiyar zuciyata jefi-jefi sabida kukan da nayi.

Muna haka har Doctor Hafsat ta shigo ta tadda mu, ta gaishe da Hajiya da Yarima Hajiya tayi mata bayanin nice na k'one da ruwan zafi, nan da nan tayimin allura tare da bani magani domin k'unar bata tashi ba bare ace za'a wanke, tayiwa Hajiya sallama ta tafi domin tana bakin aiki ne ta tawo.

Tana fita Hajiya tace.

"Ka da ka sake mai-maita hakan kana jina?".

"Insha Allah".

Abin da yace da ita kenan, yana mai kwanciya kan kusun, Hajiya tace.

"Mai yake shirin faruwa  tsakaninka da yarinyar nan?".

Yarima ya mik'e ya zauna tare da dubana yana fad'in.

"D'an bamu waje".

Na mik'e na fice abina dama duk a takure nake jina.

"Ka da dai kacemin sonta ka ke?".

Murmushi Yarima yayi yana sosa k'eyar kansa jin tambayar da Hajiyan tasa take yi masa.

Fulani Bingel tayi ajiyar zuciya domin ta fahimci komai tun farkon tattauna warsu.

"Ka da kamance 'yar aikin kace, 'yar aiki kuwa a gidan nan tamkar bayi ne ko ka mance ne?".

"A'a".

"Kasan ko Mai Martaba bazai tab'a yarda ba idan ni na amince !".

Dammm gaban Yarima ya buga amma ya dake ba tare da yace komai ba, Fulani ta cigaba da fad'in.

"Duk bama wannan ba, kasan cewa ana nema maka auren Gimbiya Safiyya kuwa?".

A firgice Yarima ya dubi Fulani.

"Safiyya kuma ni nace ina sonta ne har da za'a nema min aurenta?".

"A'a zab'in mahaifinka ne, to ita wannan d'in tasan kana son tane?".

"A'a amma ai zan fad'a mata lokaci nake jira, amma Hajiya da gaske kike akan maganar Safiyya?".

"Na tab'a yi maka wasa ne ?".

Yarima ya girgiza kai alamun a'a, yayin da kuma zuciyarsa ke ta aikin bugawa da sauri da sauri hankalinsa idan yayi dubu ya tashi, har sai da Fulani Bingel ta fahimci haka ta dafa kafad'arsa tana fad'in.

"Kada ka d'aga hankalinka Magaji ka nemi zab'in Allah kawai, domin kafi kowa sanin waye Mai Martaba".

"Amma Hajiya ki fahimtar dashi mana nifa gaskiya bana sonta".

"Kai mai zai hana ka sanar dashi, zaifi fahintar maganarka akan tawa ma".

Yarima ya dubi Mahaifiyartasa kafin ya kau da kai gefe zuciyarsa na cigaba da k'una, gefe guda kuma yana tunanin mafita akan wannan batun.

***

Aynu kuwa na fita inda ta saba zama taje ta zauna ta had'a kai da gwiwa tana kuka, ji tayi an dafa kafad'arta ta baya ta d'ago da sauri dan ganin waye?.

Zainab ce ta zagayo ta zauna tana fad'in.

"Subhanallahi !, Aynu mai ya faru kike kuka ya akayi kika k'one ke da ba a kitchen kike aiki ba?".

"Yarima ne Zainab, Yarima ne !".

Aynu ta sake fashewa da kuka tana mai d'ora kanta kan cinyar Zainab, Zainab ta d'an bubbuga bayanta alamun rarrashi tana fad'in.

"Mai kikayi masa?".

"Wai akan Yarima Jalil...".

Nan dai ta kwashe dukkan abin da yafaru ta sanar mata, Zainab tayi ajiyar zuciya tana fad'in.

"Kece bakyaji ai na gaya miki waye Jalil kin k'i yarda, amma abin tambaya kenan Yarima Fudhal yana kishin ganinki da Yarima Jalil?, Idan har kishi yake kenan sonki yake ko?".

"Oho nima nasani jeki tambayeshi".

Zainab dariya tayi domin wasu lokutan tasan Aynu 'yar rigimace ta k'arshe, a fili kuwa cewa tayi.

"A'a mai da wuk'ar bani nakar zomon ba ratayarma ban d'auka ba".

Aynu tad'an kaiwa Zainab dukan wasa, tana fad'in.

"Ni ko sona yake Allah bazan soshi ba mugune wallahi na k'arshe".

Zainab tayi murmushi tana fad'in.

"Ki godewa Allah Aynu samun irin su Yarima Fudhal wuya garesu a yanzu, wallahi nayi miki murna sosai Allah tabbatar mana da alkhairi, ni yanayin soyayyar tashi ne ma ta fara burgeni !".

Wani kallo Aynu ta jefi Zainab da shi mai dauke da harara.

"Wai ke waya gaya miki sona yake ?, nifa bai fad'amin ba".

"Daga jin yanda labarin ya fara kowa kika sanarwa Allah yasan al'amarin so ne yaja hakan, domin idan ba so ba mata nawa ne suke harka da Yarima Jalil a gidan nan amma bai da muba sai a kanki, nasan wata rana zai fad'a miki yana sonki".

"Tab..Allah ma ya kiyaye, dubi fa hannu na wanda yayi maka haka kuma yazo yace yana sonka?".

Cewar Aynu kenan tana mai k'arewa hannunta kallo cike da takaici, ba tayi aune ba sai ji tayi ruwan hawaye na bin fuskarta.

Nan sai suka Zauna Zainab na k'ok'arin ganar  da ita amma ita tana faman botsewa da haka har k'arfe biyu tayi basu sani ba, a gurguje suka had'a inasu inasu sukayi gida, dan Aynu ko part d'in Yarima k'in komawa tayi dan kada wani abun ya sake faruwa.

Yarima na dawowa sallah yahau nemanta  amma sama ko k'asa ya rasa ta sai Jakadiyya ke sanar dashi sun tafi gida, kwafa yayi yana duban maganinta da aka bata  yana tunanin yanda za'ai ta sha domin kada k'unar ta tashi kafin gobe, hankalinsa idan yayi dubu ya tashi, sai dabara tazo masa ya baiwa Jakadiyya ta kai mata domin yaga ta san ta, ba musu Jakadiyya ta karb'a ta nufi gidan su Aynu domin kai mata maganin lokacin kuwa daf da maghriba ne.

***

Ko da Aynu ta koma gida k'in sanarwa Ummanta abin da ya faru tayi, duk da cewar Umman taji muryarta ta canja tayi tambayar duniya akan meya sata kuka?, Aynu tace .

"Babu komai Umma kawai tari na d'anyi".

Nan dai ta k'ok'arta tayi dukkan abin da zata iya ta nufi Islamiyya dawo warta kenan ta shiga d'aki ta cire hijab taji sallama, ta fito domin ganin waye sai taga ashe Jakadiyya ce har Umma ta bata gurin zama.

Aynu ta fito suka gaisa tamik'awa Umma ledar maganin tana fad'in.

"Gashi Aynu maganin naki, Yarima duk ya tashi hankalinsa yace kisha kafin ki kwanta, Allah ya k'ara sauk'i ni zan koma".

"To mungode Allah saka da alkhairi ki gaida gida a yiwa Yarima godiya sosai abisa d'awainiya".

Cewar Umma kenan dake zaune gefen tabarmar da Jakadiyya ta zauna.

Jakadiyya tayi musu sallama ta tafi, Aynu dai mutuwar tsaye tayi tana jira taji mai Umman zata ce da ita.

"Zo nan Aynu".

Taji muryar Ummanta Aynu ta k'arasa kusa da ita ta zauna tana fad'in .

"Gani Umma".

"Fad'amin gaskiya mai ya faru?".

"Dama....dama fa...dama Umma ruwan zafi ne ya zubomin a hannu".

"Amma shine zaki min k'arya kice ba komai tari ki kai".

"A'a Umma kawai banaso hankalinki ya tashi ne ".

Murmushi Umman tayi tana fad'in.

"Aynu kenan, bani hannun inyi miki tofi".

Aynu ta mik'a mata hannun, Ummanta ta kama tayi mata addu'a kafin ta saki hannun tana fad'in.

"Da ace kina k'onewa ansamu gasarar koko anzuba akai ba zata tashi ba, domin k'una sanyi take so, da zarar ansanya gasarar iska na kad'awa har ta bushe shikenan ba zata tashi ba".

"Umma ai yanzuma bata tashi ba kawai dai ja hannun nawa yayi".

"To Allah sauwak'e ya kiyaye gaba ki dinga lura da kyau dai".

"To ummata".
[22/07, 20:22] Nana Sales Aliyu Fbk Mai Quratu Group: *YARIMA FUDHAL*

Na
FIRDAUSI S.A (QURRATUL-AYN)

SADAUKARWA:-Namesy Phirdauceey Jeebour.

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

12

Washe gari wayar gari akai Mai Babban d'aki wato Mahaifiyyar Mai martaba babu lafiya, baki d'aya hankalin kowa ya tashi da ka shiga gidan zaka san babu lafiya musamman Yarima Fudhal da Mai Martaba sunfi kowa shiga damuwa da ciwon Mai Baban d'aki.

Ciwo anwayi gari da shi rana d'aya amma kai kace tayi shekara tana yi, tuni aka d'ebeta sai asibiti likitoci uku ne akanta amma sun kasa gano musabbabin ciwon nata bare har asan abin da za'ayi akai.

Ni dai tun da muka doshi gidan ni da Zainab mukasan babu lafiya agidan, muna shiga kuwa muka samu bayanin Babar Mai martaba ce ba lafiya tana asibiti, Yarima ma nacan hospital d'in Zainab ce ta tayani gyara b'angaren Yarima sabida k'unar dake hannuna muna gamawa na nufi gida kuwa domin Saima ma da tazo ta tadda abin da yake faruwa bata zauna ba ta koma gida abinta.

***

Daf da maghriba kuwa Hajiyar Mai Martaba tace ga garin kunan, ba Sarkin ba duk wanda yaji mutuwar baiwar Allahn nan dole yayi kuka mace kamila mai hak'uri da dattako mai son addini da son iyalinta ga uwa uba barkwanci da faram-faram.

Gaskiya bak'aramin rashi su Yarima sukayi ba gari ya d'auka kaf da rasuwar baiwar Allahn nan, ni dai ina zaune a gida najiyo a babban masallacin unguwarmu ana sanarwa cewa za'ayi

jana'izar ta da safe idan Allah ya tashemu da rai da lafiya, ba wani shak'uwa mukai da ita ba amma naji mutuwarta sosai babu abin da yafara fad'omin arai irin so da shak'uwa dake tsakaninta da Yarima fudhal koya zaiji aransa oho?

"Allah sarki Yarima Allah baku hak'uri da dangana !".

Abin da nace kenan ina yankewa Ummata farce ta amsa min da.

"amin Aynu mutuwa ai dole ce sai dai in lokaci baiyi ba duk kuwa irin so da shak'uwar da kukai da mutum dole wataran zaka barshi".

Jikina yayi sanyi da kalaman Ummata sai naji hawaye nabin gefan fuskata har dai da na tuna Ummata da Baba na su kad'aine duniyata sune farin cikina su kad'ai na sani sune nake kalla inji dad'i, yanzu dole watara zan barsu ko su barni, duniya kenan babu matabbata Ubangiji Allah kasa mu dace ka kashemu da imaninmu amin.

***

Ka sancewar rasuwar da akai nasan kuma cin koso da jama'a yanzu sun cike gidan hakan ya saka nak'i zuwa washe garin da akai rasuwar, nayi zamana agida amma wunin ranar nayi shine cike da tunanin gidan.

washe gari kuma ranar biyu da rasuwar nayi niyar zuwa kodan inyi gaisuwa sai dai na tashi da wani irin matsanancin ciwon kai, Zainab data biyomin mu tafi har da ita asa bakin inyi zama duk da cewar naso zuwa amma Umma da Zainab suka kafe kan in zauna har zuwa gobe inga yanda jikin nawa zaiyi.

"Haba Fudhal kayi hak'uri kad'au dan gana abisa rashin Hajiya da mukayu mutuwa kasan dole ce amma sai da hak'uri, muma da muke mata munyi hak'uri bare kai namiji ?".

Cewar Yayarsu Aunty Sadiya kenan data iske Yarima d'akinsa shi kad'ai kwance kamar wani mara lafiya.

Falonsa abokansa ne cike amma shi ya wuce bedroom ya kwanta kamar mai bacci amma azahiri ba baccin yake ba domin duk abin da ake yana ji.

Ta gaji da magana amma ko d'ago kai baiyi ya kalleta ba, ta tashi ta fice daga d'akin ta koma wajen mahaifiyyarsu Fulani Bingel tana sanar mata.

Fulani tasan Yarima ya shak'u da Hajiya sosai amma tasan akwai wani abu daban da yake damunsa domin tasan waye Yarima tasan halayyarsa sarai, hakan yasa tayi murmushi kawai ta dubi Aunty Sadiya tana fad'in.

"Rabu dashi kawai akwai abin da dai yake damunsa, kar ki damu".

"Kamar ya ! Wanne abune yake damunsa haka?".

"Zanyi miki bayani wani lokacin".

Fulani Bingel ta wuce ta koma falo inda tabar jama'arta ke jiranta, ta bar Aunty Sadiya nan d'akin tana tunanin me yake damun d'an k'anin nata?.

Yarima kuwa gani yayi kwanciyar babu abin da zata haifa masa illa tarin damuwa mai yawa, hakan yasa shi mik'ewa ya fito harabar gidan yana dube-dube kome yake nema oho?.

Duk inda ya wuce sai gai dashi ake wani ya amsa wani ya wuce kawai da haka ya isa har filin shamaki inda bayi da ma'aikatan gidan ke zaune, suka durk'usa baki d'aya suna gai dashi ya amsa tare da k'urawa Zainab ido, yana tunanin indai bai mance ba tare yafi ganinsu da Aynu may be zata iya sanin wani information akanta.

"Ke zo nan".

Yayi nuni da Zainab ta mik'e da sauri tabi bayansa domin har ya bada baya ya tafi.

Wani guri yaja ya tsaya inda babu mutane yayi shiru kansa a k'asa bai ce da ita komai ba, har Zainab ta gaji da tsaiwa taji kaman zata fad'i, amma babu daman zama can ya d'anyi ajiyar zuciya ba tare daya d'ago kai ba yake fad'in.

"Ke kinsan Aynul-hayat ko?".

"Ehh Yallab'ai?".

"Ok mai yasa 2days bata zoba, ko gaisuwa ma tak'i zuwa ?".

"Ba tajin dad'i ne".

Yarima Fudhal ya d'ago kai da sauri yana dubanta, jin maganar da ta doki kunnensa.

"Me yake damunta?".

"Tace dai ciwon kai ne".

A jiyar zuciya ya saki mai k'arfi wadda har sai da Zainab ta dubeshi, ya cigaba da fad'in.

"Bani address d'inta".

Nan da nan Zainab ta bashi bayanin gidansu Aynu, tana gamawa ya juya ya tafi ya barta nan tsaye babu ko godiya Zainab tabi bayansa da kallo aranta tana fad'in.

"Ikon Allah maganar minti biyar amma ashafe awa guda da wani abu anayi, lallai Yarima na musam-manne Matarsa na da aiki kuwa".

Ta juya abinta itama tabar wajen ta koma inda ta taso.

•••

Aynu dai bata samu ciwon kan ya lafa mata ba sai dare wajen k'arfe takwas bayan sallar isha'i kenan, ta tashi tayo alwala ta hau gabatar da sallolin da bata samu ta iyayi ba, ta idar kenan tana addu'o'in data saba ko yaushe sukaji sallamar Yaro a tsakar gidansu.

Umma dake zaune gefe daga inda Aynu take sallah ta amsawa Yaron Sallama, ya gaishe da Umma yana fad'in.

"Wai ana kiran Aynu a waje".

"Aynu kuma da daren nan?".

"Ehh haka yace min Aynu yake nema".

Aynu ta sallame addu'ar tana fad'in.

"Kace ina zuwa".

Yaron ya fice Aynu ta dubi Ummanta tace.

"Yanzu haka Ya Sayyadi ne dan yaga yau banje Islamiyya ba".

"Ehh nima nayi tunanin hakan !, tashi kije kada ki jima dan kinga dare yayi".

"To Umma ni dama bana jin dad'i, tsayuwarma bazan iya ba muna gaisawa zan dawo".

Aynu tasa takalminta ta fice.

Dake dare ne kuma unguwar duhu basu da wadatar nepa, hakan yasa bata iya shaida kowane ba, yana tsaye jikin darbejiyar k'ofar gidan cikin k'ananun kaya daya tabbatarwa da Aynu ba ya sayyadi bane domin ta sanshi gwanine wajen shigar jallabiyya yau kuwa taga sab'anin haka, ta waiga bata ga kowa ba illa dai wanda ke tsaye jikin bishiyar.

Dake wa tayi tare da k'arawasa sai dai tun kan takai da isa wajen zuciyarta tahau bugun uku-uku ga kuma k'amshin turarensa daya doki hancinta wanda bata iya manceshi ko a wane yanayi taji shi zata gane nasa ne.

Shi kuwa tun fitowarta ya kafeta da idanuwa yayin da wani sanyin dad'i ya mamaye zuciyarsa, har yanaji aransa kamar yaje ya d'aukota don hutar da ita daga tafiyar da take.

Ta k'arasa wajen da sallam cikin siririyar muryarta ya masa mata ta d'an rissina ta gaisheshi tare da fad'in.

"Kayi hak'uri ban d'auka kai bane...".

Sai kuma tayi shiru, shima baice komai ba yayi shiru tare da nad'e hannunsa bisa k'irjinsa, a hankali ta d'ago kai duk da a duhu ne amma ta fahimci kallonta yake.

"Ya k'arin hak'uri kuma?, Allah yaji k'anta ya gafarta mata".

"Amin nagode sosai".

"Mai ya hanaki zuwa kwana biyu?".

Aynu ta gyara tsayuwarta sosai tana wasa da yatsun hannunta, ta bud'e baki ta bashi amsa.

"Banajin dad'ine".

"Shine dalilin da yasa kika k'i zuwa?".

"Ehh".

"Ko dai kinajin haushi nane akan k'onakin da nayi".

"A'a wallahi bani da lafiya sosai musamman yau yanzune ma nad'anji sauk'i".

"Ok".

Ya fad'a yana mai mik'o mata ledar dake ajiye gefansa Aynu ma ko lura da ita batayi ba.

Batayi magana ba haka kuma bata karb'a ba, shima kuma baice komai ba illa kafeta da idanuwa da yayi.

"Dole fa ki dinga karb'an kome na baki banason gaddama kamar yanda banaso inyi kyauta adawomin da ita".

Aynu tasa hannu ta karb'a tare da fad'in.

"Nagode sosai Allah k'ara girma da arzik'i yaji k'an hajiya".

Murmushi ne ya kufce masa wanda yasa fararen hak'oransa baiyana waje sosai yaji dad'in addu'ar Aynu agareshi, kamar yanda yake jin dad'in sautin muryarta akunnensa yana kuma jin dad'in kasan cewarta atare da shi ko da ba zaice da ita komai ba yanaso ya dinga kallon beauty face d'inta any time.

Aynu tsayuwar tafara isarta har k'afafunta na kakkarwa, amma ta gaza iya furta masa zata shiga gida.

"Kije gida sai da safe".

Taji muryarsa ta doki kunnenta, domin batayi tsammanin zai sallame ta ba a yanzu.

"To nagode sosai, a gaida su Hajiyarku".

Ta juya ta tafi domin tasan ba lallai ya amsa ba, shi kuwa bin bayanta da kallo yayi har ta shige cikin gidan nasu ya jima anan tsaye kafin ya nufi wajen da yayi parking motarsa ya shige ciki ya zauna yana tunanin da baisan kona mene ba haka kawai yaji zuciyarsa tab'aci duk da baya raba d'ayan biyun tafiyar Aynu ce taja masa hakan.

Aynu nashiga gida samun guri tayi kusa da Ummanta ta zauna tana fad'in.

"Ashe Yarima ne ba Ya Sayyadi ba".

"Yarima kuma Allah sa lafiya dai?".

"Lafiya k'alau Umma wai yazone yaji lafiya ko k'unarce take damuna banjeba kwana biyu".

"Allah sarki yaron na da kirki kuwa".

Aynu ita dai ajiyar zuciya tayi ranta tana fad'in.

"Dan bakisan waye shi bane kikace haka Umma".

A fili kuwa cewa tayi.

"Kin ga harda kaya yazomin da shi kona mene oho, bari in duba ingani".

Ta fad'a tana mai jawo ledar ta bud'e magunguna tana gani aciki sai kayan snack a ciki da juice gefe guda kuma taga wata guntuwar ta kadda ta bud'e aranta tana fad'in.

"Ko mene a ciki?".

"Kisha kowanne da k'aidarsa maganin ciwon kannaki ne".

Aynu tayi shiru tana sake karanta takaddar tare da tunanin inda yasan kanta na ciwao sai kace aljani?.

Ta fad'a aranta.

"Umma magani ne ashe tare dasu snack !".

"Allah sarki sai kisha maganin to, kyasamu sauk'in ciwon angode masa sosai Allah saka masa da alkhairi".

*YARIMA FUDHAL*

Na
FIRDAUSI S.A (QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

SADAUKARA:-Namesy Phirdauceey Jeebour.

Ina kike ne? Miemie Bashir (Queen) matso kusa wannan page d'in naki ne domin jin dad'inki kawai.

***

WASHE GARI

Cikin ikon Allah Aynu ta wayi gari lafiya k'alau kamar ba tayi ciwo ba.

"Umma gaskiya maganin nan yana da kyau kinga k'unar hannun sab'a takeyi har ta warke kenan?".

"To masha Allah haka ake so ai, Allah ya k'ara lafiya".

"Amin Ummata".

Sallamar Babanta ce ta katse su daga hiran da suke ya shigo ya nemi waje ya zauna, Aynu tayi masa sannu da zuwa tana mai mik'ewa domin kawo masa kunu da k'osansa na karyawa, taje ta d'auko ta ajiye a gabansa ya bud'e kwanun ya kurb'i kunun kafin ya dubi Aynu yana fad'in.

"Ya k'arfin jikin naki?".

"Naji sauk'i sosai Baba".

"Allah k'ara lafiya, haka akeson ji dama".

"Amin Baba".

"Yau ba zaki je gidan Sarkin ba ne?".

Ummanta ta fad'a tana mai duban gefan da Aynu ke zaune, Aynu ta d'an yatsina fuska kafin tace.

"Ban jin fita wallahi yau Umma ki bari har gobe naje".

Babanta yayi murmushi yana fad'in.

"Kiyi zamanki ki huta 'yar gidan Umma ki k'ara samun sauk'i sai kije".

"To Baba".

Baban nata ya sake dubanta karo na biyu fuskarsa fal murmushi yana yinsa da komai Aynu ta d'auko kama ce kawai ta d'auko ta Ummanta kamar antsaga kara.

"Ina Umar Faruq kuwa Aynu?".

"Ohh Baba Ya Sayyadi Umar wai? yana nan".

"Yaron na da kirki sosai kullum ya ganni har k'asa yake gaishe ni yauma fitar nan da nayi kinga naira d'ari biyar ya bani wai ayi cefane, nayi-nayi ya barta amma yak'i dole na karb'a".

Aynu tad'anyi murmushi tana wasa da yatsun hannunta take fad'in.

"Ai yana da kirki sosai akwai shi da kyauta ko a islamiyya".

"Bashi ne nake gaya maka yazo har gidan nan wancen satin ya gaishe ni ba".

Umma ta fad'a tana mai wasa da sandar hannunta.

"Ai inaji araina kamar akwai wani abu da yaron yake b'oyewa".

Cewar Baba kenan yana mai kallon fuskar Aynu cike da murmushi, itama murmushin take duk da kuwa fad'uwar gaban da taji ya tsanan ta a cikin zuciyarta, haka kawai taji hiran ta fara gundurarta tamik'e tsaye tana fad'in.

"Bari ingyara d'aki Umma".

Ta wuce ta barsunan suna ta tattaunawa, daga k'arshe sukabar hiran Ya Sayyadi Umar aka koma ta Yarima, Aynu duk tana jinsu tayi luf a d'aki domin duk cikin su babu wanda take ji hirarsa nayi mata dad'i, sun jima suna hirar kafin Baba yamik'e ya fita waje yabar Umma nan zaune.

Sai sannan Aynu ta fito domin sama musu abin da zasuci da rana kuma.

°°°

Yarima kuwa ranar wuni yayi yana zuba idon ganin Aynu amma har dare shiru, haka ya wuni kamar mara lafiya jama'a da dama suna d'auka alhinin rasuwa ne, amma anashi b'angaren abun da yakeji aransa game da Aynu shiyafi komai d'aga masa hankali da kuma mamaki.

Har ya yanke shawaran zuwa k'ara dubota domin ya zaci ko ciwon ne har yanzu ya hanata

zuwa, amma  sai dai ya share domin bayaso zak'ewarsa tayi yawa ta rai na shi.

Hakan na d'aya daga cikin abin da yasa Yarima k'in yin soyayya duk cikin shekarun da suka wuce, domin shi mutum ne mai son girma mai son a girmama shi baya son raini ko kad'an, a ganinsa da zaran ya furtawa budurwa yana sonta to raini zai iya shiga ciki shiyasa yake kau da kansa akan duk wata 'ya mace.

Amma kuma abin mamaki sai gashi rana guda ya kamu da son 'yar aikinsa kuma 'yar miskinai so mai tsanani kuwa, duk da yasan abune mawuyaci Aynu ta rainashi domin yarinyar nada tsoro sosai duk da k'arancin shekarunta ya fahimci yarinyar nada hankali da nutsuwa da sanin ya kamata, uwa uba kuma ya yaba da tarbiyarta, ba kamar sauran 'yan matan da suke son saba.

Murmushi yayi yana mai dafe kansa da yaji yana masa ciwo kad'an-kad'an, ya san hakan na faruwane sabida rashin ishash-shan bacci da kuma hayaniya domin shi baya son hayaniya ko kad'an shine dalilin da ya sama yake wuni a d'aki abinsa.

Maganin da ke aje gefan katifarsa  ya d'auka yana mai bud'e robar faron da ya aje gabansa yasha maganin ya koma ya kwanta nan da nan kuwa bacci yayi awon gaba dashi. (ASUBA TA GARI YARIMA).

***

Washe gari  tun da wuri kaman yanda ta saba tayi dukkan abin da ya kamata ace tayi kafin ta tafi, tayiwa iyayenta sallama ta kama hanya domin yau alhamis suna azumine bata tsaya bata lokacin neman abincin safe ba.

Ko da ta biyawa Zainab harta tafi  sai sannan taga lokaci ashe har takwas ta kusa setting agogonta ya goce kenan? ta gaida Babah Tasallah ta fito  a gurguje ta nufi gidan domin bata son yin late ko kad'an.

Bata tsaya ko ina ba sai cikin falon Yarima Fudhal tayi mamakin ganin falon fes dashi kamar jama'a basu zaunaba kai tsaye cikin d'akinsa ta nufa da sallamarta ta tura k'ofar d'akin tasa kai.

Yana kwance abinsa lullub'e  da bargo ya takure waje guda kaman mai jin sanyi hakan yasa ta kashe AC dake ta famanyi ita kad'ai a d'akin har lokacin baccinsa ya ke hankalinsa kwance bai ma san ta shigo ba, ta wuce toilet tahau aikinta har ta gama bai farkaba ta fito tashare d'akin ta goge amma bai ta shiba ta wuce falon ta sake sharewa ta goge, ta lek'a d'akin taga baccinsa yake har lokacin ta dawo falo ta zauna, ganin baccin nashi bamai k'arewa bane yasa ta fito daga part d'insu zuwa cikin gidan.

Taje tayiwa Jakadiyya gaisuwa tare da Uwar soro, sannan ta wuce wajen Fulani Sokoto tana shiga cikin falon ta tadda Fulani zaune tare da Yarima Jalil da Jalila suna ta hiransu ta durk'usa ta gaishe su tare da yi musu gaisuwa, shi kuwa Yarima Jalil tun da tashiga ya kafeta da idanuwa ko k'iftawa ba yayi, ciki-ciki Fulani ta amsa ki dan taga ba 'yar aikin wajenta bace? Oho.

Aynu ta mik'e ta fito daga b'angaren ta nufi wajen Fulani Bingel itama falon cike ta taddashi tayi musu gaisuwa suka amsa Fulani na fad'in.

"Kwana uku kenan ban ganki ba, ko k'unarce ta dameki?".

"A'a k'una ta warke ma banajin dad'i ne dai, sai yau naji dama-dama".

"Allah k'ara afuwa".

"Amin".

'Yan d'akin suka amsa banda Aunty Sa'ida da take ta faman banka mata harara ita dai Aynu kanta na k'asa batama san tanayi ba.

Aunty Sadiya ta dubi Fulani da murmushi tana fad'in.

"Wannan ce Aynul-hayat d'in?".

"Ehh ".

Fulani ta bata amsa, murmushi ta ya fad'ad'a a fuskarta tace.

"Kai amma taci sunan nata wallahi Hajiya".

Ita ma Fulani murmushi tayi tana fad'in.
"Sosai kuwa".

Aynu ta mik'e tana fad'in.

"Zan koma aiki".

Ta fice daga d'akin suka bita da kallo, Aunty Sa'ida taja tsaki.

"Kai wallahi Aunty Sadiya da kayan haushi ki ke !, meye wani abin kyau anan yarinya bak'auya yar talakawa".

"Ke ! banson jin wannan sha shancin anan kinji ko ina ruwanki to".

Aunty Sa'ida taja tsaki, tare da cizon leb'e.

Fulani tace "Allah ya shiryeki Sa'ida meye wani abu ajikin talaka da har zai zama abin k'i, ka da insake jin wannan maganar abakin ki".

Tafiya take kanta ak'asa tana wasa da yatsun hannunta sai ji tayi anjata gefe guda ta d'ago kai da sauri domin ganin waye?, ajiyar zuciya tayi tare fad'in.

"Zainab kin ban tsoro wallahi !".

Zainab tayi murmushi taja hannunta gefe guda suka zauna tana fad'in.

"Ke kinsan abin da yafaru kuwa?".

"A'a sai kin fad'a !".

Aynu ta bata amsa, Zainab ta cigaba da fad'in.

"Gaskiya Aynu Yarima na sonki sosai, bakiga yanda hankalinsa ya tashi ba kwana biyu da baki zoba".

Tsaki Aynu taja kad'an tare da fad'in.

"Amma ke kam kin fiye zato wallahi !, daga kinga ya shiga damuwa sai ki ce akai nane, mutuwafa akai musu kuma kinsan yanda suka shak'u da ita fa?".

Zainab abin ya bata dariya sosai ta kanne tana fad'in.

"Ba wani wallahi, shifa ya nemeni na bashi kwatancen gidanku, kuma wallahi bakiga yanda hankalinsa ya tashi ba sanda nace masa baki da lafiya, sai da yaji ciwon kai kike sannan naga hankalinsa ya d'an kwanta ko bai zo gidan naku ba ne?".

Aynu shiru tayi tana duban Zainab har sai da Zainab tad'an zungureta sannan ta dawo daga tuanin da take.

"Dama a wajenki yasan ciwon kai nake?".

"Ehh mana, yazo gidan naku kenan?".

"Ehh yazo da dare har da magun guna da kayan snack ya kawomin".

Zainab ta fad'ad'a murmushinta cike da sonjin bayani .

"To mai yace da ke?, fad'amin dan Allah yace yana sonki ko?, ki ke wani b'oyemin !".

"Sai kiyi kuma !, ke kam kina da matsala wallahi, ke nifa ko yace yana sona banjin zanso mutum irin sa".

"Sabida me?".

"Haka kawai".

"Aynu kenan ke kam baky fahimta wallahi".

"Ehh naji kinga mubar wannan maganar, kinsan kuwa Ya Sayyadi Umar sai faman zarya yake a gidanmu nifa har ya fara bani tsoro".

"Meye na tsoro kuma?, ta tsuniyar gizo dai bata wuce k'ok'i, amma nidai nafi sonki da Yarima !".

Zainab takai maganar tana dariya, Aynu ta mik'e tana turo baki wai ita adole fushi tayi ta wuce tabar Zainab nan zaune, ganin da Zainab tayi da gaske tafiya za tayi shine yasa ta mik'e itama ta bi bayanta da sauri tana kiran sunanta, amma Aynu ta toshe kunnuwanta tayi tafiyarta.

Ko da ta koma d'akin ya farka daga baccin yana zaune gefan katifarsa ya had'a kai da gwiwa, da sallama ta shiga d'akin ya d'ago da sauri yana dubanta, sai kuma ya kau da kai gefe guda kamar bayason ganinta a can k'asan zuciyarsa kuwa farin cikin ganinta ne fal ransa.

Har gabansa tazo ta durk'usa tana gaisha shi ya amsa can k'asan mak'oshi, Aynu ta d'an gyara zamanta sosai tana fad'in.

"Ya k'arin hak'uri kuma?, nagode sosa da kulawa, nazo na tadda kana bacci ne shine nak'i tashinka fatan banyi laifi ba?".

Bai ko kalle taba bare ya nuna mata ya san dashi take magana, bata damu ba ta cigaba da fad'in.

"Ko kana buk'atar wani abu ne?".

Shiru yayi na wani lokaci kafin yabud'e baki a hankali ya fara magana kamar wanda ake yiwa

dole.

"Kije falo".

Aynu tamik'e ta fito falo ta zauna tana jiran fitowarsa, ya shafe kusan mintuna talatin kafin ya fito falon sai faman tashin k'amshi yake cikin wani farin yadi mai shara-shara ana iya hango singlete d'insa ta ciki baisa hulaba illa taje sumarsa da yayi takwanta luf yaune karo na farko data ganshi cikin kayan hausawa tun dawowarsa.

Ya zauna gefan kusun yana duban Aynu, can ya kau da kansa ya mai dashi kan screeng d'in wayarsa da ke ringing.

SAIMA DARLING

Yagani bisa screeng d'in wayar tasa yasa hannu ya d'aga ahankali tare da sanyata a headfree.

Daga can b'an garen tanaji ya d'aga tahau fad'in.

"Haba Yarima !, ashe yanda na d'auke ka baka d'aukeniba!, mai yasa kake wulak'anta mai son kane?".

"Sabida banayin abu a rufe".

Ya bata amsa, cikin d'aga murya kad'an tace.

"Kamar ya kenan?".

"Kamar yanda ki kaji na fad'a".

"Ok amma mai yasa tun ran birthday d'inka baka nemeni ba, ni ina nan ina zaman jiran kiranka".

"Na manta ne".

Daga can b'arin Saima ajiyar zuciya tayi, domin ba kad'an takejin ciwon maganar da Yarima keyi mata ba duk da tanajin dad'in sautin muryarsa, ya katseta da fad'in.

"In kin gaji zan aje wayar?".

"A'a kawai banajin dad'in reply d'in kane".

"Time d'in breakfast d'ina yayi zaki iya kira anjima?".

Ya kashe wayar ya ajiye gefe, duk maganar da yake idonsa na kan Aynu yana karantar yanayinra, ita kuwa kanta na k'asa tana wasa da wani d'an k'aramin zobe kod'ad'd'e dake hannunta.

Duk tanajin maganganun da suke amsar k'arshe daya bayar da kuma kashe wayar shi yafi komai bata mamaki da Yarima, amma data tuna waye shi?, sai mamakinta ya kau domin tasan zaiyi fiye da abin da yafi haka indai Yarima ne, b'an garan jiji da kai, girman kai da d'agawa ga shegen miskilanci da wulak'anci tun da take bata tab'a ganin mutum irin yarima ba abin nasa yayi yawa.

Ya katseta da fad'in.

"Yau wannan banjin zata zo?, inaga zan koreta aiki ne kawai !, jeki kawomin breakfast ".

*YARIMA FUDHAL*

Na
FIRSAUSI S.A(QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITES ASSOCIATION®

SADAUKARWA:-Namesy Phirdauceey Jeebour.

Wannan page d'in naki ne *Ashnurpyar* Nagartacciya Allah yabar zumunci amin.

14

BAYAN KWANA BIYAR

Zaune take can gefe daga inda yake yanata aikin danne dannan wayarsa, tafiya take sonyi

amma ya hanata ko da fita cikin gidan ne.

"Zo nan Aynu".

Taji muryarsa yana kiranta tamik'e ta k'arasa wajen da yake zaune nesa da shi kad'an.

"Matso mana".

Ta d'an kuma matsawa kad'an, murmushi yayi yaga alamun bata da niyan zuwa kusa dashi mik'ewa yayi yazo daf da ita ya mik'a mata wayar hannunsa yana fad'in.

"Kalli ki gani".

Aynu takai dubanta bisa screeng d'in wayarsa wata farar mace ta gani kyakykyawa ajin farko tana sanye cikin alkyabba pink data k'ara bayyanar da kyanta.

"Gimbiya Safiyya kenan".

Ya fad'a yana mai duban fuskarta.

Murmushi tayi Aynu tare da furta.

"Amma ta had'u sosai tayi kyau wallahi".

Yarima Fudhal ya kafeta da idanuwa yana dubanta kafin yad'anyi murmushi kad'an.

"Ita ce ake son had'ani aure da ita !, nan da 3days zatazo gidan nan, amma ni gaskiya bana sonta !".

"To amma kuma kake ajiye hotonta?".

"Meye ra'ayinki akanta?".

Ya tambayeta ba tare daya bata amsar tambayar ta ba, Aynu ta dube shi da murmushi saman fuskarta.

"Ta dace da kai sosai kuwa".

"Uhmmm haka ki kace?".

"Ehh mana".

"Wannan zab'in iyayena ne, amma ni bata daga cikin zab'ina".

"Sai kabi zab'in iyayen naka ai, domin nasan basuyi maka zab'in tumun dare ba".

Tsaki Yarima Fudhal yaja yana mai duban Aynu cike da takaicin amsar da take bashi, dubanta ya sakeyi a karo na biyu yana fad'in.

"Bawai na nuna miki bane domin ki bani shawara akan zab'in da zanbi, na nuna miki ne domin.......".

Sai kuma yayi shiru maganar ta tsaya a mak'okwaronsa, dai-dai da shi gowar Saima ya d'auke dubansa daga kan Aynu ya karb'i wayarsa tare da fad'in.

"Tashi kije".

Aynu ta mik'e da sauri ta fice dama ta takura da al'amarin Yarima sosai, Saima ta bi bayanta da kallon tuhuma, har sai da Aynu ta fice sannan ta dawo da kallonta kan Yarima tana fad'in

"Kana buk'atar wani abu ne?".

"A'a jeki kawai".

Ya bata amsa batare daya dubeta ba.

DARE
8:20PM

Da dare misalin k'arfe takwas da mintuna ashirin Aynu na zaune bisa tabarmar da tayi sallah gama cin abincinta kenan akai sallama tare da fad'in.

"Wai Aynu tazo inji Yarima".

Dammm gabanta ya buga har sai da tad'an lumshe ido tare da karanto addu'a cikin ranta afili kuwa ta furta.

"Yarima kuma !, me zaiyimin da daren nan?".

"A'a tashi kiji tunda kiga mutum ya tako har inda kike yazo yana da abun da yakawo shi mai muhimmanci ne musamman manyan mutane ai sai da babban dalili suke zuwa wajen mutum".

Umma ta fad'a tana mai duban inda 'yar tata take zaune duk da ba gani take ba.

Aynu tayi ajiyar zuciya gami da tashi daga cin abincin dama ta gama ta wanko hannu ta zari hijabi ta fice.

Yana tsaye jikin katangar gidan nasu hannunsa rik'e da wayarsa yana dannawa d'aya hannun kuma na cikin aljihun wandon jeans d'insa, aranta ta furta.

"Ko ina dai ba'a gajiya da sana'ar".

Da sallama ta k'arasa wajensa Yarima ya amsa tare da fad'a d'a murmushinsa yana duban ta, Aynu tayi saurin yin k'asa da kanta sabida irin kallon da Yarima Fudhal yake ji fanta dashi idanuwanta bazasu iya d'auka ba.

Shiru ne ya ziyarci wajen kafin Yarima yayi k'arfin halin katse shirun da fad'in.

"Ke na keson aura Aynu !, zuciyata tafi aminta dake akan wacce iyayena suka zab'amin amma...".

Sai kuma yayi shiru yana mai haska fuskarta da hasken wayarsa domin ganin yanayin ta, Aynu dai kanta yana k'asa amma zuciyarta na bugun uku-uku wanda ta rasa dalilin faruwar haka.

"Ko bakya so na?".

Taji saukar muryarsa akaro na biyu yana tambayarta, maimakon ta bashi amsa kawai juya wa tayi tabar wajen ta shige gida ta barshi nan tsaye.

Yarima yabi bayanta da kallo ba tare da yayi yunk'urin da katar da ita ba yanaji zuciyarsa nayi masa zafi, tare da jin haushin abin da tayi masa.

***

Kwance yake bisa lallausar katifarsa sai faman juyi yake yana son yin bacci amma hakan ya gagare shi, tunanin abin da Aynu tayi masa d'azu shine yake damunsa, amma babban abin da yafi damunsa bai wuce jin tsoron kada Aynu tace bata son saba.

Lokacin ya jawo wayarsa ya duba agogo k'arfe biyu da kusan rabi, ya d'an ja tsaki tare da cigaba da danna wayar da alamu akwai abin da yake nema.

Can ya danna wata number tare da karawa akunnensa, sai da wayar ta kusa tsinkewa sannan aka d'aga tsaki Yarima yaja tare da fad'in.

"Kai fa d'an rainin wayo ne Anwar !, mai kake nufi ?, da ba zakayi picking bane?".

Cikin muryar bacci Anwar ya amsa da fad'in.

"Kai fa prince kafi kowa matsala wallahi ban da ni wa zaka kira da tsakad daren nan ya d'aga".

Yarima Fudhal yaja dogon tsaki kamar ya yanke wayar sai kuma ya fasa yana fad'in.

"Kaga malam maganace mai muhimmanci ka tashi daga baccin".

"Akan me?, fad'i maganarka kawai ina jinka".

"Mene ma'anar idan ka furtawa mace kan sonta tayi tafiyarta batare data baka amsa ba?".

Daga can b'angaren Anwar dariyace ta kwace masa har da rik'e ciki, ba k'aramin k'ok'ari yayi ba wajen saita kansa domin tambayar tazo masa a bazata da kuka mamakin wanda yayi tambayar, bai kai da baiwa Yarima amsa ba yaji ya katse wayar yasan dama za'ayi hakan, kira ya sakeyi harta katse Yarika yak'i dagawa sai da ya kira sau uku sannan ya d'aga batare da yayi magana ba.

Anwar cikin dariya ciki-ciki yahau fad'in.

"Am sorry Prince kawai naji mamakin tambayar da kayi min ne wallahi, da gaske soyayya kake son sanar dani ka fara ko kuwa me?".

"A'a kawai inason jin amsar ne".

Anwar yayi murmushi tare da fad'in.

"To kabari har gobe mayi magana mana".

"A'a yanzu nake so shiyasama na kiraka ai, da naso har gobe ai sai goben zan neme ka".

"Hakane, amma gaskiya a gani na duk macen da kace kana so tayi tafiyarta ta barka nan batare da amsa ba to d'ayan biyu ne ko kunyar baka amsa take ji ko kuma bata son ka...".

Kafin ya kai da k'arasa maganar Yarima Fudhal ya katse wayar ya wullata can k'arshen

katifarsa tare da yin tsaki, sai kuma yamik'e ya zauna maganar Anwar nayi masa yawo akai.

"Aynu kunyata take ji, ko kuma so nane batayi ?".

Kai ya girgiza yayin da zuciyarsa ta tsinke tsoro ya ziyarce shi, sai ya samu kansa da fad'in.

"Allah yasa kunyace ta hana ta bani reply !".

Hhhhhhh to fa !, su Yarima Fudhal anshiga taskun soyayya, to amma aganinku Aynu zata so Yarima Fudhal kuwa?.

Nabar muku wannan amsar Reader.

Kuyu hkr da wannan page d'in babu yawa, nagode sosai masoyana kuna raina koyaushe.

*YARIMA FUDHAL*

Na
FIRDAUSI S.A (QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCIATIONS®

15

8:00am

Zaune Anwar yake gefen kusun yana duban Yarima Fudhal cike da tsokana yake fad'in.

"Amma dai kowa ya ganka yaga wanda yajik'e da mayen so, amma kace min kai ba soyayya kake ba?".

Yarima dake kwance gefe ya dora hannunsa na dama bisa fuskarsa kamar bacci ko motsi baiyi ba, bare ya kula da maganar da Anwar yake masa.

Aynu ce ta fito daga cikin bedroom hannunta rik'e da moopa ta d'an risina tana fad'in.

"Na gama zan gyara nan".

Yarima ya mik'e ba tare daya dubeta ba ya wuce cikin d'akin yana fad'in.

"Sai ka ta so ko".

Anwar yabi Yarima da kallo kafin ya dawo da dubansa kan Aynu yana fad'in.

"Mene sunanki".

"AYNU".

Ta bashi amsa kai ya gyad'a tare dayin murmushi yana fad'in.

"Nice name, a wacce unguwa kike?".

Yarima ne ya banko labulan d'akin ya fito cike da b'acin rai, kallon daya watsawa Aynu shine yasa ta shan jinin jikinta tayi k'asa da kai ba tare data baiwa Anwar amsa ba.

Anwar ya sanya dariya mai sauti tare da mik'ewa yabi bayan Yarima cikin d'akin yana fad'in.

"Abin da nayi zato ya tabbata Prince, wai me yasa kake b'oyemin ne?, tun da nazo nake karantar yanayin ka akan yarinyar nan".

"Sabida kamai da zancena gist mana !, kasan ni bana wasa a cikin al'amura na".

"Ehh to zancen wasa ya wuce, amma ka da dai kacemin wannan Yarinyar kake so?, domin naga kishinta k'arar bisa fuskarka".

"Ehh ita nake so !, wani abun ne?".

"A'a amma fa yarinyar tayi wallahi, duk da dai kanta ba'awaye yake ba".

"Ehh naji koma dai mene, amma kasan wani abu ?".

"Menene fad'amin inajinka".

Saima ce ta shigo da Sallama tare da fad'in.

"Breakfast d'inka yayi ready".

"Ok ina zuwa".

Ta juya tafice, Anwar ya dubi Yarima tare da fad'in.

"Ina jinka".

"So nake kajawo hankalin wata yarinya, ma'ana kayi soyayya da ita".

"Ban fahimce kaba?".

"Ok abin da nake nufi, inaso kasa wata yarinya ta soka, ni so nake hankalinta ya tashi daga kaina ya koma kanka, Yarinyar tana so nane hakan na neman jawomin matsala ".

"Wacce matsala kenan?, amma kuma wacce yarinya ce?".

Yarima Fudhal yayi murmushi tare da kau da kansa gefe.

"SAIMA 'yar gidan Alhaji Buba, ita nake so kayi soyayya da ita, so nake kamar yanda ta furta tana sona inaso ta furta da bakinta bata so na !".

"Amma mai yasa ka yanke wannan hukuncin, Yarinya kamar Saima mai tsada tace tana sonka amma kace a'a?".

"Yes bana ra'ayin 'yan mata irin tane, jiya da Yamma Mai martaba ya kira ni ya sanarmin Baban ta Alhaji Buba da kansa yazo nan wajen Mai Martaba akan yana so ya had'a zuri'a da mu, wato dai yana so ya auramin 'yarsa, bayan kuma anmin zab'in Safiyya, amma kasan amsar da Mai Martaba ya bawa mahaifinta?".

"A'a sa ka fad'a".

"Cewa yayi ai namiji mijin mata hud'u ne, babu komai sai a had'amin mata biyu in aura aini Yarima ne kuma magajin gobe, wannan dalilin yasa na kasa daure zuciyata har sai da naje na furtawa Aynu ina sonta, sai dai bata bani amsa ba har yanzu, hakan namin ciwo sosai jiya ko bacci kasa yi nayi".

"To ka had'asu duka ukun mana".

"Bana ra'ayin hakan, kawai ka yimin abin da nagaya maka".

"To amma idan Saima ta dawo kaina, ita Safiyyan ya zakayi da ita?".

"Banyi tunani akan taba, sai na gama da wannan".

"Amma kuma idan ta furta bata sonka ni take so, rabuwa zanyi da ita kome?, dan nima gaskiya ba lallai ya kasance in so ta ba".

"Wannan ya rage naka karabu da ita ko ka aure ta, inkaso zaka iya son ta bai dame ni ba, amma nidai buk'ata ta tace bata so na".

Anwar ajiyar zuciya yasaki mai k'arfi yana mai kallon Yarima cike da tunanin al'amarinsa, shikam yasan tun yana yaro tare suka taso da Yarima amma har yanzu ya gaza fahimtar halayyar Yarima, shi wani irin murd'ad'd'an mutum ne, sai ka kasa gane inda yasanya gaba.

"Kayi shiru ko kana buk'atar lokaci ne?".

"A'a zanyi yanda kace, amma kana ganin ita wannan Yarinyar zata so ka?".

"Ban dai sani ba?, amma shirun ta na bani tsoro".

Anwar ya girgiza kai da murmushi saman fuskarsa yana fad'in.

"Babu komai Allah ya shige mana gaba".

"Amin".

Suka mik'e suka fito zuwa falon, komai ready kai tsaye wajen abinci suka nufa sukayi breakfast, suna ci suna tattaunawa domin falon babu kowa sai su kad'ai.

Zaune take bisa da kalin dake farfajiyar Shamaki babu kowa wajen sai ita, tayi zurfi cikin tunani domin ba tasan ma Yarima Fudhal na tsaye bisa kanta ba, ya kira sunanta yafi sau a k'irga amma bata amsa ba.

Hakan ya sashi zama kusa da ita tare da sanya hannu yad'an girgiza kafad'arta, firgigit ta farka tare da mik'ewa da sauri tana duban Yarima, Yarima Fudhal murmushi yayi mata yace.

"Zauna mana".

Aynu ta koma ta zauna amma duk ata kure take jinta.

"Me kike tunani?".

Ya tambayeta Aynu tayi k'asa da kanta tana duban tafin hannunta.

"Babu komai".

Ta bashi amsa, girgiza kai yayi alamun bai yadda ba.

"Bana son k'arya kodai tunani na kike?".

"A'a !".

Ta kuma bashi amsa, Yarima yayi ajiyar zuciya tare da kafeta da idanuwa har lokacin murmushin fuskarsa bai d'aukeba.

"Aynul-hayat !".

Ya kira sunanta da wata irin murya wadda tasanya tsigar jikin Aynu tashi, har tad'an rintse ido kad'an, hannunsa ya sanya bisa tafin hannunta yarik'e, ya cigaba da fad'in.

"Ki fad'amin mana, ko kunyata kike ji?".

Aynu ta girgiza kai, tana mai k'ok'arin janye hannunta amma yarik'e kam.

"Bafa zan cika ki ba, har sai kin bani amsar tambayar da nake miki".

Aynu dai tayi shiru sai motsa bakinta take amma kuma maganar tak'i fitowa, su Zainab ta hango suna nufo wajen kusan su biyar da dukkan alamu sungama aikin sune sunzo su huta domim duk a wajen suke hutawa.

Ta kafe su da idanuwa tsoro ya k'ara kama ta, jikinta har wani rawa yake Yarima ya juya yana duban inda take kallo murmushi yayi yana fad'in.

"Indai baki bani amsa ba sai dai su taddamu ahaka, danni kinsan babu ruwana !".

Aynu tahau girgiza kai kawai, bai zata ba sai jin saukar ruwa yayi akan hannunsa ya kalleta da sauri yana mai sanya hannu ya d'ago fusakarta, afili ya furta.

"Kuka kuma?, Yi hak'uri share hawayen kada suzo su gani wasa nake maki fa n".

Ya cika mata hannun yana murmushi, ya mik'e tsaye ya zuba hannuwansa cikin aljihun wandonsa yana kallon yanda taketa k'ok'arin share hawayen amma wasu na zubowa, sosai abin yake burgeshi sai yaji dama su dauwama haka yana kallonta.

K'arasowar su Zainab ce tasan yashi barin wajen yana fad'in.

"Zaki zo kisame ni ne".

Zainab tak'arasa wajen Aynu tana fad'in.

"Lafiya Aynu?".

Harara ta sakar mata tare da juyar da kai gefe, sosai take jin zafin rik'e hannunta da Yarima yayi.

"Wai ke mene yake damunki ne?".

"Babu komai".

Ta bawa Zainab amsa, Zainab tace.

"A'a wallahi nasan da wani abun, yanzufa naga Yarima yabar wajen nan, wannan ruwan hawayen kuma fa?".

Tsaki Aynu taja tana fad'in.

"Ke kam kin shiga uku da tambaya".

"Ehhh naji, ai ni dake iya wuya muna tare".

Aynu tayi murmushi ta juyo ta kalli Zainab tana mai bata labarin abin da ya faru, ajiyar zuciya Zainab tayi tare da fad'in.

"To ke mene ra'ayinki akan Yarima Fudhal, son shi ne ba kyayi ?".

*YARIMA FUDHAL*

Na
FIRDAUSI S.A (QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

16

Hello makaranta

Hope na sameku lafiya?

Ya komai, ya kowa?

Kuyi hak'uri dan Allah  zaku dinga ganin post d'ina  ko yaushe insha Allah amma ban da ranar Friday sabida wani dalili.

Nagode sosai da sosai.

"wai ni ya zanyi ne Zainab !, Yarima ya matsamin akan lallai sai yaji ina sonsa ko bana sonsa?".

"To wai ke mene ra'ayinki akansa ne !, nima kaina na kasa gane maki ko son sane bakyayi?".

Aynu ta girgiza kai cike da jimami.

"Nima har yanzu nakasa tan-tancewa ina sonsa ko bana sonsa, abin da kawai nasani ina jin tsoro ne sosai?".

"Tsoson me kuma?".

"Yarima yafi k'arfina Zainab !, mai Yarima zaiyi da ni?, 'yar miskinai kuma baiwarsa niba 'yar kowa bace Zainab !, Yarima yana tak'ama da kud'i da mulki mafiya yawan al'ummarmu na yanzu musamman masu kud'i da masu mulki sunfi son AURE KWARYA TABI KWARYA, ina jin tsoron abin da zaije ya dawo ne".

Zainab dogon tsaki taja cike da takaicin maganganun da Aynu ta fad'a.

"Toke mene zai dame ki, bafa ke kika ce kina son saba shine yace yana sonki, ni dai shawarata agare ki kada ki bari damarki ta wuce ki, kiyi 'kok'arin yin amfani da damarki, ki sanarwa Yarima kina sonsa, sauran lamarin ki barwa Allah komai kiyi ta addu'a da yardar Allah komai zaizo cikin sauk'i".

Zainab ta nisa tana mai kallon Aynu dake share kwallar dake k'ok'arin zubo mata bisa fuskarta ta cigaba da fad'in.

"Aynu kina son Yarima !, ki yarda da hakan kuma, kawai tsoro da fargaba ne sukafi tasiri a zuciyarki shiyasa kika kasa fahimtar cewa kina son sa !".

Aynu murmushi tayi tana mai duban Zainab, Zainab kai ta gyad'a mata itama fuskarta d'auke da murmushi ta dafa kafad'ar Aynu tana fad'in.

"Zan tayaki da addu'a sosai, amma kada ki bari Yarima ya sub'uce miki, domin ke kikafi dacewa da Yarima Fudhal".

Sosai Aynu taji dad'in shawaran Zainab agareta, rik'o hannun Zainab tayi tana fad'in.

"Nagode ! Nagode !! Nagode !!! Zainab Allah yabar mutare".

"Amin".

Shela aka hauyi a cikin gidan na cewar tawagar Gimbiya Safiya ta sauka aje a tarbota.

Da sauri su Aynu suka mik'e suka nufi waje.

Jerin motoci goma ne sukai parking a k'ofar gidan, wani dogari ya taka da gudu yaje ya bud'e k'ofar motar, cike da tak'ama da izza Gimbiya Safiyya ta sako k'afa ta fito, mace doguwa fara kyakykyawa ajin farko tana sanye da farar alkyabba wacce ta rufe dukkan jikinta, inbanda hannunta da k'afarta sune kawai a waje, takalimin k'afarta mai gashine shima fari iya had'uwa ta had'u k'arshe.

Aynu sai taga tafi kyau afili ma fiye da a hoto data ganta, take taji wani abu ya ziyarci zuciyarta taji ta raina kanta sosai domin babu abin da zata nunawa Gimbiya Safiyya indai kyaune zai sa aso mutum to tabbas da Yarima baice yana sonta ba, domin Gimbiya Safiyya kyakykyawace ta k'arshe.

Tana fitowa aka hau yi mata ruwan fure tare da tawagarta bayi mata biyar ke biye da ita, kai tsaye wajen Mai Martaba dake tsaye ta nufa tayi gaisuwa, sannan muka rufa mata baya zuwa cikin gidan.

Kai tsaye muka nufi b'angaren Fulani Sokoto da ita, tana tafe anayi mata ruwan fure tare da kirari har zuwa cikin falon Fulani Sokoto.

Yarima Jalil da Jalila duk suna zaune falon tare d ma'aikatan Fulani, muna shiga Fulani ta fito daga cikin d'akinta tana yiwa Gimbiya Safiyya sannu da zuwa, rungumeta Gimbiya Safiyya tayi tare da yinn kiss d'in kuncinta tana fad'in.

" I Miss u my Mom !".

Ta juya kan Yarima Jalil shima abin da tayiwa Fulani haka tayi masa, sannan ta juya kan Jalila itama haka tayi mata, mudai sakar baki mukayi muna kallon ikon Allah dan wannan ya zame mana saban al'amari aganinmu idan zata rungumi Fulani da Jalila ai bai kamata ta rungumi Yarima Jalil ba?.

Neman guri tayi ta zauna tana fad'in.

"Ku bamu waje ko?".

Duk kanmu muka mik'e muka fito zuwa waje, kowa ya kama gabansa, ni da Zainab neman

waje mukayi muka zauna muna hira, bamu jima ba akayi kiran Zainab a b'angaren Fulani Bingel, ta barni nan zaune gashi ni inba Zainab ba bana shiga harkar kowa nan nayi ta zaune har zaman ya isheni na mik'e nima na nufi b'angaren Fulani Bingel tunanina inje intaya Zainab aikin da take, ko ba komai yafi zaman da nake ni kad'ai.

Ina tafe ina 'yan wak'e-wak'ena sai ji nayi anjawo hannuna cike da tsoro na bud'e baki zanyi ihu yasa hannunsa ya rufan bakin yana fad'in.

"Sarkin tsoro !".

Fuskarsa d'auke da murmushi, ajiyar zuciya na saki tare dayin k'asa da kaina, Yarima Fudhal ya tsareta da idanuwa yana fad'in.

"Yau dai kinga kishiyarki ko?".

Aynu batasan sanda ta jefeshi da wat uwar harara ba, Yarima yayi murmushi yana mai cigaba da fad'in.

"Mene na kishi a kaina kuma?, bayan bakya sona?".

Sai lokacin Aynu ta lura da abin da tayi kunya ta rufeta sosai, murmushi yayi mai sauti.

"To yau dai sai kin fad'amin kina sona ko bakya so na?".

Aynu tayi shiru tana wasa da yatsun hannunta.

"Baki ce komai ba?, ko bakya so na?".

Ta girgiza kai alamun a'a.

"To kina so na?".

Ta gyad'a kai alamun ehhh, tana mai rufe fuskarta da tafin hannunta, murmushin dake kan fuskar Yarima ya sake fad'ad'a, sosai yake jin wani sanyin dad'i na ratsa dukkan sassan jikinsa, har yanajin kamar ya rungumeta tsabar farin ciki.

"AYNU...!".

Ya kira sunanta da wata irin murya, bata d'ago kanta ba illa amsawa da tayi kawai tana jiran taji mai zai ce.

BAN HAK'URI

Ku k'ara hak'uri dani dai, naso nayi muku typng mai yawa sakamakon jiya banyi muku post ba, sai dai Allah bai yarjemin ba wlh bbu chaji awayana yanzu kuma kunata jirana shiyasa na k'ok'arta nayi muku wannan zuwa anjima insha Allahu indai na samu chaji zaku sake jina nagode sosai da kulawa.

*YARIMA FUDHAL*

Na
FIRDAUSI S.A(QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

SADAUKARWA:-Namesy Phirdauceey Jeebour.

17

Ya cigaba da fad'in.

"Tabbas naji dad'i sosai da jin amsar data fito daga bakin ki, yau rana ce ta musamman agare ni da bazan tab'a mancewa da ita".

Yayi shiru yana mai cigaba da kallonta, har lokacin Aynu bata iya d'ago kanta ba, sanya hannu yayi ya d'ago kan nata yana mai duban fuskarta cike da so da k'auna, Aynu ta rintse ido domin bata iya juran kallonsa, sakin fuskarta yayi ya ce.

"Hak'ik'a kin bani farin ciki wanda nake fatan d'orewarsa har aba da !".

"Bari inje Mai Martaba na kira na, zan zo yau da dare gidan ku !".

Kai kawai Aynu ta gyad'a masa ya tsaya yana kallonta kamar kada ya tafi, da k'yar dai ya juya yabar wajen.

Aynu tabi bayansa da kallo tafiyarsa kanta abar burgewa domim Yarima idan yana tafiya da gaba d'ayan jikinsa yake tafiya, gyaran muryar da ta jine ya sanyata juyawa da sauri domim

ganin waye?.

Yarima Jalil ne tsaye yana binta da kallo ya nad'e hannunsa ak'irjinsa fuskarsa babu yabo babu fallasa.

Aynu tad'an risina ta gaishe shi, ya amsa tare da fad'in.

"Ya had'u ko Yayan nawa?".

Yayi maganar yana mai d'aga mata gira, murmushi Aynu tayi ba tare data iya cewa dashi komai ba.

"Anyi masa mata to !, dama kin barshi kindawo wajena Beauty".

Aynu dai batace komai ba, ya d'an matso kad'an zuwa wajenta adai-dai kunnenta ya rad'a mata.

"Dani kika fi dacewa, nine zan baki dukkan k'auna !, duk naji abin da yake fad'a miki ki watsar da batunsa, ki fuskanci batuna domin dai ga matar da zai aura nan, bayan ita kuma akwai wacce akayi magana su biyu zai aura ya angwance !".

Ya k'arashe maganar cikin dariya ciki-ciki.

Aynu da sauri ta dubeshi da kallon tuhuma tana son tabbatar da maganarsa, gira ya d'aga mata tare da wani guntun murmushi a saman fuskarsa.

"Ko baki yarda dani bani?".

"A'a na yarda mana, amma ni nace maka akwai wani abu atsakanin mune ?".

"Baki fad'aba amma idanuwanku sun shaida hakan, kiyi tunani sosai akan Fudhal dani Jalil waye zaifi dacewa da rayuwarki ?, indai har zaki yarda da soyayyata zanbar dukkan wani abu mai muni da nake aikatawa kuma zan rayu dake ke d'aya babu wata ".

Yayi shiru yana karantar yanayinta kafin yad'an cije leb'e ya cigaba da magana.

"Shin aganinki wanda zai auri mace kamar Safiyya zaiyi tunanin kuma auren wata 'ya mace ne, ki tuna bayan ita akwai wata, itama kuma ba baya ba wajen kyau da kud'i da komai n".

"Zan barki kiyi tunani akan hakan duk shawaran da kika yanke zaki iya fad'amin".

Ya juya yabar Aynu da jijiyoyin jikinta baki d'aya sun tsinke tsoro ya ziyarci zuciyarta sosai, take taji zuciyarta nayi mata zafi wajen Zainab d'in da bataje ba kenan tayi tafiyarya gida aganinta

zatafi samun nutusuwa da kwanciyar hankali idan ta koma gidan.

Sai dai ba anan gizo yake sak'arba ko da ta koma gida kasa aikata komai tayi inbanda aikin tunani babu abin da take yi, aranta tanaji Yarima Fudhal ya cuceta, duk da k'asan zuciyarta ya kasa gasgata hakan.

Ummanta tayi tambayar duniya ko akwai abin da yake damunta amma Aynu tace babu komai, daga k'arshe da taga Umman ta damu sai tace kanta ne yake ciwo tasha magani tayi kwanciyarta.

***

Haka Aynu ta kwana bacci sai dai b'arawo, amma a cikin daren sai da tasamawa kanta mafita, duk da wani b'angaren na zuciyarta ya kasa yarda da hukuncin data yankewa kanta.

Washe gari kuwa ko da takoma aiki abin da ya kaita kawai tayi, kuma daman ta tarad su Yarima sun fita tun asuba hakan ba k'aramin dad'i yayi mata ba, amma tana gama aikin da zatayi neman guri tayi falo ta zauna tare da fuskantar wani k'aton frame na hoton Yarima Fudhal da aka d'aukeshi gaba d'ayansa yana sanye da farar coat da wando fari hatta takalmi da agogon hannunsa fari ne, sosa Aynu takeson hoton tun ba yanzuba haka kawai takanji dad'in ta zauna tana kallon hoton domin kamar kace Yarima ya amsa hoton ya d'auku sosai.

11:30am.

Basu dawo ba sai k'arfe sha d'aya da mintuna ya turo k'ofar d'akin ya shigo cike da sallama, Aynu bama tasan ya shigo ba domin tayi zurfi cikin tunani, wani dad'i yaji alokacin da idonsa yakai inda Aynu take kallo murmushi yad'anyi tare da k'arasawa wajen da take zaune ya dafa kafad'arta.

A firgice ta d'ago kai sai kuma ta saki ajiyar zuciya ganin Yarima.

Turo k'ofar da akaine ya sasu juyawa baki d'ayansu, Gimbiya Safiyya ce ta shigo cikin takun k'asaitar nata tabisu da wani kallo wanda Aynu takasa tan-tance kona menene?.

"Wace wannan?".

Ta jefawa Yarima tambaya, Yarima Fudhal ya nemi guri ya zauna batare daya bata amsaba, sai ma fad'i daya hauyi.

'kawomin breakfast Aynu".

"A'a ta barshi ai tafe muke da shi, Larai...!".

Gimbiya Safiyya ta kira wata mai aiki dake bakin k'ofa, Larai ta shigo hannunta d'auke da tire ta ajiye gaban Gimbiya Safiyya data nemi waje kusa da Yarima Fudhal ta zauna.

Larai ta juya ta fice, Gimbiya Safiyya ta d'auki Apple ta kai masa baki Yarima ya kau da kansa gefe yana fad'in.

"Tea nake buk'ata Aynu zoki zuba min".

Gimbiya Safiyya ta kaiwa Aynu wani kallon wulak'anci tana fad'in.

"Au dama baki fita ba, fita ki bamu waje !".

"Babu inda zata domin kafin zuwanki ita ke ci da ni".

"To yanzu tun da nazo ba sai ta huta ba?".

Takai maganar tana hararar Aynu, Aynu tayi k'asa da kanta ba tare da tace komai ba.

"Zo ki serving d'ina".

Ya sakewa Aynu magana, Aynu tamik'e tazo tayi serving komai ta koma gefe ta zauna.

Gimbiya Safiyya tad'auki kofin tea d'in takai masa bakin wai zata ci da shi ya d'auke kansa tare da fad'in.

"Na gaya miki bana buk'ata".

"Amma kasan aure zamuyi?, mene danna ci da kai tun yanzu ai treaning nake yi".

Yarima tsaki yaja yana mai kau da kansa gefe cike da takaici, Gimbiya Safiyya ta sake duban Aynu cike da masifa tana fad'in.

"Wai ke wacce irin macace akace ki fita ko?".

Aynu tamik'e ta fice aranta tana jin zafin wulak'ancin da Gimbiya ke yi mata, amma ak'asan zuciyarta sai taji babu komai domin ita 'yar aiki ce kuma baiwa ita kuwa 'ya ce ga Sarki guda.

Yarima Fudhal bai yi magana ba har Aynu ta fice tana goge kwallar dake gefan idonta, ransa

idan yayi dubu yab'aci take yamik'e ya fito shima yabar mata d'akin.

Ran Gimbiya yab'aci sosai ta fito itama ta nufi b'angaren Fulani Sokoto tana kuka wai Yarima Fudhal yafifita Baiwa akanta ?.

Rarrashinta Fulani tayi tare da fad'in.

"Ki kwantar da hankalinki zan san abinyi dani yake zancen !".

Jalila dake zaune gefe tsaki taja tace.

"Kema dai Aunty Safiyya kin manta waye Fudhal ne?, tun da kin taka kinje wajensa ai kuwa sai abin da kika gani !, shi Allah na tuba baka shiga harkarsa ba ma ya wulak'anta ka bare kuma ka shiga....!".

"Ke gidanku nace !, rufemin baki dan taje wajensa meye a ciki?, ina nan da kwanaki kad'an mijin tane?".

Cewar Fulani kenan cike da fad'a, Jalila tsaki taja tana k'uk'uni.

"Nifa Momy ba haka nake nufi ba, Allah ya baku hak'uri".

Ta fad'a tana mai mik'ewa ta fice daga cikin d'akin.

Yarima Fudhal na fitowa neman Aynu yahauyi lungu-lungu amma bai ganta ba, sai da ya gaji da nema ya tsaya jikin windown wani d'aki sai yadinga jiyo shash-shek'ar kuka bayan d'akin, zaga yawa yayi domin ganin waye yake kukan?, Aynu ya gani ta had'a kai da gwiwa a hankali ya taka zuwa wajen tare da kiran sunanta yana mai kama kafad'unta ya d'ago ta, fuskarnan shab'e-shab'e da hawaye hannu yasa yahau share mata yana fad'in.

"Yi hak'uri kinji !, mene abin kuka kuma?".

Aynu ta janye jikinta daga nasa tana yi masa wani mugun kallo ta juya masa baya, k'ara juyo da ita yayi ta kuma juyawa masa baya ganin da yayi tana k'ok'arin barin wajen ne yasa shi shan gabanta yana fad'in.

"Wai lafiya kuwa?".

Tsaki tad'anja tana mai ratsewa ta gefansa tabarshi nan tsaye bin bayanta yayi da kallo, zuciyarsa na k'una akan abin da tayi masa yaso binta amma kuma sai ya fasa.

D'aki ya koma ya kwanta yana tunanin laifin da yayi mata har tayi fushi dashi, jiya dai sun rabu lafiya amma kuma yau tana fushi dashi kodan yace zaije bai jeba?.

Sai kuma tunanin abin da yafaru d'azu ya fad'o masa arai.

"Safiyya ce tajawo komai kenan?".

Ya fad'a cikin ransa mik'ewa yayi zaune tare da fad'in.

"May be kishi ne !, zanyi k'ok'arin shawo kanta".

Abin da yafurta afili kenan ya mik'e ya fito daga d'akin zuwa waje, ya sake dubawa amma bai gantaba daga k'arshe ya tambayi Jakadiyya tace masa ta tafi gida tun d'azu, tsaki yaja aransa ya nufi b'angaren Mahaifiyarsa.

Wunin ranar haka Yarima yayi shi sukuku da shi, b'angaren Aynu ma haka abin yake.

Ya so ya bari har dare yaje wajenta ko yasamu nutsuwa cikin ransa, amma kuma ya kasa daurewa zuciyarsa nata faman azalzalarsa k'arfe hud'u da mintuna a shirin yayi parking motarsa bakin layin gidansu Aynu.

Ya fito ya kulle motar ya taka har zuwa k'ofar gidan tun kafin ya k'arasa ya hango ta tsaye da wani zuciyarsa sai da ta buga yayi k'arfin halin k'arasawa ya tsaya nesa dasu kad'an.

Yan da suke hiran Aynu na d'an murnushi abin sosai yake sosa ran Yarima, ji yayi kaman yaje ya shak'e wanda suke tare, amma dai ya daure ya cigaba da tsaiwa har sai da wani yaro yazo wucewa yace masa ya kirawo masa Aynu.

Aynu na sane dashi tunfarkon shigowarsa layin ta ganshi amma ta kau da kai suka cigaba da hirar da suke da Yasayyadi Umar.

"Aynu kije inji wancan mutumin".

Yaron ya fad'a yana mai nuna Yarima Fudhal.

Tare suka d'ago ita da Yasayyadi suka dubi inda Yarima yake tsaye ya had'e girar sama data k'asa.

"Waye wancan d'in?".

Ya Sayyadi ya jefa mata tambayar yana mai kallonta, Aynu ta k'ak'alo murmushi tana fad'in.

"Shine wanda nake yiwa aiki ai !, Yarima Fudhal ne".

Kai kawai Ya Sayyadi ya gyad'a yana fad'in.

"Jeki dawo to zan jiraki domin akwai maganar da zamuyi".

"To".

Abin da tace kenan, ta taka zuwa wajen Yarima wanda tun tawowarta ya kafeta da idanuwa yana kallonta, da sallama tak'arasa wajen tana mai kau da kanta gefe, mai makon ya amsa sallamar sai cewa yayi.

"Waye wancan?".

"Ya Sayyadi Umar kenan, malamin islamiyyar mune".

Ta bashi amsa, Yarima ya cize leb'ansa na k'asa yana mai cigaba da fad'in.

"Anan ma Islamiyyar kuke kenan?".

"A'a yazo duba Ummata ne".

"Dubiyar anan waje ake yinta?".

"A'a rakoshi nayi zuwa waje".

"Kinsan tsayin lokacin danayi anan, nasan kuma kafin zuwana may be kun jima tsaye".

"Ehh nasan kazo mana !".

Da sauri Yarima Fudhal ya dubeta jin amsar k'arshe data bashi, cikin kasa lallliyar murya ya furta.

"Meke faruwa ne Aynu?".

"Babu komai n, yi hak'uri na barshi tsaye bari inkoma".

Bata jira mai zai ce ba ta juya kawai ta barshi nan tsaye, Yarima binta yayi da kallo yama rasa mai ya kamata yayi.

Ya bita ko ya rabu da ita ne????.

Hello makaranta

Sai dai fa kuyi hak'uri dani domin alk'alamina bazai iya zayyane muku irin son da Yarima Fudhal ke yiwa Aynul-hayat ba, kamar yanda girman kai da jiji da kai ba zasu bar Yarima Baiyyanawa Aynu irin son da yake yi mata.

Kawai sai dai ku ayyana irin son a cikin ranku....!.

ASHA KARATU LAFIYA.

*YARIMA FUDHAL*

Na
FIRDAUSI S.A(QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

SADAUKARWA:-Namesy Phirdauceey Jibour.

18

Yana cikin wannan tunanin wayarsa dake hannunsa tayi ringing, ya d'aga yakara a kunnensa ba tare daya duba yaga waye mai kiran ba.

"Haba My...! Abbana yazo har gida anyi magana fa !, amma ko ka kirani mu tattauna batun auren mu...!".

Cire wayar yayi daga kunnensa ya duba screen d'in wayar sunan Saima ne d'od'ar bisa screen d'in, guntun tsaki yaja tare da mai da wayar kunnansa, ta cigaba da fad'in.

"Duk da ance mu biyu zaka had'amu zan amince ne kawai sabida son da nake maka.... !".

Cikin b'acin rai ya katse ta yana yana fad'in.

"Duk naji amma ki sani duka ku biyun babu wacce nakeso aciki, zaki iya kashe wayar !".

Ya fad'a yana mai kashe wayar ya jefata cikin aljihun wandonsa, ya mai da kallonsa kansu Aynu dake tsaye har lokacin suna hira.

Tsaki yaja ya juya kawai ya bar wajen zuciyarsa cike da sak'e-sak'e da kokwanto kala-kala, tare da dumbin tunanin nemawa kansa mafita tunkafin lokaci yak'ure masa.

Saima kuwa yana kashe wayar hawaye ya fara zarya bisa kuncinta zuciyarta na zafi da k'una, a haka Momynta tazo ta tadda ita, dafa kafad'arta tayi tana fad'in.

"Haba Saima !, har zuwa yaushe ne zaki samawa kanki mafita abisa muguwar damuwar dakika d'orawa kanki !, nad'auka damuwarki ta kau tunda har iyaye sunyi magana ?".

Saima ta fad'a bisa cinyar Momynta da ta zauna kusa da ita cikin kuka ta hau fad'in.

"Momy Yarima Fudhal ne !".

Tsaki Momyn tayi tana fad'in.

"Me kuma yayi miki yanzu?".

"Yace duka mu biyun wai baya sonmu !, Momy ji nake kamar zan iya mutuwa wallahi indai har na rasa Fudhal arayuwata !".

A jiyar zuciya Momyn tayi tana mai d'ago da 'yar tata zaune, ta kalli fuskarta sosai.

"Haba Saima kamar ba 'ya mace ba, kamarki ki zauna kinayi namiji kuka !, ni anawa ganin tun da har ya furta baya sonku ki hak'ura da auren sa kawai, ki danne zuciyarki akan Yarima ki barshi bari na har abada !".

"Momy taya hakan zai yiyu?, ina son Yarima sosai wallahi Momy ki taimake ni dan Allah !".

"Bani da wani taimako da zan iya yi miki wanda ya wuce addu'a, sannan zan sanar dake wani abu da baki saniba arayuwa, Saima..! akan ki auri namijin da baya sonki ke kike sonshi, gara ki auri wanda yake sonki ko da bakya sonsa, domin shi zai iya jure dukkan abin da zakiyi masa na b'acin rai, sab'anin wanda kike so, kuma ba lallai auren yaje ko inaba kuskure kad'an zaki zai iya rabuwa dake rabuwa ta har aba da !".

Saima zaune tayi tana sauraren Momynta kawai, lokaci-lokaci tana share hawayen fuskarta, wayarta dake kusa da Momyn tayi ringin Momy ta d'auka ta kara a kunnensa sabida ganin number da tayi babu suna, daga can b'arin aka hau fad'in.

"Please Saima gani nan tsaye cikin gidanku !, dan Allah yau dai kifito ko gaisawa muyi kada ki shanyani kamar ko yaushe".

Momy ta kashe wayar tana mai kallon Saima tare da mik'a mata wayar tana tambayarta.

"Waye wannan?".

Saima ta b'ata rai kafin ta bata amsa.

"Momy wanine wallahi duk yabi ya takuramin".

"Har tsawon wane lokaci ya d'auka yana zuwa gidan nan?".

"Inajin dai zuwansa uku".

"Amma shine kike wulak'anta mutum Saima !, duk wanda yace yana sonka arayuwa ya gama maka komai fa !, tashi ki fita".

"Momy nidai ki rabu da shi dan Allah".

Tayi maganar cikin shagwab'a har ragowan hawayen fuskarta na fitowa.

"Ki tashi kije nace !, tum kafin ranki ya b'aci, bana son musu kin sani ".

Saima ta mik'e cike da k'uk'uni ta shige toilet ta wanko fuskarta ta fito, dama doguwar rigace a jikinta ta janyo wani yalolon mayafi ta yafa akanta ta fice.

Momy ta bita da kallo tana fad'in.

"Saura kuma inji kin wulak'antashi ".

Yana tsaye jikin motarsa cikin wata sky blue d'in shadda wanda tasha d'inki d'an ubansu, hular kansa da takalminsa duk iri d'ayane farare, kansa na kan wayarsa dake hannunsa yana daddan nawa, iya had'uwa ya had'u son kowa k'in wadda ta rasa lol.

Saima tun da ta fito take binsa da kallo aranta taji ya burgeta sosai, yanayin tsayuwarsa da sajen fuskarta tamkar na Yarima, ba da ban zuciyarta ta tsumu da soyayyar Yarima ba da babu abin da zai hanata aminta da wannan gayen, abin da ta aiyana aranta kenan.

Da sallama ta isa wajen ya d'ago kai cike da murmushi yana amsa mata tare da fad'in.

"Yau wace rana ce?, rana mafi sa'a agareni...ranar da bazan mance da ita ba....domin nayi to zali da mafi haske a cikin mata.....yau ta amsa sallamar d'an talikin da baya da zuciya akanta ko yaushe !".

Saima bata san sanda murmushi ya sub'ucewa fuskarta ba, dubansa tayi akaro na biyu kamar zatayi magana sai kuma ta kau da kai gefe.

"Yi hak'uri Madam kada dai incikaki da surutu, sunana ANWAR SALISU MAI KUD'I, nasan zaki iya sanin mahaifina ko kiji sunansa?".

Kai Saima ta gyad'a tana fad'in.

"Ehh na sanshi kace kai na gida ne ma, ai mahaifinka abokin Abbana ne".

Murmushi Anwar yayi yace.

"Nima nasan da hakan !, na d'auka ke baki san hakan bane?".

"Na sani ! ".

Ta bashi amsa a tak'ai ce, shiru ne ya biyo baya kafin ya katse shirun da fad'in.

"Saima a gaskiya bazan b'oye miki, gaskiya tun sanda na ganki a wajen birthday d'in Yarima kika kwantamin arai, sai dai naso dannewa sabida tsoron irin tarbar da zan samu daga gareki, amma zuciyata ta gaza samun nutsuwa da hak'urin da nake bata ako da yaushe".

Sosai k'irjin Saima ya buga jin ya ambaci sunan Yarima, sai dai tayi k'ok'arin danne zuciyarta, tare da k'ak'alo murmushin dole, ya cigaba da fad'in.

"Ina fatan zaki karb'i k'ok'on bara na Saima?".

"Kar ka damu zanyi shawara akan hakan".

"Ok sai dai ina neman wata alfarma?".

"Alfarmar me kuma?, fad'i ina jinka".

"Kimin alk'awarin zaki dinga d'aukan kirana dan Allah".

Saima tayi shiru na d'an wani lokaci kafin ta ce .

"To babu damuwa Allah ya bani ikon cikawa !".

"Amin".

"Ni zan koma, sai yaushe zan dawo kenan?".

Sosai Saima ta farajin hiran na gundurarta cikin sauri ta bashi amsa.

"Ko yaushe ma".

"Nagode sosai, sai kinjini a waya".

"To".

Ta juya kawai tabar wajen, ba tare datayi tunanin komai ba, domin ta kasa daurewa zuciyarta da tsayuwar da takeyi da shi.

Anwar yabi bayanta da kallo yana dariya cikin ransa.

***

Ta sowarsu kenan daga islamiyya suna tafe suna hira jefi-jefi Zainab ce ma ginshik'in hiran, can tayi shiru ta dubi Aynu da fad'in.

"Kamar fa kina cikin damuwa Aynu?".

Aynu tayi yak'e tare da duban Zainab tace.

"Wallahi abubuwa ne sunk'ullemin kai sosai, kinsan Yarima Fudhal yana sona to gefe guda kuma Yarima Jalil shima yace yana sona har yana fad'in inrabu da Yarima Fudhal indawo wajensa, ta d'aya gefan kuma Ya sayyaadi Umar".

"Dama na sani ai !, inkaga kare na shin-shinar takalmi to d'auka zaiyi, nidai kinsan daman na gaya miki na fisonn ki da Yarima Fudhal wallahi Aynu?".

"Ni kuma kinga Ya sayyadi yafi kwantamin arai domin shine dai-dai ni, shi yafi dacewa dani da rayuwata".

Zainab taja dogon tsaki.

"Ke kam bakya fahimta wallahi !, yauwa ni kuwa mai ya had'aku da Yarima Fudhal ne?".

"Mai kika gani?".

"Babu komai, naga dai kamar bakwa shiri kamar da".

"Ehh to gaskiyar daya b'oyemin akansa ne ta fito fili".

"Kamar ta me fa?".

Nan Aynu ta kwashe dukkan abin da yafaru tsakaninta da Yarima Jalil ta sanarwa Zainab.

"Ni na yanke shawaran barin Yarima Fudhal kawai?".

Cike da fushi Zainab ta hau fad'in.

"Zancen banza !, wai ke haryanzu baki san waye Yarima Jalil ba ko?, lallai da sauran ki Aynu to Jalil ya wuce dukkan tunaninki da har zaki d'auki maganarsa gaskiya wallahi zai kai ki yabaroki ne kawai".

"Nifa gani nayi gaskiya ya fa'amin ai".

"Gaskiyarsa d'in banza !, baki d'auki shawaran da nabaki ba ko?, shikenan kinga tafiyata ni".

Zainab ta wuce tabar Aynu nan tsaye tana ta kwala mata kira amma tayi banza da ita.

*YARIMA FUDHAL*

Na
FIRDAUSI S.A(QURRATUL-AYN).

NAGARYA WRITERS ASSOCIATION®

SADAUKARWA:-Namesy Phirdauceey Jibour.

Yarima Fudhal na shirin fitowa faga falonsa shima Yarima Jalil na fitowa tare da wata 'yar aikin gidan, yarinyar ta rissina ta gaishe da Yarima Fudhal tabar wajen da sauri, wani mugun kallo Yarima Fudhal ya watsawa Jalil yana fad'in.

"Wai kai yaushe ne zaka san abin da yake maka ciwo ne?, idan aure kake so ka sanar ayi maka mana da wannan muguwar rayuwar da kake?".

Yarima Jalil ya sosa k'eyar kansa yana fad'in.

"Broda bafa laifina bane 'yan matan ke bibiyata fa !".

"Ehh naga alama !, kenan Aynu ma bibiyarka takeyi ko?".

Yarima Jalil ya d'an fiddo ido waje alamun tsoro k'arara bisa fuskarsa kafin ya wayence ya nemowa fuskarsa murmushin dole tare da fad'in.

"Haba dai..!, kawai mutuncin Yarinyar nake gani amma...?".

"Daga yau ina so ka daina ganin mutuncin nata !, bana shiga harkar rayuwarka kasani ko?, kasan nafi kowa sanin waye kai Jalil?, kayi tunani idan na sanarwa duniya ko kai waye mai zai faru?, to inaso ka fita cikin tawa rayuwar kafin zuwan lokacin da zaka fara fuskantar fushi na !, fatan ka fahimce ni ?".

Yayi kwafa tare da barin wajen yabar Yarima Jalil tsaye yana binsa da kallo har sai da yaga ya b'acewa ganinsa sannan yayi dariya yana fad'in.

"Ina....bazai yiyu inzuba ido a cikin gidan nan ana neman mai damu bayi ba !, mumafa 'yayane da har zai kasance komai sai kai !, yanda aka raba ni da Gimbiya Safiyya to kaima dole ka hak'ura da Aynu..!".

Ya juya ya koma cikin falonsa cike da dariya ciki-ciki.

Aynu da ke shara falon Yarima Fudhal duk tanajin abin da ya faru, babu abin da yafi d'aure mata kai sai maganar Yarima Jalil ta k'arshe har sake mai-maita maganar tayi cikin ranta.

"Yanda aka rabani da Gimbiya Safiyya to kaima dole ka hak'ura da Aynu....".

"Ke nan Yarima Jalil yayi hakane domin yarabamu?, kenan son da yake fad'a yanaimin duk k'aryace?, ashe gaskiya Zainab take gayamin na kasa fahimta?".

Aynu ta zauna d'abas ak'asan carpet tana tunani kala-kala, tsoro ya kamata sosai har dai da ta tuna irin wulak'ancin da tayiwa Yarima Fudhal, take ta yanke aranta zata bashi hak'ura.

"Zai hak'ura kuwa?".

Wani b'angare na zuciyarta ya jefa mata tambayar, tayi ajiyar zuciya tare da addu'ar Allah yasa ya hak'ura, domin itama cikin kwanakin nan Allah kad'ai yasan halin da tashiga sabida k'auracewa Yarima Fudhal da tayi sauk'in tama tana ganinsa kullum duk da cewa bata kulashi hakan na d'an rage mata damuwar dake k'unshe k'asan zuciyarta.

Yarima Fudhal kuwa yana barin wajen neman Zainab yaje yi, a can b'angaren mahaifiyarsa suka keb'e waje guda babu wanda yake iya jin dukkan abin da suke tattaunawa akai, amma da ka kalli fuskar Yarima Fudhal zaka san ransa a b'ace yake sosai.

Sun shafe tsayin lokaci kafin yabar wajen ya koma b'angarensa, zaune ya tadda ita tayi zurfi cikin tunani bai kulata ba illa neman guri da yayi ya zauna yana fuskantarta ya k'ura mata ido na wani lokaci kafin yayi gyaran murya mai k'arfi daya sanyata d'ago kai da sauri tana kallonsa.

Aynu ta sauke kanta da sauri ba tare da tace komai ba.

"Tunanin me kike?".

Ya jefa mata tambaya shiru tayi na d'an lokaci tana wasa da yatsun hannunta tana son yin magana amma kuma ta kasa, shima bai kuma cewa da ita komai ba illa kafeta da idanuwa da yayi shi komai Aynu takeyi ba k'aramin burgeshi take ba, da k'yar dai ta iya furta.

"Kayi hak'ura abisa abin da nayi maka !".

Ta fad'a ba tare da tayi tunanin bashi amsar tambayarsa ba.

"Babu komai, amma kinsan wani abu kuwa?".

Kai ta girgiza alamun a'a, ya cigaba da fad'in.

"Mai yasa kika k'i sanarmin dukkan abin da ya faru tsakaninki da Jalil?, ke nan har yanzu baki rabu da shi ba?".

"A'a, babu yanda zanyi ne akan had'uwata da shi".

"Ok..amma mai yada kika d'au maganarsa serious ba tare da bincike ba?".

"Kawai na kasa tausar zuciyata ne".

"Aynu !, har yanzu baki yarda da son da nake maki bane?, ko nine baki yarda dani ba?".

"A'a na yarda mana".

Ajiyar zuciya Yarima Fudhal yayi yana mai cigaba da kallonta tare da nazarin yanayinta, kafin yace.

"Kada ki yaudari zuciyarki kamar akwai abin da kike kokwanto a kaina haryanzu, zanyi k'ok'arin kau da kokwantanki nan da lokaci k'ank'ani zaki fahimci waye ni Fudhal?".

"Amma kafin nan kisani ina k'aunarki sosai wallahi Aynu sai dai bazan iya tsayawa inyi miki bayanin son da nake miki ba amma zaki iya karantar hakan a cikin idona, sannan ni aganina tsayawa infad'awa mace irin son da nake mata k'auyanci ne kiyi hak'uri dani Aynu a duk yanda kika ganni, kiyi hak'uri da halayyata".

Murmushin jindad'i Aynu tayi domin sosai takejin dad'in kalamansa a cikin zuciyarta, ta fahimci Yarima Fudhal sosai yana sonta sai dai girman kai da izzar mulki bazai bashi damar nuna mata ba, duk da wani lokacin tasan zuciyarsa na rinjaye akan girman kansa indai akanta ne.

"Ba kice komai ba sai murmushi da kike?".

Aynu ta sanya tafukan hannunta ta rufe fuskarta wai ita a dole kunyarsa takeji, murmushi yayi mai sauti yace.

"Kunyarki na burgeni  Aynu, ina son mace mai alkunya sosai".

Ita dai Aynu ta gaza cewa komai, ya cigaba da fad'in.

"Wannan malamin naku naga kaman yana neman wuce gona da iri fa !, domin Zee ta fad'amin cewa shima sonki yake?".

Ya k'arashe maganar tare da guntun tsaki, Aynu ta d'anyi murmushi kawai.

"Ina magana  kinyi shiru?".

"Ni mai zance to".

"Komai ma kice, ina buk'atar jin muryar taki".

"Kinsan wani abu ?".

"Bari inje fada yanzu, anjima kad'an zan dawo ka da kitafi gida ki jira ni ".

Ya k'arashe maganar yana mik'ewa tsaye tare da sakarwa Aynu wani tsadaddan murmushi da bata tab'a ganinsa saman fuskar Yarima Fudhal ba sai yau, Aynu ta mayar masa da martanin murmushinsa tana fad'in.

"Angama Ranka ya dad'e !".

Yasa yatsan hannunsa d'aya ya lakuci karan hancinta yace.

"Kema ranki ya dad'e Gimbiya".

Ya fice yabarta zaune falon, yana fita tamik'e ta k'arashe sharar falon zuciyarta fari k'al, har wani sanyin dad'i takeji yana ratsa dukkan wasu k'ofofin gashin dake jikinta.

A gag-gauce ta kammala ta fice zuwa wajen Zainab domin taji dalilin da yasa ta sanarwa Yarima Fudhal komai.

Zainab tace "aini fushi nake da ke Aynu tunda har zaki yarda da maganar Yarima Jalil".

"To ya kikeso nayi ne Zainab kishi ne duk yajamin hakan"

Dariya suka d'anyi kad'an Zainab na fad'in.

"Kaga masoya !, Aynu ta Yarima Fudhal d'inmu".

"Ke banson iskanci fa !, me yasa kika sanar mishi abin da na fad'amiki?".

"Me zai hana bazan sanar masaba d'an bawan Allah na neman zaucewa akanki, wallahi Aynu Yarima Fudhal yana sonki sosai bazan daina fad'amiki ba".

"Nima na sani Zainab, to amma ai naga mata biyu zai aurafa, kenan ni zai aura ta uku kome?, ko kuwa matsayim k'warkwara zai aure ni?".

"Wannan ne bansani ba gaskiya".

Aynu tayi ajiyar zuciya tana fad'in

"Nasan inason Yarima Fudhal nima, amma bazan iya kishi da Gimbiya Safiiya ba".

"Nima inna tuna haka abin nad'an tsorata ni, kawai dai muyita addu'a shima abin da ya gayamin kenan".

" Yauwa wai kuwa kinsan abin da naji Yarima Jalil na fad'a d'azu?".

"Sai kin fad'a ina jinki  bani labari".

"Na fasa fad'a domin nasan sai kin gayawa Yarima Fudhal, in kina son ji sai kinyi alk'awarin bazaki fad'a masa ba".

Zainab tayi shiru tana duban Aynu taga tabbas da gaske take hakan yasa tace.

"To na amince fad'amin".

Aynu ta kwashe komai ta fad'awa Zainab, Zainab zaro ido waje tayi tana fad'in.

"Kin ji ko?, ai nagaya miki dama kiyi hankali da Yarima Jalil ya wuce dukkan tunaninki wallahi".

*YARIMA FUDHAL*

Na
FIRDAUSI S.A(QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

SADAUKARWA:-Namesy Phirdaucee Jeebour.

20

(Kuyi hkr dani abisa rashin jina da kukayi kwana biyu, amma yanzu komai nml insha Allah zaku dunga jina kullum, ngd sosai sosai masoyana da masu call zuwa message).

"Ya bawa da kyakykywar halaiyarka tasa na aminta da kai !, na baka dama ka cigaba da zuwa wajen Aynu, kafin zuwan lokacin da zamu san abinyi, duk da cewa sai kayi hak'uri da ita sosai domin Aynu yarinyace haryanzu batasan me rayuwa take ciki ba...".

Aynu da keshirin shiga gida taji Babanta yana yiwa Ya sayyadi Umar maganar, sosai k'irjinta ya buga har sai da tad'an dafe wajen da hannunta.

"Gata nan ma ta dawo ai".

Babanta ya fad'a fuskarsa cike da fara'a, Aynu ta durk'usa ta gaisheshi ya amsa yana mai cigaba da fad'in.

"Ga Malaminku nan, anan na sameshi yana zaman jiranki, ni bari ink'arasa bakin kasuwa ".

"To Baba Allah kiyaye !".

Sukayi maganar kusan atare, Aynu ta mik'e tsaye tana mai duban fuskar Ya sayyadi, sai dai yau d'aya sai taji bata son ganin fuskar tasa ma, d'auke kai tayi gefe tare da fad'in.

"Ina yini?".

"Lafiya k'alau Aynu, kwana biyu kinjini shiru ko?".

"Ehh".

Ya Sayyadi yayi d'an guntun murmushi.

"Zuwa nayi har gida inji amsa ta".

"Amsar mefa?".

"Ohh kina nufin kin manta Aynu?".

Aynu tayi k'ok'arin nemo murmushi saman fuskarta.

"Wannan mai sauk'ine tunda gashi har Baba ya amince da kai".

"Kina nufin kema kin amince kenan?".

Murmushi tayi tare da gyad'a kai, alamun ehh.

"Alhamdulillahi...Aynu nagode sosai Allah ya tabbatarmin da mafarkina akan ki".

Mai-makon ta amsa da amin sai cewa tayi.

"Zan shiga gida sai zuwa anjima nagaji wallahi".

"Babu komai Aynu kina buk'atar hutu dama, a gaishemin da Umma".

"Za taji".

Ta fad'a tana mai shigewa cikin gida ta barshi nan tsaye.

Kafin shima ya kama hanya yabar wajen.

***

" Ya kamata indai da gaske kana sona Iyayena su sanka ko?".

"Kamarya kenan !, wani abu ya faru ne?".

"Ehh jiya naji Babana yana bawa Ya Sayyadinmu umarnin ya cigaba da zuwa wajena, kuma baki d'aya su Umma shi suka sani basu sanka ba".

Ajiyar zuciya Yarima ya d'anyi, yana mai duban fuskar Aynu dake k'asa sosai yake nazarinta kafin ya bud'e baki ya fara magana.

"Ke yarinyace Aynu !, nasan cewa ina sonki sosai Aynu amma kamata yanda nake d'innan har saina k'ask'antar da kai zan samu abu?".

"Ban gane ba?".

Aynu tayi tambayar tana mai duban fuskarsa.

Dafa kafad'arta yayi da hannunsa guda d'aya, d'ayan hannun kuma cofin juice ne yana sha.

"Nifa d'an Sarki ne !, muna da kud'i da mulki aganinki ko da mahaifinki ya bayar dake idan naje zai hanani auren ki?, idan ma zai hana ai ga kud'i !".

Aynu tabishi da kallo kawai tana nazarin maganarsa amma ta kasa fahimtar abin da yake nufi, shima kuma dama bawai buk'atar fahimtarta yake ba.

" Karki damu Yarima naki ne har abada !, Mubar wannan maganar kinji ?".

Yayi maganar yana mai zama a gabanta suna fuskantar juna, aransa yasan gaskiya ta fad'a amma girman kai da Izzar mulki bazasu bari yakai kansa gaban iyayen taba domin shi akomai nasa yanayin ammafani da mulki da kud'i ne, yasan kuma indai akwai kud'i tamkar ya samu Aynu ne, domin yasan iyayenta gajiyayyu ne ba tunyanzuba sabida bai je k'ofar gidansu ba sai

da ya fara sanin wacece Aynu?.

Murmushi Aynu kawai tayi tare da dubansa duk da cewar zuciyarta bata aminta da zancen da yayi ba, shima kuma ya karanci hakan, amma yasan duk iya tunaninta bazai tab'a kawo kan abin da yake nufi ba.

Gimbiya Safiyya ce ta shigo fuskarta cike da murmushi, amma yanayin data gansu ya sanya fuskarta canjawa daga murmushi zuwa b'acin rai, Aynu tayi k'ok'arin mik'ewa da sauri ta tsaya, shi kuwa gogan ko a jikinsa wai antsikari kakkausa, saima cigaba da shan juice d'insa da yayi bai ko kalli inda take ba bare ya nuna mata cewa yasan ta shigo.

Sosai Safiyya taso danne zuciyarta sai dai shaid'an yaci galaba akanta ta hanyar hura wutar kishi sosai a cikin ranta.

A hankali ta taka zuwa inda Aynu take sai jin sautin k'arar mari kawai Yarima yayi akunnenta ya d'ago da sauri dan ganin wa aka mara ?, ganin Aynu yayi rik'e da kunci tana bin Safiyya da kallo, Safiyya ta watsa mata wani mugun kallo tare da fad'in.

"Banza kawai KARUWAR CIKIN GIDA....!".

Kafin ta kai ga rufe bakinta Yarima Fudhal shima yad'auke ta da wani gigitaccen mari, ba Gimbiya Safiyya ba hatta Aynu ta girgiza da marin da Yarima ya yiwa Safiyya, cike da b'acin rai yake fad'in.

"Zaki iya sanya hannu ki mare ni in kyaleki, amma tunaninki zaki mari Aynu natsaya ina kallonki ne!, idan kin kirata da karuwar cikin gida ke kuma a kira ki da me?, akwaima mace mara aji da rashin kamun kai data wuce matar da zata biyo saurayinta har cikin gidansu ta zauna kuma kullum k'afarta na hanyar d'akinsa wai da sunan soyayya?".

Shiru ya gauraye d'akin sai aikin kallon-kallo da sukeyiwa junansu, Yarima Fudhal ya katse shirun da fad'in.

"Akwai banbanci mai yawa tsakanin Mace me kyau Mara aji da mummuna mai aji !, da yawan 'yan mata kuna daukar aji da ake fada abun wasa ne toh aji Yana nufin wadda take tamkar MAR'ATUSSALIHA irin macen da akai kwatan ce da ita a ilmance wallahi dana auri mai kyau ballagaza mara kamun Kai kwara mummuna mai aji da sanin hak'k'ina !, har yanzu bangama aminta da tarbiyarki ba, taya zan auri macen da tarbiyarta bata wadace taba bare ta baiwa 'ya'yan da zata haifa zuwa gaba ?, kiyi tunani da kyau sosai Safiyya ni Yarima Fudhal ko kusa ban dace da ke ba sabida ni ba ajin ballagazar mace bane !".

"Sannan ina mai baki kyakykyawan albishir ki gayawa kowa AYNUL-HAYAT nakeso wato 'yar aikina kuma Baiwata !, ko da kinmatsa na aure ki to kisani babu d'igon sonki a cikin raina !, domin nasan ke baki da aikin da yawuce kai k'arata to bismillah...!".

Ita dai Aynu tana gefe tana aikin zubar hawaye k'asan zuciyarta kuwa Innalillahi wa'inna ilaihi raji'un kawai take ambato domin tasan Allah kad'ai yasan yau iya yawan ruwan da Yarima yab'allo mata.

Shi kuwa a ganinsa hakan da yayi ne dai-dai domin shi bayason takura a cikin rayuwarsa, yayi hakan ne domin ya share tunaninta naganin cewa yana sonta kawai sharewa yake, a gefe guda kuma hakan yake ganin mafita wajen warwarewar alak'ar aurensu da akeson k'ullawa.

Zuwa yayi gaban Aynu ya kama hannunta ya jata zuwa cikin bedroom d'insa ya bar Gimbiya Safiyya nan tsaye kamar anjona mata lantarki, tayi mutuwar tsaye hawayan dake zuba kan fuskarta ne kawai zai iya tabbatar maka kasan cewa da ranta ba mutuwa tayi ba tsabar kad'uwa da tayi da maganganun Yarima Fudhal.

Toilet ya kai Aynu tare da fad'in.

"Wanke fuskarki, kada ki fita da hawaye".

Shi kuma ya dawo cikin d'akin gefan katifarsa ya zauna tare da dafe kansa yana tariyo abubuwan da suka faru.

"Mai Martaba...!".

Ya furta hakan afili yana mai d'ago kansa da sauri cike da kad'uwa hankalinsa ya tashi sosai.

Ko meye dalilin hakan ?, Oho.

Gimbiya Safiyya kuwa da k'yar ta iya d'aga k'afafuwanta tabar cikin falon ta koma b'angaren Fulani Sokoto tana tafe tamkar zata fad'i, duk inda tawuce sai anbita da kallo tare da tambayarta lafiya?, amma bata iya furta komai sai hawayen takaici dake bin fuskarta.

Tana shiga falon Fulani ta zube k'asa tare da fad'in.

"Wayyo Allah Momy ki taimake ni wai baya sona!".

Fulani Sokoto da Jalila sukayi ca akanta kowa na tambayarta.

"Lafiya !, mai ya faru ?".

Safiyya ta fad'a kan cinyar Fulani ta kifa kanta, tana mai cigaba da rera kukanta, d'ago da

kanta Fulani tayi tare da fad'in.

"Kalle ni Safiyya share hawayenki ki bani bayanin abin da yafaru, domin insan abinyi insan irin lallashin da ya kamata inyi miki, amma kinzo kin sani gaba kina kuka ban san me ya faru ba taya zan lallashe ki?".

Gimbiya Safiyya ta share hawayenta ta fara bawa Fulani labarin dukkan abin da ya faru bata rage ko d'aya ba illa k'arin masu sugar da tayi cikin bayanin nata domin Fulani Sokoto ta zuciya sosai.

Ai kuwa idan ran Fulani ya kai duba ayau yab'aci, amma da yake mata ce irin 'yan duniya da suka goge a iya bariki murmushi tayi tana fad'in.

"Wannan ne zai tada hankalinki?, har kizo kina ihu akan wani banzan kwaro Fudhal !, kwantar da hankali ai anzo inda nake so azo WACECE AYNUL-HAYAT kuma ?, hmmmm karki damu yanzu za'a fara wasan indai ni naci sunan nawa da ake kirana dashi Fulani Sokoto zanga tayanda za'ayi Fudhal ya samu dukkan cikar burinsa a duniya !, bare kuma har ya auri wacce yake ikirarin ita yake so !, kuma ko yak'i ko yaso sai kin aure shi indai ina raye.... !".

Jalila dake zaune gefe tana jin batun da mahaifiyar tasu takeyi tayi wani guntun murmushi tace.

"Ai dama Momy ke kika k'yale komai haka sakaka wallahi, ya kamata ki tashi tsaye tun da wuri!".

***

Zainab ce zaune falonsu tasa kwanun abinci a gaba tana ci gefe guda kuma Maman tace zaune tana yankan farce, Zainab ta d'an dubi Mamanta tace.

"Wai kuwa Mama idan saurayi yace bazai zo gidanku yaga iyayenki ba susan juna, kawai dai yasan ko bayan anba dake zai zo da kud'ine yasan kuma dole a bashi ke me hakan ke nufi?".

Baba Ta Sallah tabar yankan farcen tana duban Zainab tare da tambayar .

"Waye wannan shi kuwa?".

"Wani ne ya gayawa Aynu wallahi".

Baba Ta Sallah tayi ajiyar zuciya kafin tace.

"A iya sanina da tunanina da kuma duk wanda yaji wannan zancen, abin da zai d'auka koma ince yanda gaskiyar al'amarin yake, shi wannan saurayin kwata-kwata baisan muhimmanci iyayenta ba, asalima ko da auren akai taya zai daraja iyayenta domin a ganinsa iyayen banza ne sun bada 'yarsu shi kuma yazo ya nuna kud'i anbashi ita !, wannan mutumin baya daga cikin irin mazajen da ya kamata mace ta aura".

Zainab tayi shiru tan duban Baba Tasallah kafin tace.

"Mama Yarima Fudhal shiya fad'awa Aynu haka, ni abin ya bani mamaki fa, yanzu ace duk irin son da yake nunawa da fad'a yanayi mata kenan ya tashi abanza tunda bai d'auki iyayenta bakin komai ba?".

"Sosai ma kuwa ni dama tunda kika bani labarin yana son Aynu nasan za'ayi haka, ku a tunaninku gidan Sarkin nan da danginsu baki d'aya sund'auki talakan mutum a bakin komai ne?".

"Ban gane ba Mama?".

"Ku yara ne yanzu kukazo duniya, amma abin da baki sani ba shine Sarki Ubaiyd bai d'auki talaka abakin komai ba illa ya zama bawansa, kuma a hakan ya tarbiyartar da iyalinsa".

"Amma kunsan hakan kuka bari muke aiki a gidan?".

"Dole ce ta sanyamu Zainab da muna da yanda zamuyi da ko k'ofar gidan ba zamu je ba".

Zainab shiru tayi tana duban Mamanta cike da tambayoyi kala-kala amma ayanda ta karanci yanayin Maman bazata iya sanar da ita komai ba.

KO MEYE DALILI?.

Nima kaina ina buk'atar sanin wannan amsar, amma nasan koma mene akwai wani boyayyan al'amari.

*YARIMA FUDHAL*

Na
FIRDAUSI S.A(QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

SADAUKARWA:-Namesy Phirdaucee Jeebour.

21

DARE
9:00PM

Falon Mai Martaba cike yake da mutanan gidan sabida meeting d'in gaggawa da Mai Martaba ya shirya a daran nan.

Gefe guda Mai martaba Sarki Ubaiyd ne kishingid'e bisa kusun, daga wajen kansa Fulani Bingel ce tare da 'ya'yanta Aunty Sadiya da Aunty Sa'ida mazajensu suka kawosu, sai Yarima Fudhal daga wajen k'afarsa kuma Fulani Sokoto ce tare da 'ya'yanta ita ma a kusa da ita, Yarima Jaleel da Jalila sai Gimbiya Safiyya .

Mai Martaba ya shafe tsayin lokaci yana bin iyalinnasa da kallo, kafin yayi gyaran murya tare da jero addu'o'i sannan yayi sallama suka amsa ya fara fad'in.

"Ba komai ne yasa ni shirya wannan taron na gaggawa ba sai dalilin faruwar bijirowar wata b'araka daga cikin danginmu, da kuma shirya rushewar martabar danginmu da mutuncin sarautarmu!".

"Fudhal...!".

Mai martaba ya kira sunan da kakkausar murya.

Kowa sai da ya dubi Mai Martaba domin yau karo na farko da sukaji ya kira Yarima Fudhal da sunansa sab'anin Magaji da akafi ji yana kiransa da shi tsayin shekaru.

Mai martaba ya cigaba da maganarsa.

"Fudhal kai ne ke shirin ruguza mana komai !, mene haka ka ke shirin aikatawa ?, k'asar wajen da na kai ka tsayin shekaru kayi karatu abin da suka koya maka kenan soyayya da Baiwarka?".

Yarima Fudhal yayi shiru kansa a k'asa ya kasa iya d'aga kansa bare har ya iya bada amsar tambayar da ake yi masa, mai martaba ya cigaba da fad'in.

"Karka manta kaifa magaji ne a bayana, shin kanason bijirewa umarni nane kome?, ko kuwa ban isa da kai bane?, kar kamance ni Ubaiyd bana magana biyu auren ka da Safiyya tamkar anyi angama ne !".

Sai lokacin Yarima Fudhal ya d'ago kai ya kalli Mai Martaba kafin ya sake yin k'asa da kansa ya fara magana.

"Bazan gajiya wajen neman afuwarka ba, sai dai ina rok'o agareka Abba ka taimaka kabani zab'in raina nasan hakan tamkar tozarcin Family namu ne amma babu yanda na iya ne tabbas inason Aynu amma da ace ina da damar da zan iya cire soyayyar da na cire ta domin samun yardarku da cika umarninku...!".

Yayi shiru nad'an wani lokaci yana jira yaji ko Mai martaba zai ce wani abu jin da yayi bai ce komai ba yasa yacigaba da magana.

"Kayi hak'uri Abba !, ni banyi haka domin na bak'anta ranku ba burina kullum bai wuce ganin farin cikin iyayena ba ko da zan rasa raina !, amma Abba ina son yarinyar ne badan komai ba sai domin ta can-canci a so ta, sabida tarbiyarta da kamalarta....sannan!".

"Kaga ya isa Magaji !, ban kira ka dan intambayeka can-cantar taba ko tarbiyarta na kira ka ne domin in tabbatar maka kome za kayi aure kai da Safiyya da Saima babu fashi sai dai idan sune sukace basa so !, kuma babu kai babu auren wannan Baiwar KO BAYAN RAINA !".

Yarima Fudhal ya rintse ido sabida yanda yaji zuciyarsa na zafi sosai, har jiyake kamar ransa zai iya barin gan-gan jikinsa a lokacin.

Fulani Bingel ta dubi d'an nata tare da duban Mai Martaba, ta so yin magana amma tasan bazai saurareta ba, tana tausayawa Yarima Fudhal domin tasan halinsa ko kad'an bai iya sanyawa ransa damuwa ba.

Mai Martaba ya sake duban kowa kafin yace.

"Sannan ita kuma yarinyar daga yau tabar aiki a gidan nan, kowa ya tashi ya tafi ".

Wannan hukuncin bak'aramin dad'i yayiwa Fulani Sokoto da Yarima Jaleel ba, musamman uwar gayyar Gimbiya Safiyya gefe guda kuma ga Aunty Sa'ida domin itama tak'i jinin ace Yarima Fudhal yarasa wadda zai lak'ewa sai Baiwarsa tir da wannan al'amarin.

Kowa ya mik'e ya fice ban da Fulani Bingel da Yarima Fudhal ya ya kasa mik'ewa, domin yasan indai yamik'e a wannan lokacin to tabbas sai dai su d'au keshi hakan yasa yayi zamansa yana karanto addu'o'i cikin ransa, Mai Martaba ya dube shi duba na musamman yana fad'in.

"Ka kwantar da hankalinka Magaji kai fa magajina ne, akan wane dalilin zaka bari ka lalata rayuwarka a banza?, ina so ka cire duk wata damuwa dake cikin ranka kayi ayyukan dake gabanka, an kammala ginin Asibitin dana shirya gina maka, na gayyato gwararrun likitocin da zasuyi aiki a cikinsa tare da kai, zuwa nan da sati guda sai ayi bikin bud'eshi ko?".

"Ehh duk yanda kace Abba, Allah yasaka da alkhairi ya k'ara girma da arzik'i ".

"Amin".

Fulani Bingel ta amsa tare da cigaba da fad'in .

"Ka k'ara hak'uri kaji ?, komai mai wucewa ne a rayuwa !".

"Insha Allah".

Yarima Fudhal ya mik'e yana mai jan k'afafuwansa da sukai masa nauyi tare da bin bango yabar d'akin kai tsaye d'akinsa ya nufa ya shige toilet ya sakarwa kansa ruwan shower mai sanyi domin wai yaji sanyi cikin ransa.

Fulani Bingel ta dubi Mai Martaba bayan fitar Yarima Fudhal tace.

"Da anbi komai a sannu Mai Martaba !, wannan hukuncin kamar yayi tsauri domin ban da Allah babu wanda yasan matar mutum, domin shi al'amarin aure sai anbi a sannu...!".

"Ki na so ki goyi bayan d'anki ne?".

"A'a ko kusa kaima ai d'an kane".

"To bana buk'atar jin wani k'orafi cikin maganar da nayi !".

"Allah ya huci zuciyarka !".

***

Ko da Aynu ta koma gida wunin ranar tayi shine sukuku, har zuwa sanda ta dawo daga Islamiyya ta zauna gaban Ummanta tare da d'aukan littafin Hisnul-muslum tana dubawa, Umman ta d'an kalli gefen da Aynu take zaune tace.

"Meye alak'arki da Yarima Fudhal kuma?".

Aynu ta d'ago da sauri fuskarta cike da murmushin jindad'i domin ansosa mata inda yake mata k'yaik'ayi.

"Umma ba wani abu bane bafa, kawai dai cewa dai yayi wai yana....!".

Sai kuma tayi shiru domin jin nauyin mahaifiyarta akan maganar da zata fad'a mata.

Umma tayi 'yar dariya tare da k'arasa mata maganar da take son yi.

"Yana sonki ko?".

"Ehh".

"Aynu kenan...!, amma kinsan abin da zan fad'a miki kuwa?".

"A'a umma".

"Duk da cewa ba ganinki nake da ido ba, amma ina kallonki ta zuciyata, nasan kina son Yarima Fudhal amma kada ki bari soyayyarsa tayi tasiri aranki da yawa domin mudai iyayanki zab'inmu

shine Ya Sayyadi Umar, duk da ba musan yanda Allah zaiyi nasa hukuncin bisa wannan al'amari ba, amma inaso kiyi tunani Yarima yafi k'arfinmu mu iyayenki bare ke Aynu ki tsaya a matsayinki kada ki kai kanki inda Allah bai kai kiba kinji ko?".

"Ehh Umma insha Allah zan kiyaye !".

Aynu takai maganar tana mai goge hawayen da ke bin kan fuskarta, tasan tana son Yarima Fudhal amma kuma bazata iya jayayya da umarnin mahaifiyarta ba.

***

Misalin 6:25 na yamma.

Aynu ta dubi Ummanta tana fad'in.

"Umma bari inje wajen Zainab yau duk bamu had'uba sabida banje aiki ba, kuma ina son karb'o wani littafi ne".

"To amma kinga yamma tayi ankusa sallar maghriba ki dawo da wuri kada Babanki yazo ya tarar bakya nan".

"To Umma dama ba jinawa zanyi ba, ina karb'owa zan tawo".

Ta kai maganar tana mai ficewa, ko da ta isa gidansu Zainab Mamanta bata nan sai Zainab d'in zaune tana yankan farce, Aynu tayi sallama ta shiga ta nemi guri kusa da Zainab d'in ta zauna suka fara hira.

"Kinsan kuwa amsar da Mama ta bani dana tambayeta akan maganar nan?".

Cewar Zainab kenan tana mai duban Aynu, Aynu tace.

"A'a sai kin fad'a".

Nan Zainab ta kwashe duk yanda sumai ta sanar mata, sosai kayan cikin Aynu suka juya har sai da ta nufi toilet ta fito ta nemi guri ta zauna tayi ta gumi tana fad'in.

"Ko kinsan d'azun nan Umma kemin maganar wai inyi baya-baya da Yarima su zab'insu Yasayyadi Unar ne?".

Zainab taja ajiyar zuciya tana fad'in.

"Karki damu Aynu muyita addu'a dai koma waye mijinki Allah ne masani kuma shine zai zab'a miki mijin da ya dace da ke, sannan akwai wata magana ma da zan fad'a miki".

"Ina jinki".

Aynu ta fad'a ba tare data dubi Zainab ba.

"D'azu Jakadiyya tazo tace a fad'a miki kinbar zuwa aiki sabida Mai Martaba ya bada umarnin kada ki sake zuwa !".

A firgice Aynu ta d'ago kai ta dubi Zainab.

"Me kika ce?, to mai nayi masa ?".

"Baki masa komai ba, akan d'ansa Yarima Fudhal yace kibar aiki gidan sabida ya raba ku".

Aynu tayi ajiyar zuciya tana fad'in.

"Innalillahi wa'inna ilaihi raji'un !, shikenan ta faru ta k'are".

*YARIMA FUDHAL*

Na
FIRDAUSI S.A(QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

SADAUKARWA:-Namesy:-Phirdauceey Jeebour.

WASHE GARI

"Aynu lafiya kuwa !, yau ba zaki je aikin ba ne?".

Aynu da ke kwance bisa tabarma ta d'ago kai ta dubi Ummanta ta bud'e baki a hankali zatayi magana suka jiyo ana sallama Umma ta amsa da fad'in.

"Amin wa'alaikissalam Ta Sallah shigo mana?".

Maman Zainab ta shiga d'akin, Aynu ta mik'e daga kwancen da take ta matsa waje guda domin bawa Maman zee waje ta zauna, Aynu ta gaishe da ita, ta amsa cike da fara'a kafin ta mai da kanta kan Umma tana fad'in.

"Umman Aynu !, Sai mukaji mummunan labari kuma ?".

"Labarin me fa?".

Umman Aynu ta jefawa Maman Zee tambaya mai makon amsar daya kamata ta ba ta.

Duban Aynu Maman Zee tayi tare da fad'in.

"A'a kardai kice Aynu bata fad'a miki ba?".

"Ni Aynu bata gayamin komai ba".

"Ai Mai Martaba Sarki Ubaiyd yace kada ta kuma zuwa aiki".

"Subhanallahi !, wani abun tayi musu ne?".

"A'a kan dai maganar yaronsa Yarima Fudhal da nayi miki magana jiya ne, to Jakadiyya tazo har gidana ta ba da sak'on nima bana gida lokacin Zainab ta samu, amma da Aynu taje gidan Zainab tace ta gaya mata.

Shiru d'akin yayi babu wanda ya sake furta ko kallama d'aya, sai can Umma tabud'e baki tace.

"To Allah ya kyauta daman inata kwab'ar Aynu dayi mata fad'a kancewa ta tsaya iya matsayin

da Allah ya ajiye ta, shikenan haka Allah yak'addara babu komai!".

Aynu dake zaune gefe sai tausayin mahaifiyarta ya kamata domin tasan abin da yake damun Ummanta bai wuce toshewar hanyar samun abincinsu ba yanzu.

"Umma kiyi hak'uri dan Allah...!".

"A'a Aynu ko kad'an bikimin laifi ba, sai dai ni yakamata inbaki hak'uri, ki cigaba da hak'uri tare da addu'a kan halin matsi da talaucin rayuwar da Allah ya d'ora mana kinji".

"Hakane komai ai mai wucewa ne Umman Aynu, wannan al'amarin dama sai addu'a".

Cewar Maman Zee kenan tana mai mik'ewa tsaye ta cigaba da fad'in.

"Ni zan koma, kuyi hak'uri dan Allah".

"Babu komai fa Ta Sallah karki damu".

Cewar Umma kenan, Aynu tabi ta da fad'in.

"A gaishemin da Zainab".

"To zataji insha Allah".

Maman Zee na fita Baban Aynu yayi sallama cikin d'akin nasu ya nemi guri ya zauna yana fad'in.

"Wacce magana naji kunayi kuma?".

"Wallahi wai Aynu ce suka kora daga aiki kan wannan yaron".

"Wanne Yaro kuma?".

"D'an Sarkin da yace yana sonta mana".

"Wai Fudhal ko Jaleel".

"Fudhal d'inne ko Aynu?".

Umman ta fad'a tana tambayar Aynu, Aynu tayi shiru tare da sauke kanta k'asa, Baba yayi ajiyar zuciya tare da kallon Aynun bai kuma cewa komai ba kan maganar sai tambayar da yayi kan abinci.

"Kuna da abin da zaku dafa yau ne?".

"Ehh a kwai Baba shinkafar da akayi mana rabonta a gidan Sarki ai bama muci ta ba".

"To yayi bari infita sai in tawo da kayan miya".

"To Allah ya kiyaye".

Suka bishi da addu'a dukansu.

"Umma wai me yasa Baba baya son maganar gidan Sarki ne !, kuma naga bai damu da barin aikin da nayi ba?".

"Karki soma tambaya akan wannan al'amari ke dai kiyi ta addu'a sosai kinji?, domin dama da k'yar ya amince kike aiki agidan shiyasa yanzu bai damu ba akan barin aikin".

Aynu ajiyar zuciya tayi kawai tana mai bin Ummanta da kallo kafin ta mik'e ta fita zuwa tsakar gida domin d'ora musu sanwar abinci.

***

"Komai ya rushe Anwar !, wai ya Abba yake so inyi da rayuwata ne?".

Yarima Fudhal yakai maganar yana mai goge kwallar data fiddo saman idonsa, Anwar ya dafa kafad'arsa yana fad'in.

"Hak'uri tare da addu'a sune abin da ya kamata kayi Yarima".

"Nasan da wannan amma zuciyata bazata iya d'aukan hukuncin Abba ba!".

"Na fahimci damuwarka sosai Yarima, dole zuciyarka ta damu sosai akan rabuwa da wacce take muradi, first love bak'aramin abu bane nasan zafin hakan, amma ka kwantar da hankalinka mu nemi mafita mana?".

Yarima Fudhal yayi ajiyar zuciyar tare da kora sas-sanyan juice d'in dake gabansa ya lumshe ido tare da kwantar da kai kan kujerar da yake kai, yakai kusan mintuna biyar a haka, kafin ya d'ago kai ya dubi Anwar dake zaune har lokacin yana dubansa.

"Mene mafita Anwar?".

Anwar yayi shiru nad'an lokaci yana juya cofin glass d'in dake gabansa, kafin yad'an d'aga kafad'arsa sama yana mai fad'awa kan kujera ya zauna ya fara magana.

"Mafita d'ayace zuwa biyu, yarinyar itama ai tana sonka sosai ko?".

"Fad'ema ai b'ata baki ne".

"Ok mafita kawai ka nemi yardar iyayenta, bayan komai ya kammala sai ka nemi aurenta ba tare da sanin Mai Martaba ba, sannan kada ka bijirewa dukkan nin umarninsa kayi dukkan abin da yace akan auren da yake son yi maka".

"Kana nufin in durk'usar da kaina gaban Iyayen Aynu !, daga baya intura iyayen k'arya in aureta kake nufi kome?".

"Yes ! durk'usawa wada ai ba gajiyawa bane, dole fa wannan karon ka ajiye duk kan wani girman kai da izzar mulki da kake tak'ama da shi ! ".

"Taya hakan zai kasance".

"Ok ka gane ko?, idan har ka samu soyayyar iyayenta suka amince da kai daga baya zamu san yanda zamuyi su yarda su aura maka ita ba tare da sanin mai Martaba ba, bayan lokaci duk ta hanyar da mai martaba ya dace asanar masa sai mu sanar, nasan lokacin dole yayi hak'uri ya karb'i Aynu natsayin surukarsa".

Yarima Fudhal yayi shiru yana gyad'a kai, kafin yace.

"Babu wata mafitar sai wannan?".

"A kwai mana dama nace maka hanya biyu ce ai, idan hakan bai yi maka ba, mai zai hana kasa iyayenta su aminta da kai sosai inyaso sai ka sanar dasu matsalarka ka mayar da Aynu makarantа har zuwa nan da wani lokaci sai ka samu sannu a hankali ka shawo kan mai martaba, ba dai talaka ce ba'aso ka aura ba kan lokacin ka mai dasu masu kud'i mana nasan kana da arzik'in da zaka iya hakan nima zan taimaka maka tunda Mai martaba bai tab'a ganinta ba kaga baka da matsala akai".

Yarima yamik'awa Anwar hannu suka tafa yana fad'in.

" Woww mutumina !, Kai amma shawaran tayi wallahi amma ta biyum zamu d'auka ita ce zata fi tafiya dai-dai ina ganin daga baya ma kawai incanja musu gari ko?".

"Ehh mana ai duk hakan na cikin tsarin amma kayi komai cikin iya taku fa...?".

" K'arar fad'uwar abu sukaji daga dai-dai window tare da ganin giftawar inuwar mutum daga jikin labulan da sauri sukayo waje domin ganin waye?, sai dai basu ga kowa ba kasancewar dare ne duk da hasken fitulun farfajiyar wajen hakan bai sa sunga kowa ba.

"Ashe ba kowa ma yanzu haka k'arar wani abu ne daga wani wajen".

Yarima Fudhal ya girgiza kai yana fad'in.

"A'a tabbas mutum ne, anyi mana lab'e !, to amma waye?".

"Kada ka zurfafawa kanka tunani Yarima, yanzu haka gizon wani abu muka gani".

"Mutum ne Anwar ka yarda kawai !".

"To shikenan koma waye ma tara wata rana".

Yarima Fudhal ya koma kan kujera ya zauna, Anwar ya dubeshi yana fad'in.

"Ni zan wuce gida sai gobe ma had'u ko?".

"Ok ".

Abin da yace dashi kenan sukai musabiha ya tafi.

***

Fulani Sokoto ce kushingid'e ta tayar da kai da kusum sai cika take tana batsewa, Baiwarta mai suna Larai tana durk'ushe gefe tana jiran unarninta.

"Kamar dai yanda aka saba Larai ga kud'innan dubu d'ari ki kaiwa Malam sai kuma dubu goma naki kiyi kud'in mota sauran ki rik'e".

Larai ta washe baki tana mai d'aukan ledar da kud'in yake tare da fad'in.

"Uwar Magajin gobe Allah ya nuna mana cikar wannan burin namu !".

"Amin, ki kula da kyaufa Larai ban da shirme kinji ko?".

"Insha Allah komai zai tafi kamar yanda aka tsara".

Jalila dake zaune gefe sai wani faman yatsine take tana fizgarwa, ta dubi Larai a wulak'ance.

"Sai ki tashi kije ko?".

Larai ta mik'e da sauri jiki na b'ari, Jakadiyya dake shirin shiga falon jin maganar da suke ya sanya ta tsayawa tana sauraron maganarsu duk da cewa ba yau ne karo na farko data sabajin haka ba, amma yau hankalinta ya tashi sosai domin ba ta san me suke k'ullawa ba, jin da tayi Larai na shirin fitowa yasa ta sanya kai cikin falon tare da sallama har suna d'an bangazar juna da Larai.

Jakadiyya ta durk'usa tana fad'in.

"Gani ranki ya dad'e".

Kallom wulak'anci Fulani Sokoto ta watsa mata tare da fad'in.

"Yarima Jaleel yana buk'atar sababbin 'yan aiki !".

"Amma ranki ya dad'e wata uku kenan da kawo masa wasu".

"Yace sun tsufa sabbi yake buk'ata !, ko bazai samu ba ne?".

Fulani tayi maganar cike da tsawa da b'acin rai, Jakadiyya ta durk'usa tana fad'in.

"Aimin afuwa ranki ya dad'e !, angama gobe insha Allah za'a kawosu".

Fulani Sokoto ta d'an murmusa kad'an .

"Tashi kije".

Jakadiyya tamik'e ta fice daga falon.

"Bintu...! Bintu...!!".

Fulani Bingel tahau kiran wata Baiwarta dake cikin d'aki tana gyarawa, sai gata da sauri ta fad'i agabanta tana fad'in.

"Gani ranki ya dad'e na amsa kiran ki !".

"Je ki kiramin Uwar  Soro ".

"Angama ranki ya dad'e".

Ta mik'e ta fice.

Mintuna kad'an sai gasu a tare sun shigo, Fulani Sokoto ta dubi Bintu tace.

"Je ki waje zan neme ki".

Ta mik'e ta fice.

"Bamu waje Jalila".

Jalila tamik'e tana tura baki gaba ta shige d'akinta .

Falon ya rage daga Fulani Sokoto sai Uwar Soro.

"Ya dai Uwar Soro !, kwana biyu babu labari ne?".

"Fulani kenan kedai kawai fad'i abin da ki ke buk'atar fad'i".

Fulani Sokoto tayi wani guntun murmushi kafin ta mik'e zaune daga kwancen da take.

"Ina buk'atar takun k'afar Yarima Fudhal !".

Tofa wata sabuwa !, ya kuke ganin abubuwan zasu kasance ne?.

Mafitar dasu Yarima suka nemawa kansu zatai aiki  kuwa?.

Me Fulani Sokoto kuma za tayi da takun k'afar Yarima Fudhal?".

Wanne abu Fulani Sokoto take shiri aikatawa haka?".

Sai naji comment naku masoyana

Team
AYNU-FUDHAL

Team
AYNU-JALEEL

Team
AYNU-YA SAYYADI UMAR

Da wanne kuke ganin Aynu ta dace?".

Ina jiran amsarku

ASHA KARATU LAFIYA.

*YARIMA FUDHAL*

Na
FIRDAUSI S.A (QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

SADAUKARWA:-Namesy Phirdauceey Jeebour.

23

Page d'in naki ne Munayshart tare da 'yan group naki, Allah yabar so da k'auna, ana tare har bada.

Cikin lokaci k'ank'ani Anwar da Saima sun fara sabawa da juna, duk da cewar a b'angaren Saima wani lokacin idan ta tuna da Yarima takanji kamar ta yaudari kanta ne, idan har ta sake

ta karb'i soyayyar Anwar ta mance da Yarima, hakan yasa wani lokacin take kakkauce masa, amma sai dai Anwar ya wuce dukkan tunaninta duk yanda taso ta kauce masa bata iyawa sabida salo da iya taku akan tafiyar da al'amarin soyayya na Anwar, shi kanshi yana tak'ama da hakan, shiyasa Yarima bai bawa kowa wannan aikin ba sai shi domin yasan shine kad'ai zai iya.

YAMMANCIN RANAR ALHAMIS.

Yarima ne tsaye k'ofar gidansu Aynu lokaci-lokaci yana duban k'ofar gidan tare da kallon agogon da ke sanye bisa tsintsiyar hannunsa.

Dai dai lokacin da ya sake d'ago kai ya kai dubansa k'ofar gidan ita kuma tana sanyo kai zata fito, wani sanyin dad'i ya ziyarci zuciyar Yarima har yana ji kamar yaje ya rungumeta sai dai yayi ta maza ya dake har ta k'araso zuwa gareshi fuskarta babu yabo babu fallasa sab'aninshi da yake ta faman doka murmushi har fararen hak'oransa na bayyana waje.

Sallama tayi tare da gaishe da shi, ya amsa cike da fara'a kafin shiru ya biyo baya.

Can dai ya katse shirun da fad'in.

"Kiyi hak'uri kinji?, abisa abin da ya faru !".

"Babu komai".

Ta bashi amsa, tana d'an basarwa.

"Kina son ki koma karatu?".

Da sauri Aynu ta d'ago kai baki a washe tana dubansa tare da fad'in.

"Ina so sosai wallahi !".

"Ok..! Zanyi magana da Babanki sai musan abinyi kafin zuwa lokacin kammalawarki zan san yanda zanyi inshawo kan Mai Martaba ya amince da auren mu !".

Sosai Aynu taji farin cikin jin wannan maganar, ta d'an risina tare da fad'in.

"Nagode sosai Allah ya k'ara girma da arzik'i...!".

Yarima Fudhal ya sanya ya tsansa d'aya kan leb'ansa yana fad'in.

"Shishshshsh...! bana buk'atar jin godiya daga gare ki, komai zan iya indai akan ki ne Aynu sabida ke ce mace ta farko dana fara so !, ina jinki sosai cikin raina...!".

Aynu dubansa tayi cike da murmushi kan fuskarta, take taji son Yarima da k'aunwrsa na k'ara shiga ranta har dai sanda taji yana fad'in.

"Ki gayawa Abbanki nan da kwana biyu zanzo muyi magana kan batunki da karatun da zaki koma !".

"Da gaske kake ?".

Yarima Fudhal kai kawai ya gyad'a mata tare da lumshe idanuwansa, sabida yanda Aynu ta wurk'a idonta kafin tayi masa tambayar ne ya sashi jin wani abu tun daga kwanyar kansa zuwa babban yatsansa, da k'yar ya iya bud'e baki ya bata amsa.

"Na tab'a yi miki wasa ne?".

"A'a".

Ta bashi amsa tare da mai da kanta k'asa, sabida wani irin kallo da taga yana binta da shi.

"Zo muje mota zan baki sak'o ".

Ya fad'a yana mai kafeta da idanuwa, Aynu ta d'anyi jim kad'an kafin tace.

"To".

Yayi gaba yana tafiya ta bishi a baya har zuwa bakin layinsu inda yayi parkin motarsa, ya bud'e gidan baya ya d'auko wata k'atuwar farar leda ya mik'a mata, tsayawa tayi tana dubansa ba tare data karb'a.

"Bana son musu kin sani dai".

Aynu tasa hannu tak'arba tare da fad'in.

"Nagode sosai".

Dubanta ya sakeyi tare da zira hannu cikin aljihun wandonsa ya zaro kud'i masu yawa ya mik'a mata, kai ta girgiza alamun a'a tana fad'in.

"Kabarshi iya hankama ya isa nagode sosai....!".

Katse ta yayi da fad'in.

"Wannan ba daga ni ba ne, daga Abbana ne yace a baki hak'k'in ki ne, na aikin da ki kai".

Aynu tasa hannu takarb'a tana fad'in.

"Ayimin godiya".

"Ni zan koma ki kulamin da kanki !, sai nan da jibi zan dawo, karki manta da maganarmu".

"To insha Allah bazan manta ba, kai ma ka kula da kanka".

Yarima yayi murmushin jindad'i yana mai bin bayanta da kallo har sai da tab'acewa ganinsa, sannan ya tayar da motar ya bar layin gidan ya nufi gidansu Anwar.

***

"Ranki ya dad'e, sai fa mun dage sosai akan Magaji wajen yi masa addu'a, sabida sharrin mak'iya !".

"Muna nan munayi Jakadiyya, ke dai kina ji da magaji sosai kullum maganarki bata wuce ta sa".

Jakadiyya tayi ajiyar zuciya kafin ta ce.

"Ai dole indamu da shi Hajiya, shi d'in ai abin so ne ga kowa".

Fulani Bingel tayi murmushi na jindad'in maganar da Jakadiyya keyi akan Yarima.

Sallama yayi ya shigo tare da neman waje ya zauna, yana mai gaishe da Fulani, ta amsa cike da fara'a tana dubansa, Jakadiyya ta rissina ta gaishe da shi tare da tamik'e tabar d'akin.

"Yanzu zancenka muke sai kuma gaka ka shigo".

Yarima ya d'ago kai daga daddanna wayar da ya ke tare da duban Mahaifiyartasa.

"Wai kai kullum babu abin da kake jin dad'ine da ya wuce danna waya?".

"Hajiya kenan...bazaki gane bane".

Ya bata amsa cike da murmushi, itama murmushin tayi tana fad'in.

"Taya zan gane ba'ayi min bayani ba?, daga ina kake ne haka?".

Yarima Fudhal ya dubi Mahaifiyartasa shi dai baya yi mata k'arya kuma baya so ya fara yi mata ayau.

"Naje gidansu Aynu, daga nan naje wajen Anwar".

Fulani Bingel kafe Yarima Fudhal tayi da ido cike da mamaki, domin yau karo na farko tana ganin tirjiya tare da kaucewa umarnin mahaifinsa.

"Kenan baka bar yarinyar ba?".

Yarima ajiyar zuciya yayi tare da duban Fulani Bingel yana fad'in.

"Kada kimin gurguwar fahimta, ki tayi da addu'a Hajiya, ni kaina na kasa kaucewa abin da zuciyata take so, na rasa yanda zanyi incire yarinyar a raina ne".

"Karka damu na fahimci damuwar da ka ke ciki, zan tayaka addu'a sosai insha Allahu kaima ka dage da addu'a kaji?".

"To Hajiya ina nan inayi dama".

"Amma Hajiya Aynu taban tausayi sosai wallahi duk sai naga ta rame, kawai na yanke shawaran mai da ita makaranta inyaso ki tayani shawo kan Mai Martaba !".

A jiyar zuciya Fulani tayi tana fad'in.

"Ka san halin Mahaifinku dai al'amarinsa sai dai addu'a Magaji, amma zanyi k'ok'arin ganin na shawo kan nasa".

"Yauwa Hajiyata !, haka ya kamata ki fad'a ai tun da farko, Allah yak'ara girma".

"Amin".

Ya kwanta bisa cinyarta, d'an bugun bayansa tayi tana fad'in.

"Wai kai yaushe zaka girma ne ?, kai da ake shirin yiwa aure !".

Fudhal yayi dariya yace.

"Ai a gunki bazan girma ba Hajiya, tunda nine auta !,, kinga ai dole kiji dani".

Fulani ta tureshi tana fad'in.

"Yau dai ka girma agun nawa".

Yarima ya zauna yana fad'in.

"Wai ina Aunty Sadiyya ta shige ne?, kwana biyu bata zuwa?".

"Ina zata zo?, tana fama da jikinta, ta kusa haihuwa fa, kai dai kam Allah ya shiryamin kai baka son zumunci ko kad'an tun da ka dawo babu gidan wacce ka taka bare har ka zaga dangi".

"Ayya Hajiya karki damu zanje ne insha Allah, kinsan tun da nadawo busy nake ne".

"To naji amma gobe kaje ka dubota".

"Allah ya kaimu goben lafiya".

"Amin".

***

Ya Sayyadi Umar ya durk'usa ya gaishe da Umma, ta amsa cike da fara'a tana fad'in.

"Munata ganin abubuwan alkhairi mungode sosai, Allah k'ara bud'i".

"Amin, Babu komai Umma, karku damu, Baba baya nan kenan?".

"Ehh bai shigo ba tukun".

"A gaishe dashi ni zan koma".

"Zaiji insha Allah, Allah kiyaye mungode sosai".

Ya mik'e ya fita, Aynu ta bi bayansa har zuwa k'ofar gida inda ya tsaya yana jiranta.

Dubanta yayi kafin yace.

"Har yanzu kink'i sakin jiki dani !, ko wani abun ke damun ki?".

"A'a babu komai".

Tayi maganar kanta ak'asa.

"Ina ganin kamar ya kamata inturo iyayena ayi magana ko?, domin zance babu tsayay-yiyar magana bata da amfani".

Dammm gaban Aynu ya buga, tuni yanayinta ya sauya har Ya Sayyai Umar yaso fahimtar

hakan.

"Yadai ko bakyaso inturo yanzu?".

"A'a kawai gani nayi zaifi dacewa ka bari ad'an k'ara kwana biyu".

Ya Sayyadi Umar yayi shiru nad'an wani lokaci kafin yace.

"Babu damuwa !, Allah ya kaimu lokacin ni zan koma ankusa kiran sallah ki gaida Baba idan ya dawo".

"Zai ji insha Allah".

Ta fad'a tana mai juyawa ta koma cikin gidan tabarshi nan tsaye.

BAYAM SALLAR MAGHRIBA...!

Baban Aynu ne zaune bisa tabarma yana cin abinci, Umma na daga gefansa, Aynu na waje d'aya a zaune, sai sak'a take tana warwarewa a cikin ranta, tana son sanarwa iyayen nata maganar Yarima Fudhal amma ta kasa tana jin nauyi sosai.

Har Baban nata ya kammala cin abincin ya wanke hannu tare da alwala yana fad'in.

"Zanje masallaci ankusa shiga sallah".

"Adawo lafiya".

Suka had'a baki da Ummanta wajen fad'i.

Sai bayan fitarsa Aynu ta matsa wajen Ummanta tana fad'in.

"Umma dama wata magana nake son fad'a miki".

"To inajinki Aynu".

Aynu ta d'anyi shiru kafin tace.

"Umma dama...! dama..!! dama !!!".

"Dama me?, kiyi magana mana Aynu".

"Dama Yarima ne yace wai...".

Sai kuma tayi shiru.

"Yace me Aynu?, fad'i ina jinki".

"Cewa yayi fa wai jibi zai zo  wajen Baba suyi magana, wai za biyamin inkoma makaranta !".

Umma shiru tayi na zuwa wani lokaci, Aynu kuwa ta zuba mata ido tana jiran taji abin da zata ce.

"To Allah ya kaimu !, zan gayawa Baban naki".

Umma tayi maganar asanyaye, kamar akwai wani abu ak'asan ranta.

Ita dai Aynu bata ce komai ba illa.

"Amin".

Data furta kawai, acan k'asan ranta kuwa farin ciki ne fal wanda ba zai fad'uba,  tamik'e ta d'auro alawala domim gabatar da sallar isha'i.

*YARIMA FUDHAL*

Na
FIRDAUSI S.A (QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

SADAUKARWA:-Namesy Phirdauceey Jeebour.

24

*BAYAN KWANA BIYU*

Yarima Fudhal ne tare da Anwar tsaye jikin k'ofar gidansu Aynu, Anwar sai bin gidan yake da kallo Yarima kuwa kansa na bisa screen d'in wayarsa yana dad-dannawa, fitowar Aynu daga

cikin gidan shine ya sanyashi mai da wayar cikin aljihun wandonsa yana binta da kallo.

Ta k'araso inda suke tsaye tare da gaishesu tana fad'in.

"Baba yana ciki !, ku shigo mana?".

Ta juya zuwa cikin gidan suka take mata baya, da sallama suka sanya kai cikin gidan, yaune karo na farkon shigar Yarima gidansu Aynu.

Ummanta na zaune gefe kan kujera da sandarta agefanta, Babanta shima na waje d'aya kan tabarma, sai wata tabarma ba kowa akai ita ce akayiwa su Yarima nuni da su zauna.

Aynu kuwa tuni ta wuce can k'uryar d'aji ta baza kunnuwa, k'asan zuciyarta kuwa cike ya ke da fargaba data rasa dalilin sa.

Zama sukayi tare da gaishe da iyayen Aynu, Yarima ya sake duban Baban nata karo na biyu a zuciyarsa yana tunanin kamar ya tab'a saninsa, sai dai yana so ya tuna amma ya kasa tunawa.

"Aynu ta gayamin kan cewa zaka zo muyi wata magana !, to yanzu gashi Allah ya kawomu, ina jinku mai ke tafe da ku?".

Baban Aynu ya katse Yarima daga dogon tunanin daya fad'a, Anwar ya gyara zama yana fad'in.

"Baba munzo ne kan maganar 'yarka Aynu !, Yarima Fudhal ya ganta yana kuma son ta !, sai dai ya yanke hukuncin zai mai da ita makaranta domin cigabanku da rayuwarta kafin zuwan lokacin da iyaye zasu shiga tsakanin maganar !".

Baban Aynu ya gyad'a kai cike da gamsuwa da maganar Anwar, kafin ya mai da kansa kan Yarima Fudhal yana binsa da kallo cike da nazarin yanayinsa, Baban Aynu yayi murmushi na wani lokaci kafin yace.

"Yaro ya sunanka?".

"Anwar, shi kuma Yarima Fudhal d'an Sarki Ubaiyd, nasan zaka sanshi ai?".

"Kwarai kuwa ni nasan Fudhal !, inajin duk cikar garinnan akwai wanda zai kai ni sanin waye Yarima Fudhal?".

Anwar ya dubi Baban Aynu cike da mamakin jin maganar da yayi, shima kansa Yarima Fudhal kallonsa yake yayin da gefe guda kuma zuciyarsa sai bugun uku-uku take.

Baban Aynu ya cigaba da fad'in.

"Naji duk kan abin da kuka zo dashi sai dai ina mai baku hak'uri abisa maganar da zanyi yanzu".

Shiru ya biyo baya na wani lokaci, yayin da Anwar da Yarima suke jiran suji abin da zai ce.

"Na riga nayiwa Aynu miji !, kayi hak'uri nagode sosai abisa taimakon da kukayi niyar yi mana !".

Zuciyar Yarima tsananta bugu tayi lokaci guda yaji kasala da mutuwar jiki sun ziyarce shi, Anwar ya dubi halin da abokin nasa ya shiga, ya mai da kai kan Baban Aynu ya bud'e baki zai yi magana Baban Aynu ya da katar da shi tare da fad'in.

"Kuyi hak'uri kawai !".

Aynu dake tsaye cikin d'aki tana sauraronsu ta zube k'asa zaune tana share kwallar dake shirin zuba kan fuskarta.

"Baba muna baka hak'uri muma !, amma naga ai bakayi mata baiko da kowa ba, ka taimaka Baba abokina nasonta sosai wallahi !".

"Nasan da hakan !, amma kusan wani abu guda d'aya ko da ban yiwa Aynu baiko ba, nariga na gama magana bazan canja ba, ko da ace babu wanda nayiwa alk'awarin aurawa Aynu bazan tab'a yarda Aynu ta auri Fudhal ba !".

Cike da firgici Yarima Fudhal ya d'ago kai ya dubi Baban nata yana fad'in.

"Me yasa Baba ?, kataimaka kada ka yimin yankan k'auna dan Allah kayarda ka bani Aynu!".

"Sai yanzu kasan da haka Fudhal !, ni nasan ba zan tab'a yi maka yankan k'aunar da ka yimin ba !, shin zaka iya tuna MALAM ABDALLAH, Tsohon malamin makarantar primary mai ritaya ?".

Yarima Fudhal fiddo ido yayi waje yana duban Baban Aynu take hawaye ya fara zarya bisa fuskarsa, wani abu yaji na fizgar zuciyarsa ya mik'e da sauri ya dubi Anwar ba tare da ya ce komai ba yayi hanyar waje.

Anwar ya biyo shi da sauri yana kiran sunansa amma bai kulashi ba, har ya shiga mota ya zauna ya jingina da kujerar maotar yana mai kwantar da kansa, idanuwansa ya lumshe take hawaye suka fara zarya kan fuskarsa.

Anwar ya k'araso da gudu ganin halin da Yarima ya shiga yasan yashi tsayawa turus yana dubansa, tare da bud'e murfin motar ya shiga mazaunin driver ya zauna, yana mai dafa kafad'ar Yarima.

Yarima ya bud'e ido a hankalin yana duban Anwar tare da bud'e baki yace.

"Shikenan yanzu ya zama dole inbar Aynu !, Anwar rabuwata da Aynu tamkar rabuwa da rayuwata ne, zuciyata zafi Anwar!".

Tausayin Yarima ya kama Anwar sai yake ji kaman shima zaiyi kukan da k'yar yayi k'arfin halin fad'in.

"Kai ne kab'ata komai ai, mai makon kabari mushawo kansa mu bashi hak'uri sai kawai ka tashi ka fito !".

Yarima yayi murmushin da yafi kuka ciwo tare da duban Anwar.

"Bazai tab'a hak'ura ba !, ka sani yana son yayi amfani da wannan damar ne kawai wajen d'aukar fansarsa a kai na!".

"Kamarya kenan!, ban fahimce kaba ?".

"Malam Abdallah, tsohon malamin makarantar primary ba kowa bane illa mahaifin Aynu !".

"To amma wani abu ya tab'a had'aku ne?".

Yarima ya dubi Anwar natsayin lokaci batare da ya bashi amsar tambayar da yake yi masa ba.

"Muje gida Anwar insha magani zuciyata zafi ".

Anwar bai kuma cewa komai ba ya tada mota suka bar layin gidansu Aynu zuwa gida.

***

"Ka da kace min kana son d'aukan fansar abin da yafaru ne tsayin shekaru?".

"Ko kusa Umman Aynu, bana da burin fansa cikin rai na !, kawai ina son yin amfani sa wannan damar ne wajen mai da Fudhal cikakken mutum domin shi har yanzu bai san waye shi ba?, sabida shi duk da tarin shekarunsa amma bai cika mutum ba !, har yanzu yana matsayin rabin mutum ne !, ina son in nuna masa muhimmancin mutum da darajar da d'an adam yake da shi a wajen Allah da cikin dukkan halittu !, inaso in nuna masa abin da mahaifinsa ya kamata ace ya nuna masa tsayin shekaru amma ya gaza yin  hakan !, ka da ki yiwa maganata gurguwar fahimta domin kinfi kowa sanin mai ya faru?, taya zan yarda Aynu tayi aure a gidan da basu san darajar d'an adam ba?".

"Kina tunanin sarki Ubaiyd zai yarda Fudhal ya auri 'yar talaka ne?, shima kanshi Fudhal d'in da abu biyu yazo wajena a yanzu, nasan abin da shi kanshi Fudhal d'in bai san nasani ba, haka kawai Fudhal bazai k'ask'antar da kansa a garemu ba !, da a ce ya zomin a cikakken mutum  da fuska d'aya da bazan tab'a ta da abin da ya riga da ya wuce tsayin shekaru ba, sai dai ya zomin da fuska biyu ne ba akan gaskiyarsa ya zomin nan ba !, nariga da nasan wannan tun ba yanzu ba, kawai addu'a ce taki cikin wannan al'amari domin bamusan abin da Allah ya riga ya b'oye ba !, sannan kuma kada ki sa damuwar wannan abin da ya faru aranki dan Allah kinji?".

Umman Aynu kai kawai ta gyad'a tare da fad'in.

"To, Allah ya shige mana gaba".

"Amin, ni zan fita, sai zuwa anjima zan dawo".

"Allah kiyaye a dawo lafiya".

"Amin".

Yana fita Aynu dake cikin d'aki ta fito da gudu ta fad'a kan cinyar Ummanta tana mai rushewa da kuka mai cin rai.

Ummanta d'an bubbuga bayanta tayi tana fad'in.

"Kiyi hak'uri Aynu ka da kisa abun aranki kinji?, komai zai wuce da yardar Allah".

Aynu ta d'ago ja jayen idanuwanta ta dubi Ummanta tana fad'in.

"Amma Umma mai ya sa Baba ya yanke hukuncin tauyemin hak'k'ina?, ina son inyi karatu sosai Umma ki fahimtar da Baba mana!".

"Aynu ki sani ni bani da abin cewa cikin wannan al'amarin ban da addu'a kaman yanda mahaifinki ya fad'a, yanzu babu abin da zai fahimta kome zan fad'a masa, sai dai ina mamakin canjawar Malam lokaci d'aya haka ban sanshi da rik'o ba !, amma koma dai mene nasan akwai wani babban dalilin da ya sanya mahaifinki yanke wannan tsats-tsauran hukuncin kamar yan da ya fad'a?".

"Amma Umma wanne abu ne ya faru tsayin shekaru haka da yake shirin zamowa silar wargajewar farin ciki na?, ki sanar dani Umma!".

"Babu abin da zan fad'a miki Aynu !, amma ki sani kada ki k'ullaci Mahaifinki domin shine yayi silar zuwanki duniya yana da ikon da zai yanke ko wanne irin hukunci akan ki...!".

"Amma Umma.....!".

"A'a Aynu kada ki sake furta komai akan wannan maganar kinji, kibi umarnin mahaifinki!".

Umma takatse Aynu daga maganar da take son yi.

Aynu ta mai da kanta kan cinyar Ummanta tana mai goge kwallar dake zuba bisa fuskarta lokaci-lokaci.

*YARIMA FUDHAL*

Na
FIRDAUSI S.A (QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

SADAUKARWA:-Namesy Phirdauceey Jeebour.

25

Cikin lokaci k'ank'ani Aynu ta fita haiyacinta sosai ta rame ba ta da walwala ko kad'an, ita kanta bata san tana son Yarima Fudhal sosai haka ba sai da yayi mata nisa, dan ma Zainab a kullum tana k'ok'arin ganin ta d'ebe mata kewa, Babanta kuwa yanzu bai fiye shiga harkarta ba sosai shiyasa abun ya had'u yayi mata yawa, b'angaren Ummanta kuwa kullum lallashi ne nata tana tausayawa rayuwar 'yarta sosai to amma bata da abin da zatayi da ya wuce add'a.

To shima Yarima Fudhal a nasa b'an garen haka abin ya ke, shi zama a iyacewa abin nasa ya zarce na Aynu domin cikin kwana biyu da faruwar al'amarin sabida sanya damuwa da yayi da yawa a ransa abin har ya kai shi da kwanciya.

Anwar ne zaune gefan katifar da Yarima Fudhal ke kwance yata lallashinsa akan ya daure ya sha ko da ruwan tea ne amma ya yi banza da shi domin ji yake baya sha'awar komai anan cikin duniyar nan.

Turo k'ofa akayi tare da sallama Fulani Bingel ce ta shigo tare da ma'aikatanta su biyu na biye da ita, daga gefe guda kuma Aunty Sadiya ce da tsohon cikinta sai Aunty Sa'ida kuma da ta keta cika tana batsewa.

Suka zauna kusa da shi Anwar ya gaishe da su ya mik'e ya koma falo domin ya basu waje, Fulani ta dafa goshin Yarima tana fad'in.

"Haba Magaji !, jibi yanda duk ka lalace kaman ba kai ba?, ya kake so ka sanya rayuwarka cikin tsaka mai wuya ne?".

Yarima ya dubi Mahaifiyartasu hawaye nabin gefen idonsa bai damu daya share ba haka kuma bai iya cewa da ita komai ba, tasa hannu ta goge masa tana mai cigaba da fad'in.

"Kayi k'ok'arin cire wa kanka damuwa da yawa haka kaji?, kada ka jawa kanka wani ciwo na daban".

Sai lokacin Yarima ya saki wani guntun murmushi ta gefan fuskarsa, amma har lokacin bai furta komai ba kamar yanda hawayen bai bar zuba bisa pillown da yake kai ba.

Aunty Sadiya ta nisa tare da fad'in.

"Hajiya al'amarin Magaji sai addu'a wallahi !, amma ka daure dan Allah karage yawan damuwar da kake sanyawa kanka, addu'a ita ce mafita wata rana sai labari!".

"Mtsww kema dai Aunty Sadiya !, wallahi dan yaga kawai ana lallab'ashi ne, amma kaman Magaji ace sai angaya masa abin da ya dace da wanda ba dace ba, Doctor ne shi fa yafimu sanin abin da damuwar zataje ta jawo masa!".

Cewar Aunty Sa'ida kenan, tayi maganar cike da fushi da b'acin rai, Yarima ya jawo hannunsa ahankali yana mai kama hannunta yarik'e gam, fuskarsa har lokacin da murmushi samanta, sai kuma jikinta yayi sanyi k'alau ta janye hannun tamik'e ta fice daga d'akin tana goge kwallar data kawo mata domin ya bata tausayi sosai a wannan lokacin.

"Kayi hak'uri Allah ya baka lafiya, zamu cigaba da tausar Mai Martaba insha Allahu  komai zai dai-dai ta kaji?".

Yarima ya gyad'a kai, Fulani ta d'auki kofin tea d'in ta mik'a masa, ya mik'e ya zauna yana mai karb'an kofin ya fara shan tea d'in a hankali.

"Ni zan koma Magaji ka cigaba da hak'uri kaji?".

"To nagode sosai".

Ya furta yana mai kallonta, itama shid'in take kallo kafin ta mik'e da k'yar tana takawa tabar d'akin.

Fulani ta bita da kallo kafin ta dawo da kallonta kan Yarima tana fad'in.

"Allah Sarki Sadiya Allah dai ya sauke ta lafiya, cikin nan yana d'an bata wahala sosai, amma sabida k'arfin hali tun da akace mata kana kwance ta tada hankalinta sai tazo ta ganka".

Yarima yayi murmushi har cikin ransa yana son Yayar tasa, domin itama tana k'aunarsa sosai gata da sanyin rai da hak'uri, kusan ince baki d'aya ita ta d'auko halin Fulani Bingel.

Ajiye kofin yayi ya koma ya kwanta abinsa, Fulani ta lullub'e shi da bargo tana fad'in.

"Ka kwanta ka huta, zuwa anjima zan dawo kaji?".

Ya gyad'a mata kai ta fice daga d'akin, afalo ta samu Anwar tana fad'in.

"Sannunka da k'ok'ari Anwar mungode sosai Allah yabar zumunci".

"Amin Hajiya babu komai".

Ta juya tabar d'akin, shi kuma ya mik'e ya koma wajen Yarima, ya nemi guri ya zauna, Yarima ya mik'e zaune shima yana duban Anwar ba tare da yace komai ba, amma da dukkan alamu so yake yayi magana.

Da k'yar dai ya bud'e baki yana fad'in.

"Kana ta tambayata kan abin da ya had'ani da mahaifin Aynu ko?, zan sanar dakai yanzu insha Allahu!".

***

Baban Aynu ne zaune bisa tabarma a tsakar gida, gefe guda kuma Umman Aynun ce zaune suna hira, yayin da Aynu keta shige da fice tana aikace-aikacen data saba duk da cewa bata wal-wala amma hakan bai hanata yin abin da ta saba ba acikin gidan.

Baba ya dubi 'yar tasa ta ba shi tausayi sosai, kiran sunanta yayi tare da fad'in.

"Zo nan Aynu".

Aynu tazo ta durk'usa tana fad'in.

"Gani Baba".

"Kin sa kanki a damuwa sosai Aynu !, kada ki d'auki fushi ki d'ora kan mahaifinki Aynu, ban so ki san wannan labari ba amma yau yazama dole infad'a miki, domin ki yanke hukunci da kanki akan barin soyayyar Yarima ko cigaba da son sa!".

Baban ya d'anyi shiru na wani lokaci kafin ya cigaba da fadin.

SHEKARU GOMA SHA SHIDA DA SUKA WUCE....!

"Ni na kasance haifaf-fan k'asar senegal ne, na taso cikin dangi da abokai tsayin shekaru nayi karatu na duk a can senegal d'in, sanadiyyar barin k'asata kuwa wata annoba ce ta addabi garin da muke ciki, an rasa rayuka sosai a lokacin ciki har da iyayena da 'yan uwana, kuma lokacin

anrasa maganin wannan annoba data saukar mana, hakan ya saka gwannati ta bada jirgi domin d'ebo raguwar mutanan da suka rage a cikin garin zuwa duk k'asar da muke so, domin tsiarar da rayuwarmu, ni dai alokacin na zab'i Nigeria domin nakanji Mahafina yana yawan bada labari akan k'asar wajen kasuwanci saboda yasha zuwa yana komawa domin kasuwancinsa".

"Nazo Nigeri bani da kowa haka kuma bansan kowa ba, na sauka a gurin dagacin wata unguwa wanda shine mahaifi ga Ummanki ya rik'e ni da amana da gaskiya har dai dana basu labarina da abin da ya kawo ni k'asar nan, kasancewar nayi karatu shine ya samamin aikin koyarwa a makarantar MAI TASA PRIMARY SCHOOL".

"Cikin ikon Allah suka d'auke ni, da albashin da nake d'auka nake temaka mana muna ci da kanmu kasancewar na samesu suma bawani hali garesu ba sai dai rufin asirin Allah, shima kamar ni yake bashi da kowa sai Ummanki ita kad'aice 'yarsu, bayan wani lokaci mai tsayi suka yanke hukuncin aura mun ita, bayan aure da shekara guda sukayi gobara da dare duk suka k'one a cikin dak'i, munyi kuka sosai domin munrasa wanda suke uwa da uba a garemu bayansu ba mu da kowa a duniyar nan".

"Haka mukayi hak'uri muka dan gana, ki sani Aynu ba ke kad'aice 'yarmu ba, kafin ki akawai Yayanki mai suna Muhammad Shadad !".

Aynu ta share kwallar dake idonta tana murmushi farin ciki fal ranta taji ance tana da yaya, cike da d'oki ta fara fad'in.

"Ina da Yaya Baba!, Ina yake to?".

Baba yayi shiru na wani lokaci cike da tausayaa Aynu kafin ya cigaba da fad'in.

"Bayan rasuwar su Malam ashe Ummanki na da ciki, bayan wasu watanni ta haifi d'a namiji, mun raineshi cikin so da k'auna, har zuwa samuwar cikin ki bayan shekaru uku, Shadad na da shekaru uku a duniya aka haifeki, yaron na sonki sosai kamar yanda muke sonku dukanku, domin ku kad'aine kuka zamto duniyarmu".

"Har lokacin dai ina aikin koyarwa lokacin na sanya Shadad a makarantar primary d'in, tare muke tafiya da shi idan antaso mu dawo tare, har Yayanki ya kai kimanin shekaru biyar a duniya yayin da kike da shekaru biyu ke kuma".

WATA RANA

"Rana ce da ta zamto silar rugujewar dukkan wani farin cikinmu !, rana ce da ta zamto sanadiyyar zamowarmu haka ayanzu, ranace da ba zamu tab'a mancewa da wanzuwarta a garemu ba har abada !, a ranar antaso daga makaranta kenan ina janye da hannun Shadad a wannan lokaci domin tsallaka titi, a wanna lokacin wata mota ta kawo kai kan titi mu kuma mun riga da mun kai tsakiyar titin kafin inyi wani yunk'uri motar tayi gaba da mu, na fad'i k'asa tayar motar tabi takan k'afata yayin da Shadad akan idona yayi sama ya fad'o k'asa a wannan lokacin ko shurawa baiyi ba yace ga garenku nan!".

Aynu ido ta fiddo waje cike da hawaye tana fad'in.

"Ya mutu kenan Umma?".

Umma ta gyad'a mata kai tana mai share kwallar da ke zuba bisa fuskarta itama.

"Naga dai yaron da ke tuk'a motar amma alokacin bansan waye shi ba?, kuma bansan ko d'an gidan waye ba?, jama'ar gurin ne suka d'aukeni zuwa asibiti, yayin da wasu suka nufi gidana domin sanarwa Umman ki, a lokacin wani mutum ya raka Ummanki gidan yaron da yake tuk'a motar ba kowa bane ashe Fudhal ne lokacin baifi shekara goma sha biyar ba a duniya !".

"Mutumin da ya yiwa Ummanki rakiya zuwa fada kuwa mahaifin Zainab k'awar ki ne !, da zuwansu sun ba da bayanin dukkan abin da ya faru amma kuma sai me ya biyo baya?".

"Sarki Ubaiyd ya rufe ido yace shi sam d'anshi bai aikata ba yaushema ya iya mota har da zai tuk'a?, yaje yayi wannan d'anyan aiki wai basu dai gani da kyau ba".

"Ummman ki tayi kuka alokacin ta rok'eshi ko da ba zai yar da d'ansa bane to ya taimaka sai cewa yayi da dai a ce neman taimakon suka zo kai tsaye zai taimaka, amma tunda sun fara neman d'ansa da sharri babu abin da zai yi musu".

"Haka suka taso suka tawo, ni kuma ina kwance a asibiti ana jiran a kawo kud'in aiki kimanin dubu d'ari domin amin aiki, sai dai a ina zamu samu wannan kud'in ?, mu da bamu ajiye ba bamu bada ajiya ba?".

"Sai da na kwana uku a kwance ahaka da k'afa a karye tun tana zub da jini ta daina ta kumbura likitoci sunce ba zasu tab'a ni ba sai anbada kud'i, bayan kwana uku kuma a kace ai k'afar ta

rub'e sai dai ayanke, haka Ummanki ta sai da gidan mahafinta dubu ashirin,  Baban Zainab ya taimaka da dubu goma da ya sai da ragunansa guda biyu ya bayar ta cika takai kud'i dubu talatin aka yanke min k'afata, wannan shine asalin rasa k'afata guda d'aya, kuma shine dalilin rasa aikina da nayi, domin sunce taya mai k'afa d'aya zai iya aikin koyarwa?, tun da aka koreni ban kuma samun wani aiki da zanyi ba duk inda naje sai ace baza'a d'auki wanda ya nakasa ba!".

"Bayan wannan abu da ya samemu kuma Ummanki ba ta da aiki kullum sai kuka sabida duk sana'ar data kama sai ta lalace, muka shiga k'angin rayuwa gidansu Zainab ne kawai suke temaka mana da abinci kullum har sai da muka shekara biyu a haka, sabida yawan damuwa da Ummanki ta sanyawa ranta ya haifa mata da hawan jini shine yayi sanadiyar rasa idonta sabida rashin mgani da kuma samun abinci mai kyau, lokacin kina da shekaru uku da rabi, nine na dinga kula da ke a wannna lokaci sabida Umman ki bata da idon da zata iya kula dake har zuwa sanda ki ka kai shekaru hud'u na sanya ki makarantar primary har zuwa sanda ki ka kai shekaru goma a duniya cikin rufin a sirin Allah, a lokacin kuma aka tsananta karatun domin duk team ana buk'atar a biya d'ari takwas mu kuwa bamu da ita bare dalilinta, domin fafutukar abin da zamu cima ta ishemu, wannan shine silar barin karatun ki, ki ka dawo zaman gida sai islamiyya, kulawarki ta koma hannuki kafin ki kai shekaru goma sha biyar kin iya komai har sai aikin gidan da komai ya koma hannunki har zuwa yanzu".

"Wannan shine ta k'ai taccen abin da ya faru ga  rayuwarmu baki d'aya, yanzu hukunci ya rage naki na gaya miki ne domin ki daina ganin laifina cikin wannan al'amari".

*YARIMA FUDHAL*

Na
FIRDAUSI S.A(QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

SADAUKARWA:-Namesy Phirdauceey Jeebour

Shiru ne ya biyo baya illa shash-shek'ar kukan Aynu da ke ta shi, Ummanta keta aikin lallashinta kafin Baban yace.

"Kuma ni duk ba wannan ne abin da yasa na yanke wa Fudhal wannan hukuncin ba, kafin yace zai zo gidan nan da kwana biyu wani saurayi yaje ya same ni a zaune a bakin kasuwa ya kira ni bayan mun gaisa yake fad'amin cewa....!".

"Ya zo ne wajena da muhimmin abu, abin kuwa shi ne ya kunnamin a cikin wayarsa muryar Yarima ce sosai da abokin nan nasa suna tattaunawa ne a bisa yanda za suyi su shawo kanmu ta hanyar yaudara".

"Babu abin da yafi d'auremin kai, sai shawaran da suka yanke na cewar zasu sanya Aynu makaranta, sannan zai nemi soyayyarmu daga baya kuma zasu mai da mu masu kud'i...!, wato Ummun Aynu ki fahimci wani abu guda d'aya, da yawan al'ummarmu na yanzu muna mancewa da Allah a cikin dukkan al'amarinmu, shin su Yarima sun mance cewa babu wani mai azurtawa sai Allah?, kuma babu mai talautawa sai Allah!, abin ya d'auremin kai sosai wannan dalilin ya sanya na yankewa Yarima wannan hukuncin amma ba wai dan BURIN FANSA ba..!"

Aynu ta mik'e ta shige d'aki da gudu ta durk'ushe a k'asa tana rusar kuka, kafin ta share hawayenta daga baya tana ganin meye amfanin zub da hawaye akan wanda bai cancanta ba?, a yau ta yanke duk wata damuwa da hawaye indai akan Yarima ne.....!.

SHIN HAKAN ZAI YIYU KUWA?.

***

Yarima ya dubi Anwar yana mai cigaba da fad'in.

"Ko kad'an bani da laifi akan duk kan abubuwan da suka faru Anwar!, tabbas nasan na d'auki mota na fita a wannan rana sai dai ban san yanda akai hakan ta faru ba duk iya k'ok'arin da nayi domin take burki a lokacin gagara yayi ashe burkin ya samu matsala ne?, ban sani ba Allah ne kai ya kai ni gida a lokacin cikin ta shin hankali da tsoro....".

"Tabbas babu wani bawa da zai iya kaucewa k'addararsa komai k'ank'antarta domin ita

k'addarar mutum a rubuce take tun gabanin zuwansa duniya, Anwar Mahaifina shine ummul-aba isin haddasa dukkan a bubuwan daya faru, a ranar da abin ya faru nazo gida cikin rud'u da tsoro fuskantar hakan da Mai Martaba yayi ne kuma yaji dukkan abin da ya faru sabida son da yakemin sai yak'i yarda da abin da aka ce na aikata !, a lokacin nayi k'ok'arin zuwa fada domin in tabbatar da abin da ya faru alokacin da iyayen Aynu suka zo, sai dai Mai Martaba ya sanya aka tsare ni aka hanani zuwa ko ina, a washe garin ranar ya nema min visa da komai domin barin k'asata da kowa a cewarsa kafin dawowata an mance da komai nima kuma na mance, amma bai san hakan babbar matsala ya jawomin ba, sabida ni kai na tun da naje k'asar tsayin shekaru goma sha shida kenan abin yana raina wallahi Anwar k'arshema sanadin hakan ne ya jawomin ciwon zuciya..!".

"What...!, ciwon zuciya fa kace?".

"Yes...kana mamaki ne?".

Anwar mik'ewa yayi a rud'e ya fara duba magungunan da Yarima kesha domin bai tab'a dubawa ba bare har yasan abin da yake damunsa.

"Ban da kai a yanzu nan gida babu wanda yasan abin da yake damuna sai doctor Mansur da ya zo ya duba ni farkon dawowata time d'in da nayi fama da fever shima na rok'eshi kada ya sanarwa kowa kuma bai fad'a d'in ba".

Shiru ne ya biyo baya kowa yana tunani a cikin zuciyarsa, can Anwar ya nisa tare da duban Yarima.

"Kayi hak'uri komai zai wuce insha Allahu !, zanyi k'ok'ari wajen shawo kan Mahaifin Aynu !, tun da ai abisa kuskure abubuwan suka faru ina ganin idan yasan gaskiya zai sauko !".

Yarima ya dubi Anwar kamar zai ce wani abu sai ya fasa, ya mai da kai kawai bisa katifa ya kwanta.

***

"Me ki kace Aynu !, ki na so ki cemin Yarima Fudhal ne yayi sanadin mutuwar yayanki?, yayi sanadiyyar rasa k'afar Baba tare da rasa idon Umma?".

"Ehh haka ne Zainab!, nima ajiya nasan wannan al'amarin".

Zainab tayi shiru tana duban Ayn cike da tausayawa, kafin ta dafa kafad'arta.

"Kenan ya zama dole ki rabu da Yarima kenan?, ko badan hakan bama iyayenku basa son had'in?".

"Ehh".

"Bani da abincewa daya wuce addu'a Aynu, Allah yayi maki zab'i mafi alkhairi!".

"Amin summa amin".

Aynu ta fad'a tana mai share kwallar da ta taru cikin idonta.

***

"Ina son ganin Aynu !, Anwar dan Allah ka raka ni!".

"Kana son ganin Aynu kuma Fudhal?".

"Ehh haka nace".

"Amma taya zaka ga Aynu yanzu a cikin wannan halin, kuma da dare haka?, ka da ka mance da a bubuwan da suke faru wa ?".

"Na sani Anwar amma ko ta wanne hali inason ganinta !, dan Allah muje ka raka ni Allah idan ban ganta a yau ba zan shiga wani hali....!".

"In baza kaba kaga tafiyata".

Yarima Fudhal ya mik'e cike da k'arfin hali ya zari key d'in mota zai fita bai ko damu da yanayin jikinsa ba.

Ganin da Anwar yayi tabbasa da gaske tafiya zai yi, kuma a cikin halin da yake ciki, shi yasa Anwar ya mik'e da sauri ya bi bayansa tare da kiran sunansa.

Tafe suke a mota Anwar ne ke driven d'insu babu mai cewa da wani komai, har suka isa

unguwarsu Aynu Anwar yayi parking dai-dai layin gidan nasu, Yarima har ya riga Anwar fitowa sai da Anwar ya d'an taka da gudu kafin ya taddashi yana fad'in.

"Wai kai lafiyarka kuwa?".

Yarima bai ko kalleshi ba bare ya kulashi.

Tsaye take k'ofar gidan nasu tare da Ya Sayyadi Umar suna hira, galabin hiran shine domin Aynu daga uhmmmm sai uhm-uhmm abin da take furtawa kenan domin ko kad'an hiran ba tayi mata dad'i, Allah-Allah takema taji yace zai tafi.

Tana wannan halinne taji k'irjinta ya tsananta bugu da sauri, k'amshin turarensa taji ya daki hancinta kamar ance ta d'ago kanta, tana d'agowa suka had'a ido duk da garin da d'an duhu amma akwai hasken farin wata, a tare zuciyoyinsu suka buga lokaci guda Aynu ta mai da kanta k'asa da sauri ba tare data sake marmarin sake kallon inda yake ba!.

Ya Sayyadi Umar ne ya lura da cewa wajenta suka zo, kuma ya gane Yarima ne ya dubi Aynu yana fad'in.

"Zo muje mu gaisa da alamu wajenki ya zo?".

"Kaje kawai ni babu inda zanje!".

"A'a kada kiyi haka Aynu bak'onka fa Annabinka, kinsan kuma babu kyau wulak'anci, ki taimaka dan Allah ki saurareshi ki ji da abin da ya zo kinji?".

Bata kuma cewa komai ba tabi bayansa, Ya Sayyadi Umar ya mik'awa Anwar hannu sukayi musabiha ya mik'awa Yarima Fudhal amma Yarima ko kallon inda yake baiyi ba, Ya Sayyadi ya sauke hannunsa cike da murmushi yana mai da kallonsa kan Aynu.

"Zan jira ki".

Haka yace da ita ya koma inda suke tsaye ya tsaya yana zaman jiran Aynu.

Aynu ta kau da kanta gefe ba tare da ta ce da su komai ba, har tsayin wani lokaci shi Anwar yama rasa ta inda zai fara domin Aynu ayau sai yaji tayi masa kwarjini da yawa gashi kuma ta had'e girar sama da ta k'asa alamun babu wasa, Yarima kuwa ya kafeta da ido babu ko k'iftawa sai faman doka murmushi kawai da ya keyi wani sanyin dad'i na ratsa dukkan sassan jikinsa, Anwar ne yayi k'arfin halin fad'in.

"Sannu Gimbiyarmu, kina lafiya?".

"Lafiya k'alau".

Hakan da tace ne ya bashi damar ci gaba da fad'in.

"Kina neman zauta Yariman mu da soyayarki ko?, yanzu dai gashi nan ya tasomu cikin daren nan ya ce inbai ganki ba babu zaman lafiya....!".

Kallon data watsa masa ne ya sanya shi tsuke bakinsa tun kafin ya k'arasa maganarsa.

"Yanzu ai ya ganni ko?, to zaku iya tafiya daga yau bana k'aunar sake ganinku k'ofar gidanmu har a bada !, wancen shine wanda zan aura nan da lokaci k'ank'ani fatan kun gane?".

Bata jira mai zasu ce ba tajuya abinta, ba Anwar ba hatta Yarima mutuwar tsaye yayi a wajen, yama rasa ta cewa domin dama kasa furta komai yayi sabida bai san mai zai ce da ita ba, amma ko babu komai ya d'anji sanyi a cikin ransa domin yaga farin cikin rayuwarsa Qurratul-aynun sa (Sanyin idaniyarsa).

Anwar ne ya ja shi har zuwa mota suka shiga Anwar ya tada mota suka bar layin.

"Yanzu kenan Aynu ta san komai?".

Cewar Yarima kenan yana mai duban Anwar, Anwar bai dube shi ba ya fara fad'in.

"Ai ba sai ka tambaya ba, daga maganganun da take da irin kallon da take jifanmu da shi wannan kawai ya isa ka bawa kanka amsa...!".

Yarima Fudhal yayi a jiyar zuciya tare da kwantar da kansa bisa kujerar motar ya lumshe ido sai ga hawaye na bin gefan idonsa a hankali ya furta.

"AYNUL-HAYAT fountain of life.....!".

*YARIMA FUDHAL*

Na
FIRDAUSI S.A(QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

SADAUKARWA:-Namesy Phirdauceey Jeebour.

27

BAYAN SATI 'DAYA...!

Cikin satin abubuwa da dama sun faru ciki kuwa har da d'an samun sauk'in jikin Fudhal, hakan ya sanya aka gudanar da bikin bud'e sabon asibitin Yarima Fudhal da mai martab'a ya gidana masa, an fara aiki gadan-gadan kwararrun likitoci aka d'auka domim taya Yarima Fudhal gudanar da asibitin yanda ya kamata.

Duk irin dauriya da dannewa da Yarima ya keyi amma hakan na neman fin k'arfinsa, domin wani lokacin yakan kasa daurewa zuciyarsa daga abin da take muradi, har sai ya d'auki mota yaje layin gidansu Aynu ya tsaya har lokacin zuwa islamiyyarta sai ya ganta sannan yakan d'anji dama-dama cikin ransa, Aynu da Zainab basu tab'a gane shine a cikin motar ba domin yakan d'auko d'aya daga cikin motar abokan aikin sane baya d'aukar motarsa sabida gudun kada su gane shi.

Al'amarin Aynu kuwa a kullum burinta bai wuce tamance da Yarima Fudhal ba, tana so tasa aranta tamkar mafarkinsa tayi ta farka, sai dai hakan ya gagara a gare ta, sau tari idan suka zo wuce wa ta inda Yarima ke tsaye Aynu takanji bugun zuciyarta ya tsananta sosai kuma tanajin k'amshin turarensa sai dai Zainab takance ba shi bane kawai dai har yanzu tana son sane shiyasa takeji kamar shine a motar, batun turare kuma ai bashi ka d'ai ne ke amfani da irin saba, ba shi kad'ai campany suka yiwa ba, ita dai Aynu tana barin zancen ne kawai domin Zainab ba ta yarda amma tanaji a cikin ranta tabbas Yarima ne.

"Wai Uwar soro har yanzu aikin yak'i samuwa ne?".

Uwar soro ta d'an risina tana fad'in.

"Wallahi ranki ya dad'i duk iya k'ok'arin da nakeyi abin ya faskara na rasa yanda zanyi insamo...!".

"Kinga idan kawai bazaki iya ba ki sanar dani tun da wuri !, abu kusan wata guda amma ya gagara?".

"A k'ara hak'uri dai ranki ya dad'e insha Allah cikin satin nan komai zai kammala".

"To babu damuwa amma fa kiyi aiki da nutsuwa da kulawa".

"Babu matsala ranki ya dad'e kada ki damu".

"Shi kenan tashi kije".

Uwar soro ta mik'e tabar d'akin, Jalila dake zaune gefan Fulani Sokoto tana faman danne dannan wayarta tayi tsaki tare da wurga wayar kan kusun tana fad'in.

"Aikin banza!, Wallahi Mama ke ki ke yarda da aikin wasu bare, ni da kin yarda da tuni anyi komai ya wuce munriga munsan matsayar da muke".

Fulani tayi murmushi tare da fad'in.

"Jalila kenan !, Ke fa yarinya ce har yanzu , amma bazank'i ta taki ba, me kike ganin zaki wanda bazamu iya ba?".

Jalila gyara zama tayi tana fuskantar Mahaifiyarta sosai.

"Yauwa Momy abin da ya kamata ki ce kenan tun d'azu, ki bani kwana biyu cikin kwanakin tabbas zan samo maki takun k'afar Fudhal".

"To amma ta yaya?".

"Momy...! Ke dai kawai ki zuba ido".

"Bawai nak'i ta taki ba ne, inajin tsoron al'amarin ne kawai, amma dai kiyi komai cikin nutsuwa da taka tsan-tsan, domin kinfi kowa sanin yanda Fudhal da d'an'uwanki suke, ban-bancin kamanni ma kad'anne haka wajen kayansu zuwa takalmi kinsan abune da sai mutum ya lura sosai  da kulawa sabida ka da a samu miskila".

"Haba Momy...!, Ni har sai anmin wannan baya ni, idan ni ban iya tan-tance Fudhal da Jalil ba waye zai gane?".

"Uhmm to haka ne kuma Jalila".

"Yauwa wai Mama ina Jalil kuwa?, kusan 2week fa kenan bana ganinsa cikin gidan nan?".

Fulani tayi ajiyar zuciya tare da tab'e baki tana fad'in.

"Ni ina zan sani Jalila..! komai ina yi ne domim gobenku, amma shi baya fahimta kullum al'amarin nasa k'ara gaba yake yi, shi da ya kamata ace yana girma yana hankali amma ina...!, waye zai yarda abashi ragamar Sarauta a cikin wannan halin nasa?".

"Ka da ki damu Momy komai zai dai-dai ta".

"Fatana kenan Jalila".

***

Dawowarsa kenan daga asibiti lokacin kusan k'arfe biyar da mintuna na yamma ya zauna gaban Fulani Bingel tare da fad'in.

"Wash Hajiya wallahi nagaji yau sosai".

"Kai dai ka shigesu da lalaci kamar ba namiji ba?".

"Namiji baya hutu kenan Hajiya?".

"Ni dai bance ba, amma kai kullum ka dawo wash ne sallamarka cikin falon nan tun da ka fara aiki".

Yarima Fudhal yayi murmushi wanda ya baiyana hak'oransa waje, amma daka kalli fuskarsa zaka san yana k'ok'arin danne damuwar da ke kwance bisa fuskarsa ne.

"Au.. Magaji ai kuwa zama bai ganka ba, yanzu akayimin waya Sadiya ta haihu ".

"Masha Allah mai ta haifa Hajiya?".

"Yan biyu ne aka samu mace da namiji".

"Allah ya rayasu yanzu kuwa zanje, fatan tana lafiya dai ko?".

"Lafiya k'alau ta haihu har an sallamesu daga asibitin sun koma gida".

Yarima Fudhal ya mik'e yana fad'in.

"Bari inje inshafo maki kan jikokin naki".

"Ko dai kaje ganin 'ya'yanka dai?".

Nan ma dariya sukayi a tare, tana bashi sallahun ya gaishe da su tare da mik'a masa wata k'atuwar leda fara ta ce ya kai mata, Yarima Fudhal ya amsa ya fice, Fulani Bingel ta bishi da fad'in.

"In kaje ka samu kaci abinci dai".

Ya amsa da "to Hajiya".

Bayan fitarsa Fulani Bingel murmushi tayi a fili take fad'in.

"Ina ruwan Magaji...! shi dai yana son yara sosai, Allah dai ya nunamin ranar da zanga naka yaran kai ma".

Baki har kunne ya shiga cikin gidan, da sallama ya sanya kai cikin falon mijinta ne zaune shi da yaransa guda biyu mata kusan kansu d'aya ga kuma mugun kama da suke yi, yaran tubarkalla gasu da kyau, da gudu yaran suka taso suna fad'in.

"Oyoyo Uncle..!".

Suka rungumeshi ya tsunna ya rumgumosu jikinsa yana fad'in.

"Saleema da Saleena anyi k'anne kuma baki ba rufuwa".

Dariya suka yi atare suka sumbaci kumatunsa, shafa kansu yayi yana fad'in.

"Nagode yara na !".

Ya mik'e ya k'arasa wajen Baban nasu suka gaisa, yana tambayarsa .

"Ina Maman tasu?".

"Suna ciki ka shiga ku gaisa mana".

Yarima Fudhal ya kama hannun yaran suka shige cikin d'akin, Aunty Sadiya na kwance bisa gado sai jariran agefan ta, gefe guda kuma Aunty Sa'ida ce da wasu mata su biyu, suka gaisa da matan suka fice.

Yarima ya gaishe dasu Aunty Sadiya ya d'auki yaran yana mai k'are musu kallo, kafin yayi murmushi yana duban Aunty Sa'ida.

"Aunty na sai nakejin yaran nan kamar Aynu d'ita ce ta haifamin wallahi, shi yasa Hajiya na gayamin na kasa daurewa sai nazo na gansu".

Aunty Sa'ida ta tab'e baki kawai tana dubansa cike da takaicin maganar da yayi.

"Au wai kai har yanzu baka bar maganar yarinyar nan ba?".

Cewar Aunty Sadiya kenan tana daga kwance.

"Taya kuwa zan barta Aunty na, baki san yanda nake jinta ba a cikin raina Allah".

"Sai kayi kuma, iska na wahal dame kayan kara".

Aunty Sa'ida ta fad'a tana mai jan hannuwan Saleema da Saleena suka fice daga d'akin, Yarima Fudhal ya bita da kallo ko kad'an bayajin dad'in yanda take yi masa akan Aynu, Aunty Sadiya ta dafa hannunsa tana fad'in.

"Kar ka damu k'anina, komai zai wuce soyayyarka ta gaskiya ce insha Allahu zaka sameta idan har matar kace, idan kuma Allah bai k'addara matar ka bace kayi hak'uri kaji sai Allah ya musanya maka da mafi alkhairi".

Yarima Fudhal murmushi yayi cike da jin dad'in maganar Auntyn tasa, bai ce komai ba illa mai da kallonsa kan 'yan Jariran da yayi yana mai kai musu kiss a goshinsu cike da so da k'auna sosai yakejin yaran cikin ransa.

Hello

Kuyi hak'uri da wannan dan Allah babu yawa rashin chaji yaja nayi muku typng kad'an dan kada kuji ni shiru.

Nagode sosai da sosai masoyana kuna raina ko da yaushe.

*YARIMA FUDHAL*

Na
FIRDAUSI S.A(QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

SADAUKARWA:-Namesy Phirdauceey Jeebour.

28

"Wannan shine gaskiyar abin da ya faru, please Baba..! Dan Allah ka taimaka kajanye hukuncin da ka d'auka, ka san gaskiyar abin da ya faru yanzu wallahi Yarima yana son 'yarka da gaske so na tsakani da Allah".

Baban Aynu shiru yayi kansa na k'asa, tsayin lokaci ya shafe yana tunani kafin ya d'ago kansa ya kalli Anwar dake zaune yana jiran yaji amsar da zata fito daga bakinsa.

"Yaro kayi hak'uri kuje ku sake wata shawaran wannan ba zata samu karb'uwa ba, domin nasan ka zo ne da silar yaudara kamar yanda kuka zo da farko".

"Baba wallahi dukkan abin da na fad'a a yanzu gaskiya ne, idan da farko munzo da yaudara wallahi tallahi Allah d'aya ne Baba bazan yi rantsuwa akan k'arya ba dukkan abin da na fad'a a yanzu babu haufi a cikin sa".

Shiru ne ya sake biyowa baya kafin Baban Aynu yace.

"Shikenan kaje zan neme ka".

Anwar yayi godiya tare da mik'ewa ya bar wajen zuwa cikin motarsa ya tada ita ya bar bakin kasuwar, Baban Aynu ya shafe tsayin lokaci zaune yana nazari a kan maganar da Anwar ya sanar da shi yanzu, kafin ya mik'e ya nufi gida zuciyarsa cike da wasi-wasin al'amarin.

***

"Kayi farin ciki Yarima na sanarwa Baban Aynu gaskiya da dukkan alamu kuma ya yarda damu yanzu, ya kayi tsaye kana kallona baka farin ciki ne?".

Yarima ya ajiye wayarsa dake rik'e a hannunsa kan table d'in gabansa ya dubi Anwar cike da kulawa kafin ya fara magana.

"Me zance to Anwar?, zai nememu fa kawai ya ce da kai, inajin tsoron abin da zai biyo baya ne, kana da tabbacin ya yarda da abin da ka gaya masa?".

"Ehh mana, ya kamata kayi kyakykyawan zato Yarima".

"Hakane nagode sosai Anwar".

"Haba dai mene abin godiya kuma?, ai ana tare".

***

Baban Aynu ne zaune bisa tabarma da Umma a zaune gefansa suna tattaunawa kan batun Aynu da Ya Sayyadi.

Baba ya dubi Umma cikin kulawa ya ce.

"Ya kamata a ce da Umar ya fito ayi magana, ko ya kika gani Umman Aynu?".

"Haba dai Malam..! Me zai hana a d'an k'ara kwana biyu, kana ganin yarinyar nan fa yanda ta koma har yanzu ta kasa mai da walwalar jikinta".

"Ehh haka ne, amma ni ma a son raina dama ba yanzu ba, to wancan yaron ne ke neman canjamin a kalar maganata ne, kinga idan aka riga akayi baikon ya hak'ura ai".

"Haka ne kuma, amma malam kamarya yana neman canja akalar maganarka?".

"Ehh to d'azu a kasuwa a bokinsa ya zomin da maganar dukkan abin da ya faru a shekarun baya, ba na so tausayin yaron yayi tasiri araina incanja maganata".

Nan dai ya kwashe komai ya sanarwa Umman Aynu, Umma ajiyar zuciya tayi tana fad'in.

"Allah sarki yaban tausayi sosai wallahi, a she ba shi da laifi laifin duk na mahaifinsa ne?, yanzu mai ka yanke akan hakan?".

"Maganata babu canji Aynu Umar zata aura, domin shi yafi dacewa damu da rayuwarta, yaron d'an mutunci wanda ya san mutunci taya zamuyi sake ya sub'uce mana a matsayin suruki?".

"Gaskiyarka Malam domin duk wata uwa ta gari burinta 'yarta ta auri miji nagari, haka kuma duk wata uwa ta gari burinta d'anta ya auri mata tagari, nima har cikin raina Umar ne zab'ina".

Aynu dake zaune cikin d'aki duk tana jin tattaunawar da iyayenta keyi, tana faman share kwallar dake zubo mata bisa kan fuskarta a fili ta furta.

"Yanzu ya zama dole inkoyawa zuciyata son Ya Sayyadi Umar, kamar yanda ya zamana dole in fidda son Yarima a cikin raina..!?".

Ta kifa kai bisa tabarmar da take zaune a kai tana shash-shek'ar kukan da babu mai lallashinta.

BAYAN KWANA UKU.

Zaune yake a office d'insa kamar kullum yayi nisa cikin tunani sosai, ya yin da k'asan zuciyarsa keta faman azal-zalarsa da son ganin Aynu, har sai da ya kasa jurewa bare ya iya sarrafa kansa wajen bawa zuciyar tasa hak'uri.

Ya d'ago jajayen idanuwansa dai-dai lokacin da agogon office d'in ya buga k'arfe shida da 'yan mintuna, sai lokacin ya san irin dad'ewar da yayi a zaune yana aikin tunani, tattara komai yayi ya mayar inda yake ya fice da sauri zuwa wajen motarsa ya tayar da ita ya fice daga cikin harabar asibitin.

Kai tsaye gida ya nufa bai tsaya ko ina ba sai cikin d'akinsa yana shiga ya fad'a toilet y sakarwa kansa sassanyan ruwan shower, wai dan ya d'anji sanyi a ransa amma duk da haka bai samu yanda yake so ba.

Fitowa yayi bayan ya d'auro alwala ya ta da sallar maghriba domin lokacin anata kiraye-kirayen sallar shi kuma baijin zai iya zuwa sabida yanda yake jin jikinsa, ya jima kan sallah yana jero tarin addu'o'i wanda zan iya cewa addu'artasa duk a kan Aynu ce, sai a lokacin ya d'anji dama-dama a cikin ransa.

Yana shafawa ya janyo wayarsa ya kira number Anwar amma switchoff hakan yasa ya wurga wayar kan katifa ya mik'e ya shirya cikin k'ananun kayan riga T.sheet fara da adon bak'i a jikinta sai ya sanya bak'in wando jeans bai damu da ya gyara sumarsa ba kamar yanda ya saba ya d'auki key d'in motar ya fice daga gidan.

Duk a bin da yake Jalila na lab'e tana kallonsa, domin yau taci alwashin sai ta samu abin da take so, har sai da ya fice sannan ta fito daga mab'oyarta ta koma part d'insu tana zaman jiran

dawowarsa.

A k'ofar layin nasu ya tsaya yayi parking ya fito ya kulle motar ya taka har zuwa k'ofar gidansu unguwar shiru kamar anyi shara ya shafe tsayin lokuta a tsaye amma babu ita babu labarinta kuma ya rasa wanda zai aika zuwa gidansu, domin yau yaci alwashin kome zai faru sai yaga Aynunsa.

Yayi nisa cikin tunani yaji ana fad'in.

"Lafiya dai Yarima?".

D'ago kai yayi da sauri domin a tunaninsa Aynu ce sai dai yaga sab'anin haka Zainab,murmushi ya saki wanda bai wuce kan leb'ansa ba yana fad'in.

"Alhamdulillahi gara da Allah ya kawo ki".

"Lafiya wani abun ya faru?".

"A'a babu komai, kawai dai wani taimako nakeso kimin dan Allah".

"Taimakon me fa?".

"Ki fitomin da Aynu ".

Zainab ajiyar zuciya tayi kafin ta ce.

"Ai kuwa Aynu bana jin zata fito yanzu, dama dai kayi hak'uri kuma kasan a gida ma ba za'a bari ta fito ba".

"Please dan Allah ki taimake ni".

Yayi maganar kamar zai yi kuka, sosai tausayinsa ya kama Zainab ta ce.

"To jira mugani Allah yasa ta fito".

Ta juya ta shige cikin gidan ta bar Yarima nan tsaye yanata zuba addu'o'i cikin ransa akan Allah ya taimake shi ta fito.

Kusan mintuna goma sha biyar suka shud'e ba amo babu labarinsu can dai kamar ance d'ago

kanka ya gansu sun fito tare Aynu na faman turjewa Zainab na rok'onta, cikin d'acin rai Aynu ke fad'in.

"Kema kin koyi mumafunci ko?, ki ka cemin Ya Sayyadi ne".

"Yi hak'uri dan Allah ki saurare shi".

Aynu ta dubi inda Yarima yake shek'ek'e ta buga tsaki ta juya zata koma, Yarima yayi saurin kamo hannunta tare da shan gabanta yana fad'in.

"Kiyi ha'uri dan Allah ki saurare ni".

Yayi maganar cikin sanyin murya, Aynu ta tsaya tana kallonsa kawai nan suka hau kallon kallo tsayin wasu lokuta kafin Aynu ta fizge hannunta tana yi masa wani irin kallo daya kasa fassara kona mene.

Tsaki taja kafin tace.

"Ka b'acemin da gani Yarima..! Na tsaneka..! Bani son ganinka ko kad'an acikin rayuwata domin ka jiwa zuciyata ciwon da banajin akwai maganin warkewarta, me ya sa..! Me yasa...!! Me yasa Yarima?".

Sai kawai ta fashe da kuka, sosai Yarima kejin kukan Aynu har cikin zuciyarsa, a hankali ya cire hannunsa da ke cikin aljihun wandonsa yakai hannun da niyar share mata hawayen sai kuma ya sauke hannun da k'yar yayi k'arfin furta.

"Kiyi hak'uri Aynu...!, Ki sani ina sonki har cikin raina wallahi, dukkan abubuwan da suke faruwa har yanzu ban fidda rai da ke ba, domin inajin a raina ke tawace har abada kuma zamu rayu tare, amma yau she ne wane lokaci ne abubuwan zasu dai-daita ban sani ba?".

Aynu ta d'ago jajayen idanuwanta tana kallonsa cike a takaijin jin maganar da yake yi.

"Kama daina wannna mafarkin, domin Aynu nan da wasu watanni matar wani ce, kalamanka banjin zasuyi ta siri a raina Yarima, kamar yanda kuka so yi da farko sai dai Baba ya taka muki burki, to nima inaso kamanta da ni...!".

Kafin ta kai ayar maganarta sai ganin Yarima Fudhal tayi tsugunne a gabanta bisa gwiyoyinsa idanuwansa fal da hawaye.

"Kiyi hak'uri dan Allah da Annabinsa nasan nayi kuskuren da babu abin da zanyi domin gyaransa amma ki sani Aynu babu wani bawa da zai iya kaucewa k'addararsa, nasan na zalunce ku ke da iyayenki amma ki sani komai muk'addari ne daga Allah, dan Allah ki janye daga batun auren wani bani ba, Aynu inasonki wallahi zan iya rasa raina Ayn...!".

"Naji kana so na..!, amma duk kai kaja dukkan abubuwan nan suke faruwa, Babana bawai yana da burin d'aukan fansa bane, haka ni ma bana da burin fansa cikin raina, amma me yasa Yarima kayanke shawaran azurtamu da kud'inka kamance Allah ke azuratawa ba bawa ba, kai ma da kuke tak'ama da kud'i da mulkin ai duk Allah ne ya baku ayau in yaso sai ya karb'e abinsa, mai yasa kazo wajen Baba da fuska biyu?, mai yasa baka zo kanka tsaye ba domin kafuwar soyayyar da kakemin idan har gaske ne?, ina ji a raina bani kake so ba akwai dai abin da kake so, domin idan har ni kake so ba zaka yi tunanin amfani da kud'i ba zakayi ne domin yak'ini da zuciyarka".

Yarima kamo hannun Aynu yayi yarik'e k'am ba tare da ya lura da hakan da yayi ba.

"Ki fahimce ni Aynu, sonki shine yafi tasiri a zuciyata fiye da komai, sonki ne ya sanya zuciyata ta rufe, tunani na ingyara kuskuren da nayi, amma mai makon in gyara sai in k'arawa kaina wani laifin ba tare da nasan hakan ba, ki ga farce ni dan Allah ka da kiyar da ki auri wani ba ni ba Aynu zanyi k'ok'arin ganin na gyara kuskure na...!".

"Taya zaka gyara kuskuren naka?, Kuskure ka riga kayi ai sai dai ka kiyaye gaba , amma ka sani har yau ba zan dai na fad'a maka ba, gobe za'ayi bai kona da Ya Sayyadi nan da watanni ni mata ce a gare shi, ina so ka manta da ni kasa wa ranka tamkar mafarki na kayi ka farka...!".

Aynu ta fizge hannunta ta shige gida da gudu tana kuka, Yarima zaman dirshan yayi a wajen zuciyarsa na zafi da k'una, har ya naji dama Allah ya d'auki ransa a dai-dai wannan lokaci akan yana ji yana gani Aynu ta auri wani ba shi ba, duk abubuwan da suke faruwa Zainab na gefe tana kallo har sai da suka sanyata zub da hawaye ita ma.

Yarima da k'yar yayi k'arfin halin mik'ewa yana jan k'afa cike da tangad'i kamar wani d'an shaye-shaye ya bar layim gidansu Aynu zuwa inda yayi parking motarsa ya bud'e ya shiga ya zauna tare da kifa kai bisa sitiyarin motar.

[04/09, 05:00] Hassan Atk: *YARIMA FUDHAL*

Na
FIRDAUSI S.A(QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

SADAUKARWA:-Namesy Phirdauceey Jeebour

30

Am so sorry abisa jina da kukayi shiru kwana da yawa wlh fever ya rik'eni...amma yanzu Alhmdlh ngd sosai da call naku zuwa text message ubangiji Allah yabar kauna amin kuna raina any time ana mugun tare.!

***

"Haba Yarima ka da ka mance kaima Doctor ne?, amma ya kake k'ok'arin jawa kanka matsala ne?, ka fini sanin illar da ke tattare da ciwonka fa...!, Please Yarima kayi k'ok'arin cirewa kanka damuwar da ke tattare cikin zuciyarka tun da wuri domin kana dab da fuskantan babbar matsala?"

Yarima Fudhal bai ce komai ba illa kafe Doctor Mansur da yayi da shanyayyun idanuwansa babu ko k'iftawa, Anwar ne ya dubi Doctor Mansur cike da kulawa yana fad'in.

"Insha Allahu zamuyi k'ok'arin kiyayewa Doctor zan fahimtar da shi da yardar Allah komai zai yi normal".

"Ok babu damuwa tun da kai ka fahimce ni zaka iya fahimtar da shi, Allah ya k'ara lafiya ni zan

koma?".

Sukai sallama da Anwar ya fice daga d'akin ba tare daya sake duban Yarima ba.

Yana fita aka sake turo k'ofar Yarima Jalil ne ya shigo cikin shiga irin ta Yarima Fudhal farar T.sheet da bak'in wando Jeans har adon rigar da komai iri d'aya.

Zama yayi a gefan da Fudhal ke kwance bayan ya mik'awa Anwar hannu sun gaisa yana fad'in.

"Ya dai Bro bakajin dad'i ne?".

Yarima Fudhal ya gyad'a masa kai alamun E .

"Ayya am sorry..! Jalila ma nacan kwance da alamu ko magana bata iyayi amma ta matsa a kirawo mata kai".

Yarima Fudhal ya kafe Jalil da ido yana fad'in.

"Meke damunta?".

"Waya sani?, Momy dai ta ce tun dare ne tayi mafarki shikenan take ta aikin kuka har safe bata koma bacci ba, amma kuma tak'iyin magana ".

"Subhanallahi...bari intashi muje to !".

Yarima Fudhal ya mik'e da k'yar suka fito daga d'akin dukansu a hanyar zuwa part d'in Fulani Sokoto ne yake tambayar Yarima Jalil.

"Wai kai ina kake zuwa ne? ina lura da kai kusan 2week kenan baka gidannan, yaushema ka dawo ne?".

Yarima Jalil sosa k'eya yayi tare da wata 'yar guntuwar dariya.

"Naje hutu ne kawai, jiya da dare na dawo na shiga d'akinka baka nan ai".

Yarima Fudhal ya watsa masa wani mugun kallo kawai ya d'auke kansa, a can k'asan ransa bak'aramin ciwo yakeji ba akan munanan halayen Jalil bai san meya sa baki d'aya ya gama

lalacewa shine shaye-shaye neman mata duk ya had'a kamar ba jinin sarauta ba?.

Suna shiga falon babu kowa kai tsaye d'akin Jalila suka nufa da sallamarsu Momy ce zaune gefan Jalila ita ce ma ta amsa musu sallamar, dukansu suka gaisheta tare da tambayar jikin Jalila, ita kuwa Jalila tun da suka shigo take bin Fudhal da Jalil da wani irin kallo kamar yau ta fara ganinsu.

Yarima Fudhal ya zauna gefanta yayin da Anwar da Jaleel suka nemi gefe guda suka zauna Momy ta mik'e ta fice daga d'akin.

Fudhal ya rik'o hannunta yana fad'in.

"Ya jikin naki?".

Kai kawai ta gyad'a amma babu bakin magana.

"Bakya iya magana ne?".

Nanma kan ta sake d'aga masa.

Yarima Fudhal shiru yayi kawai yana dubanta tausayin k'anwar tasa ya kamashi yama rasa mai ya kamata yayi mata?.

Mik'ewa yayi ya fito daga d'akin zuwa falo dai-dai lokacin da Momy ke fad'awa Larai baiwarta.

"Kiyi maza ki kai masa sak'on dan Allah bana son a samu kuskure kice a yi aikin cikin gaggawa dan Allah...!".

Maganarta ta katse dai-dai sanda Fudhal ke fitowa zuwa falon, Fulani Sokoto tayi wani mayaudarin murmushi tana fad'in.

"Har ka fito Magaji?".

Fudhal ya nemi guri ya zauna ba tare daya bata amsa ba, Larai kuma tamik'e da sauri ta fice daga d'akin.

"Momy ta fad'a miki abin da tayi mafarki ne?".

"A a nidai ihunta kawai naji cikin dare ina shiga d'akin na lallasheta tayi bacci na koma d'akina da nufin da safe na tambayeta amma da safen duk yanda naso tabud'e baki tayi magana amma

abu ya faskara".

Yarima Fudhal yayi shiru nad'an wani lokaci kafin yace.

"Bari musan abinyi to a tafi da ita hospital d'inmu domin akwai kayan aiki sosai, zamu gano inda matsalar take".

Fulani Bingel ce tayi sallama dai-dai wannan lokacin Fudhal ya amsa fuskarsa fal murmushi ya durk'usa ya gaishe da ita, suka gaisa da Fulani Sokoto tana tambayar.

"Ina mai jikin?, naji ance Jalila ba taji dad'i ba".

"E tana d'aki ".

Cewar Fulani Sokoto kenan, Fulani Bingel ta mik'e ta nufi d'akin yayin da Fudhal da Fulani Sokoto suka take mata baya.

"Allah sarki !, Sannu kinji Jalila Allah k'ara sauk'i".

"Amin".

"Amma mene yake damunta?".

Fulani Sokoto ta d'anyi dariya tare da bata amsa.

"Mafarki ne tayifa shine baki d'aya ta koma haka".

"To a san abinyi tun da wuri mana".

Fudhal ne yayi saurin bata amsa a wannan lokacin.

"E muna kanyin hakan kika shigo, nace a kaita hospital namu sai induba inda matsalarta take".

Fulani Bingel ta gyad'a kai tare da mik'ewa suka fito daga d'akin dukansu, tayiwa Fulani Sokoto sallama ta fice daga part d'in yayin da Fudhal da Anwar suka tako mata baya.

Sai da suka raka ta har cikin falonta sannan suka fito suka koma d'akin Fudhal domin ya d'an kwanta ya huta sabida shima ba lafiyarce gareshi ba.

Kwanciya yayi bisa carpet tare da d'ora kansa kan kusun, Anwar ya zauna kusa da shi yana mai

k'are masa kallo kafin ya bud'e baki ya fara magana.

"Wai Fudhal mene matsalarka ne?".

Fudhal ya bud'e ido a hankali tare da saukesu kan fuskar Anwar yana mai jifansa da wani guntun murmushi da bai wuce kan leb'ansa ba.

"Tambayarka nake, wai ina kaje ma jiya da dare ne?"

"Wajen Aynu".

Ya bashi amsa a tak'aice.

"To amma meye dalilin tashin ciwonka, kasan a halin da nazo na tadda kai kuwa?".

"Koma a wanne yanayi ne nasan zaka iya tadda ni, sabida abin da ya faru ajiya bana sonma ina tunashi ko kad'an".

"Aynu da bakinta tace bata sona ta tsanane ita bazata aure ni ba, tariga ta tsai da wanda zata au...!".

Maganar ta mak'ale a mak'oshinsa sabida numfashinsa da ke barazanar d'aukewa, hakan ya sanyashi yin shiru ya mai da idonsa ya rufe yana fitar da wani irin numfashi mai zafi.

Sosai tausayin Fudhal ya kama Anwar sai binsa da kallo kawai yake, mutumin da in banda Mahaifiyarsa bai d'auki mace wani abuba arayuwa, yau gashi mace na wahalar da shi kuma macen ma ba 'yar gidan kowa ba 'yar talakawa, shi da ya d'auki soyayya kamar shirme ko hauka yau gashi a kanta yana neman rasa rayuwarsa, dama bahaushe yace komai lokaci ne abin da kake rainawa wata rana shine zai baka tsoro.

Yarima Jaleel ne ya shigo falon yana fad'in.

"Broda anshirya Jalilah inji Momy".

Sai lokacin Fudhal ya sake bud'e idonsa daya kad'a yayi jajir ya dubi Jaleel tare da fad'in .

"Ku wuce kawai zan biyoku a baya".

Jaleel ya fice daga d'akin cikin sauri domin jiransa suke a mota.

Bayan fitar Jaleel Yarima ya shafe tsayin lokuta ba tare daya mik'e ba, da k'yar dai ya mik'e ya shige bedroom nasa domin ya d'an watsa ruwa yabar Anwar zaune a falo.

Cikin mintuna kad'an sai gashi ya fito cikin k'ananun kaya duk da cewa ba wani tsayawa yayi yin gwalli ba hakan bai hana kyawunsa da b'oyayyar damuwar dake kwance k'asan fuskarsa baiyana ba, Anwar ya jefawa key d'in mota tare da fad'in.

"Tashi mu tafi".

Anwar bai ce komai ba yamik'e yabi bayan Fudhal don shi tuni yayi waje abinsa.

Suna isa asibitin Jaleel da Momy na zaune zaman jiran zuwansa, bai tsaya wani b'ata lokaci ba ya nufi d'akin da aka kwantar da Jalilah domin gwajin da za'ayi mata.

Sun shafe kusan a wanni uku zuwa hud'u duk abin da ya kamata ayiwa Jalilah anyi amma hakan bai sanya angano takamai-mai abin a yake damunta ba, abin da result ya bayar kawai maleria ke damunta.

Ko da Fudhal ya fito ya had'a zufa sosai ga kuma kansa dake matsanancin sara masa, bai bi takansu Momy ba kawai office nasa ya wuce yana goge gumin da ke tsatstsafo masa, ya zauna kan kujera tare da k'aro sanyin A.C da ke office d'in, ya kwantar da kansa kan kujerar tare da lumshe ido yana aikin daya saba.

Turo k'ofar da a kayi ne tare da kiran sunansa ya sanyashi d'ago kai yana mai k'are masu kallo, Anwar da Jaleel suka zauna akan kujerun da ke gaban table d'in Yarima suna mai binsa da kallo suma.

"Lafiya Yarima ya jikin Jalilan?".

Anwar ya jefa masa tambaya, Yarima ya gyara zamansa tare da janyo file d'in Jalilan yana dubawa can ya rufe yana mai mayar da kallonsa kansu.

"Al'amarin ne yake d'auremin kai Anwar duk iya binciken da mukayi maleria kawai result yake bamu".

Fudhal yayi  maganar murya a sanyaye, Jaleel ya gyara zama sosai yana fad'in.

"Maleria kuma?, ba'a gano dalilin da yasa bata magana ba?".

"Wallahi munyi iya yinmu Jaleel nima abin da yake damuna kenan".

Shiru ne ya biyo baya kafin Anwar yace.

"Kuma ban da maleria babu wani ciwo da ke damunta?".

"E".

"Abin da mamaki fa?".

Cewar Jaleel ya fad'a tare da mik'ewa yana mai cigaba da  fad'in.

"Bari inje insanarwa Momy to".

"Zaku iya wucewa da ita gida, nima yanzu zan tawo domin nafara jin fever wallahi".

"Ok Allah yak'ara lafiya sai kun dawo".

Ya fice daga office d'in ya barsu.

KUYI HAK'URI DA WANNAN.

NAGODE SOSAI DA SOSAI MASOYANA MASU BIBIYAR LITTAFINA INA K'AUNARKU NIMA HAR A ZUCIYATA.
[04/09, 05:00] Hassan Atk: *YARIMA FUDHAL*

Na
FIRDAUSI S.A(QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

SADAUKARWA:-Namesy Phirdauceey jeebour.

29

Ya shafe tsayin lokaci a zaune a cikin motar ya rasa abin da yake masa dad'i cikin duniya, ji yayi baki d'aya bazai iya driven ba hakan yasan yashi fara lalub'en wayarsa domin kiran Anwar ko Jalil wani yazo ya d'aukeshi amma sai bai ganta ba, sai can ya tuna yabarta agida.

Da k'yar ya iya sanyawa motar key ya kunnata tare da barin layin gidan nasu Aynu.

A wannan lokaci Allah ne kad'ai ya kai Yarima gida lafiya, domin tun kafin ya kai ga k'arasawa yaji idanuwansa na dishi-dishi har dai yayi parking a harabar gidan ya kashe motar kawai ba tare da ya cire key d'in ba ya nufi part d'insa, yana shiga falo kuwa ya zube k'asa lokacin agogon da ke falon ya buga k'arfe sha biyu da rabi dai-dai, da rarrafe ya k'arasa cikin bedroom d'in zuwa wajen drower da yake adana magungunansa ya nufa ya d'auko ya fara had'iyarsu d'aya bayan d'aya ba tare da ruwa ba, sai da ya tabbatar ya gama had'iya sannan ya rarrafa ya d'auko gorar ruwan faro mara sanyi ya sha, a wajen ya zube a kwance.

Tsalle tayi tare da fad'awq kan cinyar Fulani Sokoto tana fad'in.

"Na samo Momy na samo burinmu zai cika Momy".

Cike da murna da garin ciki Fulani Sokoto ta karb'i k'unshin k'asar dake d'aure hannun Jalila tana fad'in.

"Alhamdulillahi...! lallai Jalila kin cika 'yata nayi murna sosai wallahi, ai da nasan zaki iya da tun farko aike zan sanya aikin".

Jalila tayi murmushi cike da jin dad'in kalaman yaban da Mahaifiyarta ke yi mata.

Sun shafe tsayi lokaci suna hira kafin Jalila ta mik'e ta nufi d'akinta tana fad'in.

"Asuta gari Momy".

"Mu tashi lafiya Jalila".

Ta shige d'akin ta bar Fulani Sokoto zaune falon cike da murna harta matsu taga gari yawaye .

Aynu kuwa tana shiga gida d'aki ta wuce da gudu ta zube kan katifar dake yashe tsakar d'akin tana shash-shek'ar kuka, a haka Ummanta ta tadda ita ta zauna zaman lalashinta, Aynu ta d'ora kanta kan cinyar Umman ba tare da ta ce komai ba, illa sharar hawayen da take kawai Ummanta na aikin bata hak'uri.

Zainab ita dai daga wajen bata koma gidansu Aynu ba gida ta koma jikinta yayi sanyi sosai tausayin Yarima yake kamata domin ita ayanzu tafi jin tausayinsa akan Aynun.

"Wayyo Allah na Momy...!".

Jalila ce ya farka daga bacci agigice sai faman zufa take baki d'aya ta rud'e, Momy da ke zaune falo har lokacin ba tayi bacci ba ta shigo d'akin da gudu tana fad'in.

"Lafiya Jalila..!, Mai ya faru?".

Jalila dake faman muzurai ta k'ank'ame Fulani Sokoto tana zubar hawaye.

"Kinga dan Allah karki damu mafarki kikayi ne?".

Jalila ta gyad'a mata kai domin ta kasa d'aga harshenta bare harta furta wata kalma.

"Aiba komai bane yi shiru kinji, mafarki ba gaskiya bane maza koma kiyi baccin ki babu abin da zai faru".

Fulani ta kwantar da ita tare da rufa mata bargo tana fad'in.

"Kiyi baccinki 'yata karki damu, da safe mayi magana".

Ta juya ta fice daga d'akin tare da ja mata k'ofa ta rufe, Jalila ta kalli inda agogon d'akin yake kafe agogon ya nuna k'arfe uku da 'yan mintuna na dare, amma sam Jalila ta kasa komawa baccin da take sosai tsoro yake ratsata tasan da wuya Mahaifiyarta ta fahimceta.

"Meke shirin faruwa ne?".

Ta furta hakan cikin ranta tare da mik'ewa zaune tana karanto addu'a cikin ranta.

Yarima kuwa tun da yayi wannan zubewar ya kwanta bai tashi farkawa ba, sai da garin Allah ya waye kusan k'arfe goma na safe ya bud'e ido tare da k'arewa d'akin kallo ya sauke dubansa kan Anwar dake zaune gefansa ga kuma Doctor Mansur yanata faman aunashi.

K'ok'arin mik'ewa Yarima Fudhal ya hauyi hakan ya saka suka fahimci ya farka, kamashi sukayi tare da jinginashi jikin pillow, Doctor Mansur ya zauna gefansa yana k'aremasa kallo kafin ya bud'e baki ya fara magana.

*YARIMA FUDHAL*

Na
FIRDAUSI S.A (QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

SADAUKARWA:-Namesy Phirdauceey Jeebour.

31

*BAYAN SATI 'DAYA*

Cikin satin abubuwa da dama sun faru ciki kuwa har da kawo kud'in auren Aynu da Ya Sayyadi Umar yayi kimanin dubu talatin tare da sanya ranar biki wata guda mai zuwa domin Baban Aynu yace baya son wasu bidi'o'i, shima Ya Sayyadin a nasa b'angarensa abin haka yake, hakan yasa bak'aramin dad'i yaji ba da yaji hukuncin da Babannata ya yanke a kan batun auren.

A cikin wannan lokaci ba zaka iya tantance halin da Aynu ta ke ciki ba farin ciki ko bak'in ciki Allah ne ya baiwa kansa sani sai kuma Aynun kanta.

Yauma kamar kullum tsaye yake jikin bishiyar darbejiyar dake k'ofar gidansu, yana zaman jiran fitowarta mintuna kad'an sai gata ta fito tana sanye da doguwar riga ta atamfa purple mai ratsin pink da adon fari ajiki sai ta sanya hijab pink mai hannu bak'aramin kyau kayan sukayi mata ba duk da cewar ita bak'ace amma hakan bai hana baiyanuwar kyawunta a cikin kayan ba.

Cikin takunta kamar bazata taka k'asa ba ta tako zuwa gareshi fuskarta babu yabo babu fallasa ta tsaya d'annesa dashi kad'an tare da yin sallama.

Ya Sayyadi ya amsa yana fad'in.

"Barka da fitowa".

"Yauwa barka kana lafiya yasu Umma?".

"Duk suna lafiya sunce a gaishe dake".

"Ina amsawa sosai kuwa".

Tayi maganar tare da yak'e har fararen hak'oranta na baiyana a waje.

"Kinyi kyau sosai Amaryata".

Aynu tad'an rufe idonta da tafukan hannunta tana fad'in.

"Nagode sosai".

Ya Sayyadi Umar ya cigaba da fad'in.

"Yanzu hankalina ya kusa kwanciya Aynu kina daf da zama mata a gare ni dama shine babban fatana a kodayaushe, gashi kuma inaji araina Allah ya amsa addu'ata".

Aynu tad'anyi murmushi kad'an ba tare da ta ce komai ba illa wasa data hauyi da yatsun hannunta tana sauraren kalaman da ke fita daga bakinsa wanda a nata b'angaren bazata iya tan-tance ya matsayin kalaman suke aranta ba.

***

"Wai lafiya kake kuwa Magaji, tun dawowarku ka kwanta anan ka kasa motsi?".

"Wallahi Hajiya ina fama da fever ne kawai".

"Ayya sannu !, Allah ya k'ara lafiya".

"Amin Hajiyata".

"Wai kuwa ya batun ciwon Jalilah?".

Yarima Fudhal yad'anyi ajiyar zuciya kafin yace.

"Nidai narasa gane inda matsalarta ta dosa domin duk iya gwaje-gwajenmu bamu gano taka mai-mai abin da yake damunta ba result d'inmu kawai maleria yake bamu".

Fulani Bingel tayi shiru tana kallon Yarima cike da kulawa, kafin ta bud'e baki ta fara magana.

"Anya kuwa Jalilah ba gamo tayi ba?, sati guda abu yak'i ci yak'i cinyewa, kasan mutanan b'oyannan sune ke rik'ewa mutum baki ko k'afa ko hannu ko su toshewa mutum kunne".

"Gamo kuwa Hajiya?".

"E kana mamaki ne?".

"E to zai iya kasancewa, nima abin da nake tunani kenan, amma Hajiya yakike ganin za'ayi?".

"Kuje wajen Mallam Kallah may be a samu addu'o'in da za'a dingayi mata ko Allah yasa a dace bakin ya bud'e".

"Ok hakanma za'ayi bari zuwa gobe da safe idan Allah ya kaimu sai muje ni da Anwar".

"To Allah ya nuna mana goben lafiya, kaje ka kwanta yanzu ka huta kaji ko".

"To Hajiya sai da safe?"

Yarima Fudhal ya fad'a yana mai mik'ewa tsaye ya nufi b'angarensa domin lokacin k'arfe goma na dare ne, gidan shiru kowa yayi makwancinsa sai kukan tsuntsaye kawai da ke tashi.

***

Malam Kallah ne zaune bisa buzunsa yana rubuce-rubuce gefe guda kuma almajirai ne rukuni-rukuni suna tak'ara(karatu).

Yarima Fudhal da Anwar sukai parking motarsu dai-dai rumfar suka fito dukansu zuwa inda Mallam Kallah ke zaune, sallama sukayi suna masu cire takalmansu suka shiga cikin runfar tare da rissinawa suka gaishe da shi, Mallam Kallah ya amsa fuskarsa fal murmushi yana mai aje allon da yake rubutu ajiki ya mai da hankalinsa kacokan kansu Yarima, tare da tambayarsu mutanan gida da kowa, Anwar yace.

"Duk suna lafiya Mallam".

"To masha Allahu, ya Mai Martaba kuma kwana biyu yajini shiru ko?".

"Yana nan lafiya amma ba shine ya aiko mu ba, munzo ne kan batun Jalilah".

Cewar Yarima Fudhal kenan yana mai gyara zamansa ya fuskanci Mallam Kallah, Mallam Kallah ya d'anyi shiru kafin ya bud'e baki ya fara magana.

"E nima ina da niyar ziyartar Mai Martaba domin sanar da shi batu a kan ciwonnata amma tun da kunzo Alhamdulillahi".

"Jalilah zan iya cewa ta taka *SAWON B'ARAWO* ne (littafin Noorieyya), abin da yasa nace haka kuwa jifa aka binne domin wani ya tsallaka sai akayi rashin dace ta tsallaka a daren ita kuma ".

Anwar da Yarima suka dubi juna cike da mamaki, yayin sa Mallam Kallah ya katse mamakin nasu da fad'in.

"Zan baku rubutun AYATUSSHIFA ta d'inga sha tare da shafe jiki insha Allahu da yardar Allah (S.W.A) koma mene zai karye, sannan kai kuma abin da zan fad'a maka".

Yayi nuni da Yarima.

"Kana da mak'iya da yawa a cikin gidanku da waje yawanci jifan da ake yi kai ake yiwa sai dai kuma da taimakon Allah da taimakon Ayatul-kursiyyun da ka rik'e da kuma al-azkar sune suka zamo makami daga gareka don haka kak'ara dagewa wajen al-azkar da tsayuwar dare, domin abin da mu mutane bama ganewa ayanzu wannan Ayatul-kursiyyun da muke rainawa gata dai aya d'aya ce amma maganin da zatayi maka yafi dubu domin ita babbar kariya ce ga duk wani muminin da yarik'eta yana karanta ta ko yaushe dare da rana, sannan abu na gaba azkar muna shagala da yawa tare da barin damarmu a kodayaushe al-azkar nada matuk'ar kariya da muhimmanci  a tare damu, domin idan kayi shi da safe Allah Ubangiji (S.W.A) zai sanya mala'iku  suyita gadinga tun daga safiyya har zuwa yammaci, idan kayi shi da yammaci za'a sanya mala'iku  suyita gadinga daga yammaci har zuwa asuba kagani mutum na cikin kariyar Ubangiji taya tuggun wani bil'adama zai ci shi?, koma mene mutum ya nufoka da shi sai dai ya koma kansa amma ba dai yazo gareka ba, Allah yasa mu da ce yasa mufi k'arfin zuciyarmu ya karemu daga sharrin mak'iyanmu".

"Amin ".

Su yarima suka amsa tare yayin da kowa acikin zuciyarsa yake tunani na daban akan batun da Mallam Kallah yayi musu yanzu.

Sun d'an tab'a hira kad'an, wanda dukkan hirar wa'azi ne gami da nasiha Mallam Kallah keta yi musu, basu bar wajensa ba sai da jikinsu yayi la'asar sosai nasiharsa ta shigesu, sukayi masa sallam tare da karb'an rubutun Jalilah suka nufi gida.

***.               ***.          ***

"Ina fatan kinsanar masa ayi aikin nan da gaggawa ko?".

"Ehh ranki yadad'e, yace ma cikin satinnan komai zai kammala".

"Yauwa haka nake son ji, domin bahaushe ya ce da zafi-zafi akan daki k'arfe, tashi kije sai kin jini".

Larai ta mik'e da tsumar jiki tabar falon Fulani Sokoto, tana fita su Yarima na kawo kai, zama

sukayi gefan Fulani sokoto tare da gaisheta  sannan suka fara sanar da ita dukkan abin da Mallam Kallah ya fad'a musu dangane da ciwon nata.

Fulani sokoto najin cewa Jalilah ta taka asirin da akayiwa wani ne, haba wa sai tamik'e zaune ta fara sababi da masifa.

"Ai wallahi duk ma mai hannu a ciki narantse da Allah da kansa zai bayyana kasan, har ni za'anunawa asiri?, ai ko da guraye mutum yake yawo yayi kad'an yamin haka, karku damu nasan waye yayimin hakan kubar komai  a hannuna".

Yarima da Anwar suka saki baki kawai suna kallonta cike da jimamin jin batun da ke fita daga bakinta.

Anwar ya mik'a mata gorar rubutun yana fad'in.

"Gashi ta dinga sha inji Mallam Kallah ta shafe jikinta, Fulani sokoto takarb'a tare da binsu da wani irin kallo da suka kasa fassara kona menene?.

Mik'ewa sukayi tare da yimata sai anjima suka fito daga falon, suna fita Fulani sokoto taja tsaki tare da dariya tana fad'in.

"Aikin banza aikin wofi har ni za'a nunawa bariki?, ayo asirin sannan a biyo ni da wani munafikin rubutu wai inji Mallam kallah, kuji wani rainin wayo wato a biyo ta hanyarsa a k'arasa kashemin 'yartawa to ba dani ba wallahi Fulani Bingel da ni kike zancen dan nasan wannan duk tuggun ki ne burinki kawai kiga bayana ni da yarana to kafin kiga nawa sai naga naki, wannan abin kuwa zubar da shi zanje inyi wallahi abin da kuka k'ulla sai dai ya koma kanku".

Haka Fulani sokoto ta shafe tsayin lokuta tana ta faman sambatu kamar wata tab'ab'b'iya Jalilah na d'aki tana jinta.

***

"Wai ni kuwa Aynu k
ina ya labarin Yarima Fudhal kuwa?".

"Oho ni ina zan sani?, idan nemansa kike kije gidansu mana".

"A a kawai dai tambaya nayi bai kuma zuwa ba?".

Aynu taja guntun tsaki gami da jefawa Zainab harara.

"Wai ke meye naki a ciki akan Yarima nifa nariga na fidda shi daga cikin rayuwata tun ba yau

ba".

"Ni kam bana tunanin Yarima zai manta dake Aynu".

"To ni namance da shi sai me?".

Tayi maganar cike da masifa, Zainab ta fiddo ido waje tana fad'in.

"A a mai da wuk'ar yi hak'uri kada ki rufe ni da duka".

Dariya suka d'anyi a tare, kafin Zee ta sake fad'in.

"Nifa ina ganin abune mawuyaci Yarima ya hak'ura dake tun yanzu".

"To sai kuma gashi ya baki mamaki ya hak'ura ko?".

"Bana tunanin hakan".

"Kinga Zee mubar maganar Yarima dan Allah kina b'atamin rai muyi abin da ya kawo ni kawai".

"To inajinki meke tafe da ke?".

"Au kinma mance abin da nace zanzo muyi magana akai?".

"Ohh yi hak'uri, yanzu tare kuke da Ya Sayyadin?".

"E mana".

"To bari ind'auko hijab muje to, amma kinsan ni banson bidi'a wallahi abarmu mud'anyi partynmu ko yane, saura kimin buk'ulu".

"A a ni babu ruwana ke da mai bada kud'in".

"E naji dai tashi muje".

Suka mik'e suka fito daga gidan zuwa inda Ya Sayyadi Umar ke tsaye shi da wani abokinsa suna zaman jiran fitowarsu.

*YARIMA FUDHAL*

Na
FIRDAUSI S.A (QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

SADAUKARWA:-Namecy Phirdauceey Jeebour.

32

*Mutane da dama na tambayata wai shin Yarima Fudhal ya hak'ura da Aynu ne koya?, nima dai bani da wannan amsar sai mu jira abin da alk'alamina zai bayar, nagode sosai Masoya iya wuya ana mugun tare*

***

"Wai ina na sanya wannan abin da aka kawomin ne?, inje inzubar da shi yanzunnan domin bansan abin da aka k'ullo a ciki ba".

Cewar Fulani Sokoto kenan tana 'yan dube-dubenta, kafin ta sanya wata 'yar k'aramar Yarinya da ke aiki a wajenta ta kirawo mata Larai.

Mintuna kad'an sai gasu sun dawo tare, Fulani Sokoto ta dubi Larai da fad'in.

"Da kukai gyaran falon nan baku ga wata gorar faro ba?".

"E ranki yadad'e bamu ga komai ba nan falon".

Fulani Sokoto ta cije yatsa tana fad'in.

"Ikon Allah abin da mamaki sosai wallahi, nan fa na tashi na barta jiya namanta shaf ".

Tayi maganar tana mai nuni da gabanta inda take zaune, Larai tace ita dai bata ga komai ba.

"Tashi kuje to".

Suka mik'e suka bar d'akin cikin rawar jiki, Fulani ta dubi Jalilah da duk diramar da ake tana zaune gefe rik'e da waya tana game.

"Ke !, Jalilah".

Fulani ta kira sunanta, Jalilah ta d'ago kai tana duban Fulani.

"Ba kiga gorar faron ba?".

Jalilah ta gyad'a kai alamu E, tsaki Fulani Sokoto tayi cike da takaici.

Yarima Fudhal ne yayi sallama cikin falon ya shigo, Fulani ta nemo wani munafukin murmushi ta d'ora akan fuskarta domin danne b'acin ran da take ciki don ka da Fudhal ya fahimci b'acin komai, Jalilah kuwa ajiye wayar tayi tana mai binsa da kallon fuskarta d'auke da murmushi ta d'an matsa masa inda take zaune, tana yi masa alamun yazo ya zauna.

Yarima Fudhal ya zauna kusa da ita yana gaishe da Fulani tare da tambayar jikin na Jalilah yak'ara da fad'in.

"Da fatan dai tana shan rubutun nata?".

Yak'e Fulani tayi tana fad'in.

"E tana sha mana, abin da babu d'aci bare barci".

Jalilah kuwa kallon Fulanin kawai take yi, Fulani ta mik'e tana fad'in.

"Bari inbarka da k'anwartaka ind'anje Shamaki".

"To a dawo lafiya, nima office zanje yanzu".

Fulani ta fice ta barsu nan zaune, tana fita Jalilah ta d'auki waya tare da shiga wajen text message tayi rubutu kamar haka.

"Yaya Mama fa bata son insha maganin nan".

Ta mik'a masa wayar tare da mik'ewa ta nufi d'aki, mintuna kad'an sai gata d'auke da gorar rubutun ta fito, tana murmushi Fudhal ya tsare ta da tambayar.

"Me yasa bata so kisha?".

Shiru Jalilah tayi domin ta rasa amsar da zata bashi, tana ji a ranta ba zata iya tonawa mahaifiyarta asiri ba, domin tana gudun b'acin sunan mahaifiyarta a idon Fudhal.

Karb'ar wayar tayi ta sake rubuta masa.

"Wai bata yarda da maganin ba zubarwa za tayi, amma dan Allah kada ka nuna mata kasan haka, zan b'oye maganin indinga sha ko wanne magani zaka kawo ka dinga bani zanyi".

Yarima Fudhal ya karanta tare da yin murmushi yana mai duba agogon dake d'aure bisa tsin-tsiyar hannunsa kafin ya dawo da dubansa kan Jalilah yace.

"Karki damu ki dinga sha ab'oyen rubutun nada matuk'ar muhimmanci a tare da ke, lokaci ya k'ure domin nayi late sai na dawo".

Yakai maganar yana mai dafa kanta ya fice da sauri, ajiyar zuciya Jalilah tayi mai k'arfi kafin tayi maza ta koma d'aki ta b'oye gorar rubutun ta dawo dalon ta zauna inda Fulani ta barta.

Sosai Yarima Fudhal ya mai da hankali kacokan kan ciwon Jalilah kullum yana jigilar karb'o mata magani duk da cewa a b'oye yake bata Fulani Sokoto bata sani ba, wasu kuma wajen Fulani Bingel yake a jiyewa kullum idan lokacin sha yayi sai taje ta sha ta koma.

Sai dai tana cike da kokwanto da mamakin yanda a kayi Yarima Fudhal ya yarda da abin da ta fad'a masa ba tare da yayi tunani ko tambaya akan dalilin da yasa Fulani Sokoto ba ta so Jalilah tayi amfani da magungunan da yake karb'o mata ba.

Amma sai dai ta gaza tambayarsa  domin gudun zargi da tsoron wani abu da zai iya zuwa ya dawo.

Cikin sati biyu da fara ciwon nata sosai sauk'i ya fara samuwa sai dai matsalar rashin maganar da tafi damun kowa, amma Fulani Bingel takance ya kwantar da hankalinsa ya cigaba da addu'a sauk'i yana daga Allah.

***

A b'angarensu Aynu kuwa shirye-shiryen biki ake gadan-gadan domin bikin ya rage saura sati biyu a shiga cikin hidimar bikin, su Aynu anraba anko tare da taimakon Zee domin ita Aynu da cewa tayi kowa yasa kayansa amma Zee ta ce ina bazai yiyu ba dole ayi anko kamar yanda ake yi a kowanne biki, INA RUWAN ZAINAB MANYA, K'IRJIN BIKI KENAN.

*(Ni FA BAN GANE BA, ZEE TA KOMA B'ANGAREN YA SAYYADI UMAR NE?, YA ABIN YAKE NE?).*

"Yadai lafiya kuwa kake ta faman kirana a waya?".

Anwar ya fad'a yana mai zama a d'aya daga cikin kujerun da ke gaban table d'in Yarima Fudhal.

"Babu komai rakiya nake so kamin".

"Zuwa ina kenan?".

Yarima ya kafe Anwar da shanyayyun idanuwansa ba tare daya bashi amsar tambayarsa ba ya mik'e tsaye tare da fad'in.

"Kai dai tashi muje kawai".

Anwar ya d'anyi jim kafin shima ya mik'e yad'an zunkud'a kafa yana fad'in.

"Muje to amma fa kamai da ni d'an rakiya wallahi, ko ina nake kome nake yi sai ka kira ni inraka ka wani waje, na kusa samawa kaina mafita nima dai".

Yarima najinsa baitanka masa ba domin yasan duk surutun banza yake yi bazai iya aikata abin da yake ikirarin zai yi ba.

"Kana jina kayi shiru?".

Anwar ya jefa masa tambaya dai-dai sanda suka isa jikin motar Anwar d'in.

"Au wai a motata  za'aje ma?".

Ya sake jefawa Yarima Fudhal tambaya.

"E da a motar wa za'aje?, idan ba taka ba".

Ya bashi amsa yana mai shigewa cikin motar ya zauna, tsaye Anwar yayi yana binsa da kallo.

"Ka shiga muje mana".

"Wai driven d'inma ni zanyi?".

"Kaga malam kafiya k'orafi da surutu dan Allah ka shigo kaja mota muje".

Anwar yayi murmushi a can k'asan ransa yana mamakin hali irin na Yarima, yau ka ganshi fari gobe ka ganshi bak'i kullum da salon halin da zai nuna maka.

"Matarka zatayi fama wallahi".

Anwar yayi maganar yana mai sanyawa motar key, idan kujerar da yake kai tayi magana to shima ya tanka, kwanciyarsa yayi jikin kujerar motar tare da lumshe ido kawai yana sauraron abubuwan da zuciyarsa take raya masa.

Sai da Anwar ya hau babban titi sosai sannan ya juyo fuskarsa ya dubi Fudhal da har lokacin yana kwance ido a lumshe.

"Wai ina zamu ne?, ka barni sai faman tafiya nake".

"Unguwar kwari".

Ya bashi amsa ba tare da ya bud'e idonsa ba.

"Unguwar kwari kuma?, kana nufin gidansu Aynu zamu je?".

Yarima Fudhal ya bud'e ido tare da gyara zamansa kafin ya bashi amsa da fad'in.

"E unguwar kwari zamu je, amma ba gidansu Aynu ba".

"To wajenwa zamuje a unguwar kwarin?".

"Kai dai muje kawai zaka ga wajen wanda zamu je".

Anwar bai kuma cewa komai ba ya juya kan motarsa ya hau titin da zai sada shi da unguwar, a dai-dai bakin layin sukayi parking motarsu, Fudhal ya fito ya tsaya jikin motar yana mai k'arewa layin kallo har Anwar d'in ya fito shima ya kulle motar yana fad'in.

"Sai ina kuma?".

"Ka fiye tambaya ka...!".

Maganar ta mak'ale a dai-dai sanda ya hango Zainab na fitowa daga cikin layin, Fudhal ya fad'ad'a murmushinsa tare da fad'in.

"Yauwa ga Zainab d'innan ma".

Zainab ba k'aramin mamaki tayi ba sanda idonta ya sauka kan Yarima Fudhal, k'arasawa tayi da fara'a tare da sallama.

Fudhal ya amsa yana fad'in.

"Ina Aynu?, wajenta muka zo".

Zee ta d'anyi jim kafin ta bud'e baki ta fara magana.

"Ai nad'auka ka hak'ura da ita wallahi".

"Kamarya kenan, mai yasa kika ce haka kuma?".

"Naga tun randa kukayi rabuwar babu dad'i baka sake nemanta ba, ko layinan ka daina zuwa".

"Aiki ne ya tsare ni".

"Ayya amma ba kada labarin aurenta ko?".

"What..! Aure kuma?, wa zata aura?".

Fudhal ya jero tambayoyin cikin rud'u da tashin hankali.

"Ya sayyadi Umar zata aura, nan da sati biyu masu zuwa".

Yarima Fudhal yayi sauri ya jingina a jikin mota bai sake furta ko kalma d'aya ba, sabida ji da yayi bugun zuciyarsa na k'ara tsananta da bugu fiye da kima.

Zainab bata lura da yanayin da yake ciki ba ta cigaba da fad'in.

"Gaskiya nima banji dad'i ba wallahi, naso a ce aurennan da kai za'ayishi amma babu yanda muka iya haka Allah ya tsara".

"E hakane dama ai matar mutum k'abarinsa inji malam bahaushe, mungode sosai Zainab".

Anwar yayi maganar yana mai dafa kafad'ar Yarima, Zainab tace.

"To ni zan koma gida dama sak'o na kaiwa Aynu sai anjimanku".

"To sai anjima ki gaida Mamanku".

Cewar Anwar kenan, yayin da Zee ta juya tabar wajen.

Anwar ya bud'e mota ya zaunar da Yarima yana fad'in.

"Please ka sanya ranka salama dan Allah kada ka jawa kanka matsala fa?".

Yarima Fudhal ya dubi Anwar da jajayen idanuwansa da suka rine daga fari zuwa ja tsabar d'acin rai.

"Yanzu Aynu zata iya auran wani ba ni ba?, why Anwar mai na aikata haka a rayuwata da SO yake wahalar da ni haka?, wanne zunubi na aikata wa Ubangiji ya jarance ni da irin wannan SO?, har zuwa yaushe ne zan samu muradin raina?, har tsayin wanne lokaci ne zuciyata zata samu abincinta, har yaushe ne idaniya zata samu haskenta?, yaushe ne rai zai huta daga fuskantar barazanar yin bankwana da duniya?, Anwar ka taimake ni dan Allah ina son Aynu wallahi inasonta kamar raina ita ce dukkan burina na duni...! ".

Bai samu damar k'arasa maganarba sabida kukan daya sark'e masa murya, sosai Yarima Fudhal ya bawa Anwar tausayi, yasan zafin so amma bai san zafin yakan kai har wannan matakin ba, ya rasa kalmar da zai lallashi Fudhal da ita hakan yasa kawai ya sanyawa motar key suka bar layin gidan domin ya fuskanci Yarima Fudhal baya cikin haiyacinsa a wannan lokacin.

*YARIMA FUDHAL*

Na
FIRDAUSI S.A(QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCITION®

SADAUKARWA:-Namesy Phirdauceey jeebour.

32

Ganin halin da yake ciki ne ya sanya Anwar mai makon ya kai shi gida sai suka nufi gidansu Anwar d'in, ko da yayi parking motar a parking space ya shafe tsayin mintuna amma Yarima Fudhal ko motsi bai ba ganin da yayi ba shi da niyar fitowa ya sanya shi bud'e b'angaren da yake zaune ya kamo hannunsa ya fito da shi suka nufi part d'in Anwar.

Suna shiga falo Fudhal ya nufi frige kai tsaye ya d'auki gorar faro mai sanyi zai sha Anwar ya karb'e da sauri yana fad'in.

"Kanka k'alau kuwa Yarima ka shiryawa kanka bankwana da duniya ne?".

Fudhal bai kulashi ba ya koma kan kujera ya zauna yana mai da numfashi, ya shafe kusan mintuna talatin a haka Anwar na tsaye gefe yana kallonsa cike da tausaya shi yama rasa mai zai yi masa da zai samu zuciyarsa tayi sanyi a yanzu.

Wunin ranar Yarima Fudhal gidansu Anwar yayi shi haka ya wuni babu ci babi sha, har dai b'arawon bacci yayi a won gaba da shi, bai farka ba sai bayan sallar maghriba, ko da ya farka kaso talatin na daga damuwar da yake ciki a cikin d'ari ya ragu, mik'ewa yayi ya nufi toilet yayo alwala yana fitowa ya shimfid'a sallaya yahau jero salloli bayan idarwarsa ya shafe tsayin lokuta yana addu'o'i fuskarsa cike da hawaye yana nemawa kansa sauk'i a wajen Allah, a haka Anwar yayi sallama ya taddashi , Yarima Fudhal ya sallame daga addu'ar da yake ya dubi Anwar da fad'in.

"Muje ka ajiye ni a gida".

"Ka bari har gobe mana".

"A a yanzu nake so zansha maganina ne".

"To kaci abinci mana, mai za'a kawo maka?".

"Bana buk'atar komai yanzu idan naje gida zanci".

Anwar yasan tunda ya kafe ba zai zauna ba garama kawai ya tashi ya kaishi gidan, Anwar yace

"To shikenan tashi muje".

Domin yasan halin Yarima tunda yasa kanshi tafiya babu yanda za'ayi ya zauna kome zai ce masa kuwa.

A tare suka fito Yarima ya shiga mota ya zauna Anwar yaja suka bar harabar gidan.

Ko da suka isa gidan Anwar yaso sanarwa su Hajiyar Fudhal abin da yake damunsa amma Yarima Fudhal ya kafe a kan kada ya fad'awa kowa, akan dole Anwar yayi shiru da bakinsa sukayi sallama ya koma gida tare da fad'in da safe zai dawo insha Allahu.

Anwar na tafiya a mota wayarsa tayi ringing baiyi niyar d'agawa ba amma ganin number da ke kan screen d'in wayar ya sanya shi d'agawa tare da sanya wayar a handfree.

Daga can b'angaren a kayi sallama tare da fad'in.

"Dan Allah idan babu damuwa ko takura kazo gidanmu yanzu".

Anwar ya d'anyi jim kad'an kafin yace.

"Lafiya dai ko?".

"Lafiya k'alau wallahi, kazo dai kawai".

"Ok ina kan hanyar zuwa gida ne yanzu amma bani mintuna goma sha biyar yanzu zaki ganni a k'ofar gidanku insha Allah".

"To sai kazo, Allah kawo ka lafiya".

Aka katse wayar, Anwar yabi screen d'in wayar da kallo cike mamaki tare da wani guntun murmushi daya mak'ale gefan fuskarsa afili ya furta.

"Yau SAIMA da kanta tana nemana...".

Ya d'an daki sityarin motar yana fad'ad'a murmushinsa cike da jindad'in wannan lokaci.

Kafin ya hau tunanin abin da ya faru tsakaninsa da ita sati uku da suka wuce.

*MUD'AN KOMA BAYA KAD'AN*

SATI UKU DA SUKA GABATA KAFIN WANNAN RANA !.

Zaune Yarima yake cikin office d'insa yana ta faman duba wasu file-file da ke gabansa, Anwar ya turo k'ofa ya shigo tare da sallama Fudhal ya amsa ba tare daya d'ago kansa ba, Anwar yaja

kujera ya zauna yana fad'in.

"Kaga Mallam ajiye aikin nan magana zamuyi mai muhimmanci".

Yarima Fudhal ya rufe wani file daya bud'e ya d'ago kai yana fad'in.

"To Oga ina jinka".

Anwar yayi murmushi kafin yace.

"Koma dai mai zaka ce naji, wani tunani nayi akan Saima".

"Tunani kamar name fa?".

"E to naga Yarinyar ta yarda dani sosai, sai nake ganin kamar infad'a mata gaskiyar abin da yake faruwa kafin k'urewar lokaci ta zo ta sani abubuwa kuma sukwab'e".

Yarima Fudhal yayi shiru kafin ya gyad'a kai.

"Ra'ayinka ne wannan in kaso ta san gaskiyar to, idan kaga baka buk'atar ta sani shikenan, amma zanfi so ka saurari zuciyarka akan abin da take raya maka".

"Nidai nafi aminta da sanar mata ".

"Ok babu damuwa Allah ya taimaka".

Cewar fudhal kenan yana mai da kansa kan file d'in.

"Ni bari inkoma naga yau aiki kake sosai".

"Allah kiyaye".

Yarima ya bashi amsa ba tare daya d'ago kai ba, Anwar ya kama hanya ya fice daga office d'in.

DARE...!
8:30

Da dare misalin k'arfe takwas da rabi Anwar ne tsaye jikin motarsa cikin harabar gidansu Saima, ya shafe tsayin mintuna goma kafin ya hango fitowarta cikin tafiyarta mai kama da wacce bata son taka k'asa, har ta k'araso inda Anwar yake tsaye fuskarta babu yabo babu fallasa .

Sallama tayi Anwar ya amsa mata, tad'an gaisheshi tare da tambayarsa gida da kowa, ya amsa mata da "Duk suna lafiya, suna gaishe ki".

"Ina amsa kuwa".

Cewar Saima kafin shiru ya ziyarci wajen har na wasu 'yan dak'ik'u, Anwar ya katse shirun da fad'in.

"Ina son sanar da ke wata magana amma ina fatan bazaki min mummunar fahimta ba?".

"E insha Allah, fad'i inajinka".

Saima ta bashi amsa agaggauce, Anwar ya cigaba da fad'in.

"Gaskiya Saima nazo wajenki ne ba dan soyayyar gaskiya ba, na zo ne kawai domin injanye ra'ayinki daga kan Yarima Fudhal kuma tare da umarninsa na zo, domin baya son aurenki da shi kamar yanda baya son auransa da Safiyya".

Zuciyar Saima sai da ta buga daga jin wannan zance cike da mamakin jin maganar Saima take bin Anwar da kallo, kafin Anwar d'in ya cigaba da fad'in.

"Amma sai dai tunkafin aje ko ina na kamu da soyayyarki da gaske Saima ina fatan zaki fahimce ni ku...!".

"Kaga dakata Anwar ...!".

Saima ta katse shi cike da b'acin rai kafin ta bud'e baki ta hau fad'in.

"Na fahinci komai Anwar na fahimta, wato ka zo ka yaudare ni ka rabani da wanda nake so da gaske sannan kai kuma ka kama hanya katafi kabarni...uhmm to da kyau hakan nagodewa Allah daya ganar dani gaskiya tun yanzu, amma kafin nan inaso kayi gaggawar barin harabar gidannan tun kafin insa a fid da kai".

"Amma Saima...!".

"Nace ka tafi karabu dani babu wata kalma da zan tsaya ji daga bakin ka !".

Anwar kai ya girgiza kawai tare da kunna motarsa ya shige yabar harabar gidan, yana tafiya Saima ta zube a gun cike da matsanancin kuka, kafin ta koma gida aguje bata tsaya ko ina ba sai kan gadonta ta fad'a tana mai cigaba da ruggar kukanta.

K'arar hon d'in motar da yaji daga bayansa ne ya sanya shi dawowa daga tunanin da yake, murmushinsa yak'ara falala saman fuskarsa domin ko babu komai yana ji a ransa wani abin alkhairi ne zai fari tsakaninsa da Saima.

Bai tsaya ko ina ba sai cikin harabar gidansu Saima, ya kashe motar ya fito  tare da zaro wayarsa daga cikin aljihun wandonsa ya fara neman numberta domin ya sanar mata cewa ya iso.

Mintuna kad'an sai gata ta fito tana takunnata data saba wanda yazame mata jiki a yanzu, Anwar binta yayi da kallo cike da so da k'auna harta k'araso gareshi fuskarta fal murmushi sab'anin lokutan baya daya saba zuwa.

Gaishe shi tayi ya amsa tare da fad'in.

"Gani gareki na amsa kiran ki".

Murmushin kan fuskarta ya k'ara fad'ad'a kafin ta ce.

"Mu shiga daga ciki to".

Tana fad'in haka tayi gaba ya bita abaya kamar rak'umi da akala yau ya cika da mamakin Saima sosai domin yaune karo na farko da tayi masa iso cikin falon saukar bak'i.

Suna isa tayi masa nuni da kujera ya zauna, sannan itama ta zauna table d'in gabansu cike yake da kayan marmari(Fruit) dasu juice kala-kala, Saima ta zuba masa juice a cikin d'aya daga cikin kofunan glass d'in da ke kan table d'in.

Ya karb'a yasha har lokacin binta yake da kallo kamar yanda itama har lokacin murmushin kan fuskarta bai gushe ba.

Gyaran murya tayi tare da sadda kanta k'asa tana wasa da yatsun hannunta ta bud'e baki ahankali ta fara magana.

"Bansan ta inda zan fara ba Anwar, amma hak'ik'anin gaskiya na yarda da maganarka nayi godiya da Allah sosai daya ganar dani gaskiyar Yarima Fudhal baya sona tun kafin ayi aurena da shi, a ranar da ka barni har zuwa kwanakin da suka shud'e nayi kuka sosai tare da addu'a akan zab'in Allah sai dai zuciyata da hankalina sunfi aminta da kai".

Anwar yayi ajiyar zuciya yana mai gyara zama sosai yake jin dad'in kalaman da take har baiso daka tawarta ba, Saima ta cigaba da fad'in

"Bazan b'oye makaba naso Fudhal sosai a rayuwata Anwar, a dalilin sonsa nayarda na zamo baiwa a gareshi domin kawai samun soyayyarsa, sai dai duk da haka ban samu abin da nake so ba, hakan ya saka har asibiti na kwanta Abbana yayi binciken abin da yake damuna Momy ta sanar masa shine dalilin da yasa yaje wajen Mai Martaba domin Yarima ya aure ni sabida soyayyar da yakemin ni kad'aice 'ya a gareshi basa fatan su rasani suna son dukkan abin da nake so kamar yanda suke k'in dukkan abin da nake k'i, ban samu lafiya ba har sai da naji cewa Mai martaba ya yarda Fudhal ya aure ni duk da cewa mu biyu zai had'a amma hakan bai dameni ba domin ina ganin indai zansamu abin da nake so Alhamdulillahi".

"Amma a yanzu na gayawa Abbana kai ne wanda nake so zan aura, na hak'ura da Fudhal nasan shi ba mijina bane har abada".

"Kenan ke ce Saima wadda ke zuwa yiwa Yarima aiki, kuma kece Saima da kikaje wajen Birthday d'insa?".

Anwar ya jera mata dukkan wad'annan tambayoyi lokaci guda, wani guntun murmushi tayi tare da had'iyar wani yawu mai d'aci kafin ta bashi amsa.

"E duk nice Basaja ce kawai nayi domin samun cikar burin raina".

"Har yanzu kina son sa?".

"Ada dai zuciyata ta Yarima ce, amma a yanzu taka ce".

Tayi maganar tana mai rufe fuskarta da tafukan hannunta, wani sanyi dad'i ya tsarga dukkan ilahirin sassan jikin Anwar, da sauri ya mik'e daga inda yake zaune ya koma kusa da ita yana fad'in.

"Da gaske kike Saima?".

Kai kawai ta gyad'a masa domin a wannan lokacin muryar da yayi amfani da ita wajen tambayarta baki d'aya ta kashe mata lakar jiki.

***

Zaune yake cikin falon Fulani Bingel ya takure waje guda ya sanya kansa cikin cinyoyinsa tamkar wani k'aramin yaro, Fulani ce ta fito daga cikin d'akinta ta ganshi a haka da sauri ta k'arasa gunsa ta dafa shi tana fad'in.

"Yadai Magaji lafiya kake kuwa?".

Yarima ya d'ago fuskarsa data jik'e sharkaf da hawaye.

"Subhanllahi...Magaji mai ya faru?".

"Hajiya Aynu ce...! ki taimaka kada ta auri wani dan Allah, wallahi zuciyata zata iya bugawa a kanta...!".

Fulani ta zaro ido waje tana bin Yarima Fudhal da kallaon mamaki kafin ta girgiza kai tana fad'in.

"Mai yasa baka iya sanyawa zuciyarka hak'uri da salama ba Magaji, ka fauwalawa Allah komai kayi addu'a idan Aynu matarkace tabbas saika aureta, idan kuma ba matarka bace kome zamuyi bazaka tab'a aurenta ba, bahaushe yace matar mutum k'abrinsa kuma mahak'urci ai mawadaci ne Magaji dan Allah ka share hawayenka kamar ba namiji ba?".

Yarima Fudhal kai kawai ya girgiza ko kad'an maganganun Fulani basuyi ta siri aransa ba domin shi kada'ai yasan mai yake ji a cikin zuciyarsa.

B'alle boturan rigarsa yayi ya kamo hannun Fulani ya d'ora dai-dai saitin zuciyarsa yana fad'in.

"Kinji fa Hajiya zuciyata zata fashe Hajiya kiyi wani abu dan Allah".

Kafin Fulani tayi wani yunk'uri hawaye yafara bin kan kuncinta domin yanda taji zuciyar Yarima na bugu tare da wani matsanancin zafi da k'irjinsa ya d'auka sosai ta tsorata ainun ido waje take kallon Fudhal ba tare data iya cewa komai ba.

*YARIMA FUDHAL*

Na
FIRDAUSI S.A (QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

SADAUKARWA:-Namesy Phirdausy Jeebour.

Kuyi hkr dan Allah nayi mistake d'in number ne mai makon insaka 33 sai na sake mai maita 32 a wancen page fatan zaku fahimce ni nagode sosai.

34

Zaune yake bisa d'aya daga cikin kujerun falon, gabansa centre table ne cike da kwalaban giya kusan guda biyar gefensa kuma Shisha ce sai karan sigarin dake rik'e bisa hannunsa yana zuk'a lokaci-lokaci.

Idan ya zuk'i sigarin sai ya kora da d'aya daga cikin kwalaban giyar kamar wani tab'ab'b'e.

Tsaki yaja yana mai kashe karan sigarin ya jawo Shisha yahau sha, kafin ya mik'e tsaye yana maiyin ball da shishar tare da d'aga centre table d'in baki d'aya kwalaban giyar suka rotse hatta table d'in ba'abarshi abaya.

Juyawa yayi gefansa ya d'au wata giyar dake gefansa itama ya had'ata da bangon d'akin take ta fashe ruwan giyar na bin bangon.

Komawa yayi ya zauna yana mai cusa hannunwansa biyu cikin sumar kansa yana sosawa tamkar wani mahaukaci sabon kamu, duk wanda ya ganshi a wannan lokacin cikin wannan yanayin dole ya tsorata da shi.

"SAFIYA....!".

Abinda ya furta kenan cikin ihu da k'araji badan babu kowa a harabar ba da babu abin da zai hana mutane shigowa wajensa da gudu.

Mik'ewa yayi cike da layin giya ya nufi hanyar fita daga falon ko takalmi babu a k'afarsa, duk inda ya wuce sai anbishi da kallo sabida yanda yake layi da had'a hanya, bai tsaya ko inaba sai cikin falon Fulani Sokoto yana Shiga ya zube bakin k'ofa.

Fulani da muk'arrabanta dake zaune falon  sukayo kansa suna fad'in.

"Subhanallahi....! lafiya Yarima Jaleel?".

Kama bango yayi yamik'e ba tare da yace dasu komai ba, Fulani na ganin haka ta fahimci halin da yake ciki, umarni ta bawa kowa ya fice aka barta daga shi sai ita sai kuma Jalilah.

Kamo hannunsa tayi takaishi tsakiyar falon ta zaunar dashi tare da jinginashi da jikin kujera kafin ta koma ta zauna tana mai binsa da kallon takaici.

Kafin tamik'e tsaye tana faman safa da marwa Jalilah kuwa sai bin Fulani da Jaleel take da kallo.

Can Fulani ta koma ta zauna tare da sakin wata irin ajiyar zuciya kafin ta bud'e baki ta fara magana.

"Haba Jaleel har yaushe ne zakayi hankali?, yaushe ne zaka nutsu kasan ka girma?, mai yasa kake k'ok'arin ganin ka b'ata gobenka ne?".

"Kullum fad'i tashin da nake akanka ne, ina tufka kana warwara haba Jaleel ka nutsu mana  ko ka samu ka cikamin burina Jaleel".

Duk surutun da Fulani take Jaleel kawai binta yake da kallo amma a zahirin gaskiya ko kad'an maganganun basa tasiri a kwakwalwarsa.

A hankali ya bud'e baki yana fad'in.

"Naji Momy zan daina amma ki taimaka ki auramin wacce nake so nima dan Allah".

Dogon tsaki Fulani taja tana fad'in.

"Au dama akan mace kake son ruguzamin burina Jaleel?, akan mace kake neman b'atawa gobenka", wace ita? fad'amin ko wacece ni kuwa duk yanda zanyi sai na aura maka ita indai har zansamu cikar burina Jaleel".

"Safiya ce ! Momy ita nake so".

"Safiyya kuma ! wacce kenan?".

"Gimbiya Safiyya Momy".

A razane Fulani take bin Jaleel da kallo cike da rud'u da tashin hankali, ba Fulani ba har Jalilah dake zaune gefe tana jinsu ta girgiza dajin batun da Jaleel yazo da shi.

"Jaleel kana cikin hankalinka kuwa?".

"E Momy nidai ita nake so, idan na rasata zan iya rasa rayuwata Momy".

"Amma dai ina kasan angama magana Fudhal zata aura".

"Nasani Momy amma tun farko nine nake sont.....!".

Bai kai ga k'arasa maganarsa ba sai jin k'arar saukar maruka yayi a duka kuncinsa guda biyu, cikin firgici ya dafe fuskarsa yana bin Fulani da kallo bai kuma magana ba yami'e cikin layi ya fice daga falon.

Fulani ta koma kan kujera tazub'e dab'as zuciyarta na suya da k'una akan maganar da Jaleel yazo mata da ita yanzu har ace yau Jaleel ne take fad'a yana fad'a.

"Meke faruwa ne?".

Abin da ta furta kenan cikin ranta da sauri ta mik'e tsaye kamar antsikareta duban Jalilah tayi tana fad'in.

"Maza jeki saka a kirawon Larai...au namanta kefa baki da baki yanzu".

Takai maganar tare da jan tsaki, mik'ewa tayi ta fice daga falon tabar Jalilah zaune.

Kwance yake kan carpet ya d'ora kansa bisa kusun idonsa a lumshe kamar mai bacci amma a zahiri ba baccin yake ba, domin daka kalli gefan idonsa ruwan hawaye zakaga yana fita lokaci-lokaci, can ya mik'e zumbur kamar antsikareshi yana mai dafe kansa da yake sara masa d'aga kai yayi ya dubi agogo lokacin k'arfe tara na dare 9pm.

Toilet ya nufa ya wanke fuskarsa yana fitowa yayi waje zuwa harabar gidan, yana tafe zuciyarsa na cigaba da tsananta bugu amma duk da haka ya d'aure harya k'arasa bakin k'ofar falon da sallamarsa yasa kai cikin falon ba tare daya nemi iso ba.

Mai Martaba na kishingid'e a falo yaji sallamar Fudhal d'in tare da shigowarsa, murmushi ya fad'ad'a a fuskarsa Mai Martaba yamik'e zaune yana fad'in .

"Zonan zauna Magaji, kamar kasan yanzu nake zancen insaka a kirawomin kai".

Yarima Fudhal yayi k'ok'arin nemo murmushi ya d'ora a kan damuwar dake kan fuskarsa, ya durk'usa ya gaishe da Mai Martaba tare da gyara zama danjin mai zai ce.

Gyaran murya Mai Martaba yayi yana fad'in.

"Munyi magana da Iyayen Saima sunce sun janye maganar aurenka da 'yarsu, sannan kuma muntsai da bikinka kai da Safiyya nan da sati biyu masu zuwa hakan yayi maka ko a k'ara?".

"Duk yanda kukayi dai-dai ne Abba, amma ina da 'yar magana akan batun auren".

"Babu damuwa ina jinka fad'i".

"Abba ka taimaka dan Allah bawai zanyi jayayya da kai bane na yarda zan auri Safiyya amma ka yarjemin in auri Aynu dan Allah Abba".

Mai Martaba bin Fudhal yayi da kallo kawai yana gyad'a kai kafin yayi murmushi yana mai fad'in.

"Nima a matsayina na Mahaifinka zan umarceka da abu guda d'aya a yau koda bayan raina kada d'ayanku yayi gangancin had'amin zuri'a da talaka !".

Cike da mamaki Fudhal yake bin Mai Martaba da kallo yarasa wacce irin k'iyayyace Abban nasu keyiwa talaka haka?, ya bud'e baki zaiyi magana kenan sai ganin fad'owar mutum sukayi cikin falon.

Jaleel ya tako da Sauri ya zube gaban Mai Martaba tare da kama k'afarsa yana fad'in.

"Dan Allah Abba kada ayi auren nan wallahi Abba nine nake sonta Momy ce tace kada nafad'a inbari a aurawa Broda".

"Kai lafiyarka kuwa?, akan wa kake magana ne?".

"Gimbiya Safiyya Abba itace wadda nake so dan Allah Abba a auramin ita ni nafi dacewa da ita ba Fudhal ba".

Mai Martaba mik'ewa yayi tsaye yana mai bin 'ya'yan nasa da kallo kafin ya koma ya zauna yana fad'in.

"Wato kuna so kumai da ni k'aramin mutum ko?, mai yake damun kune?, kai da nake ganinka mai hankali Magaji ashe kallon kitse nakewa mai?".

"To kutsaya kuji ni da kyau ko bayan raina babu kai babu auren 'yar matsiyatarnan Magaji aurenka da Safiyya kuma babu fashi, kai kuma Jaleel ko zaka mutu bazan tab'a canja maganata ba akan ka dai, yaushema kake da hankalin da zanyi maka aure yanzu kana tunanin duk abin da kake aikatawa bani da masaniya a kai?, Ku tashin kuficemin daga nan kada insake jin Wanda yazomin da makamanciyar irin wannnan maganar".

"Ku b'acemin daga nan nace...!".

Yayi maganar cikin tsawa ba shiri suka mik'e suka fice kowannansu zuciyarsa cike k'una da b'acin rai.

Babu wanda ya tankawa wani har suka isa part d'insu kowa ya nufi d'akinsa.

Yarima Jaleel dai yana shiga d'aki fridge ya nufa ya d'auko kwalaban giyarsa yahau sha babu ko k'ak'k'autawa bare yayi tunanin zata iya illata shi.

Fudhal kuwa yana shiga d'akinsa kwanciya yayi bisa katifarsa yana juyi yayin da zuciyarsa ke cigaba da tsananta bugu tare da zafi.

Har kusan k'arfe biyun dare amma al'amarin nasa babu sauk'i sai da takai takawoma juyinma da k'yar yakeyinsa.

Jiyayi amai na taso masa da rarrafe ya shige toilet amma sai aman ya koma, nan yayi k'arfin halin mik'ewa yana dafa bango har ya fito daga toilet zuwa tsakar d'aki anan ya yanke jiki ya fad'i numfashinsa na fita sama-sama.

Hello

My luvly fans
Har yau dai bazan gajiya da baku hak'uri ba, abubuwane suka rik'eni amma yanzu alhmdlh insha Allahu indai ba wani uzuri mai k'arfi ba kullum zaku dinga samun post nawa da yardar Allah har Allah ya nunamin inkammala muku ngd sosai masu call & message kuma raina iya wuya ana tare.

Bissalam

*YARIMA FUDHAL*

Na
FIRDAUSI S.A (QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

SADAUKARWA:-Namesy Phirdausi Jeebour.

35

5:00AM

Har aka kira sallar asuba Yarima Fudhal yana ji amma ya gagara tashi wayarsa dake can kan

katifa sai faman ringing take yi har tagaji ta katse.

Fulani Bingel na shirin shiga toilet domin ɗauro alwala wayarta tahau ringing hakan yasa tayi saurin ɗagawa domin ba k'alamin faɗuwar gaba taji ba alokacin aranta ta furta.

"Ko waye ke kirana da asubar nan Allah yasa dai lafiya?".

Tayi maganar tana mai ɗaga wayar tare da karawa bisa kunnanta.

Daga can ɓangaren aka amsa da faɗin.

"Hello Hajiya lafiya kuke kuwa?".

"Lafiya ƙalau Sadiya  wani abune ya farune naga kiranki da asubar nan?".

"Wallahi Hajiya hankalina ya kasa kwanciya ne tun jiya da dare nake kiran wayar Fudhal baiyi picking ba, yanzuma sai da na kira amma bai ɗaga ba".

Fulani take taji gabanta ya tsananta faɗuwa amma ta daure ta bata amsa da faɗin.

"May be yana bacci ne, idan ya farka nasan zai nemeki".

"To amma dai Hajiya kisa adubo shi".

"Insha Allah bari inyi sallah".

Fulani ta katse wayar tare da shigewa toilet a can kasan zuciyarta kuwa addu'a kawai take ta faman zubawa domin tasan cikin kwanakin nan kaf baya cikin nutsuwarsa ita al'amari nasama bakaramin tsoro yake bata ba.

A gaggauce ta ɗauro alwalar ta fito ta shimfida abin sallah ta tayar da sallah.

Ta nayin sallama ta fito daga ɗakin domin zuwa dubo Fudhal sabida zuciyarta ta kasa jurewa.

Gidan shiru babu kowa har ta isa part ɗin nasu, kofar ɗakinsa buɗe dan haka kai tsaye ta sanya kai cikin falon ta nufi bedroom ɗinsa tana sa kai ta hangoshi kwance tsakar ɗakin sai nunfarfashi yake sama-sama da gudu ta karasa wajen tana faɗin.

"Subhanallahi...! Baka da lafiya Magaji?".

Ta karasa Kansa kenan ta ɗago shi sai ga Anwar ya faɗo ɗakin shima  shine ya taimaka mata ya miƙar dashi tsaye sai lokacin suka lura a she aman jini yake yi da basu lura ba da yake dumm light ne a ɗakin da sauri sukayi waje da shi Anwar ya sanyashi a mota sannan ya juyo ya kalli Fulani yana faɗin.

"Bari in wuce da shi asibitin kafin ki sanar da Mai Martaba domin yana bukatar taimakon gaggawa".

Bai jira jin amsartaba ya shige mota yaja da gudu yabar harabar gidan, Hajiya ta koma ciki da sauri kai tsaye shashin Mai Martaba ta nufa ta Sanar dashi halin da ake ciki.

Nan da nan aka tashi driver suka bi bayan Anwar.

Anwar bai tsaya a ko inaba sai a NANAH KHADIJAH PRIVATE HOSPITAL kai tsaye Emergency aka nufa dashi.

Anwar ya kasa zaune ya kasa tsaye sai safa da marwa yake, a haka su Mai Martaba suka taddashi abinka da masu gari office ɗin Babban Doctor aka kai Mai Martaba ya zauna tare da Hajiya idan banda addu'a babu abin da ko wanne daga cikinsu yake yi cikin ransa.

Likitoci sun shafe tsayin a wanni biyar akan Yarima Fudhal kafinsu samu nasarar dai-daita numfashinsa dake barazanar yin bankwana da duniya.

Babban likitan ya fito yana share gumi ya nufi cikin office ɗinsa inda ya barsu Mai Martaba na zaman jiransa.

Ya bude wani file yayi ƴan rubuce-rubucensa kafin ya ɗago kai yana binsu da kallo ya bude baki a hankali yana faɗin.

"Ya akayi kuka bari yana wasa da bin ƙa'idojin shan magani?, nasan kunsan illar dake tattare da ciwonsa, ga kuma damuwa daya sanyawa ransa da yawa Wanda yin hakan na daf da Ku iya rasashi baki ɗaya".

Mai Martaba da Hajiya bin Doctor kawai sukeyi da kallo domin basu fahimci maganarsa ba.

"Amma Doctor mene kake magana akai haka?".

Cewar Mai Martaba kenan yana mai bin fuskan Doctor ɗin da kallo.

"Kamar ya?, kuna nufin kuce bakusan ciwon dake damun ɗanku ba?".

Doctor yayi maganar yana mai jingina a jikin kujerar da yake kai, tare da ƙare masu kallo ɗaya bayan ɗaya.

"E gaskiya bamu sani ba, amma kada kaga laifinmu abisa hakan domin ba anan ya girma ba".

"OK a takaice dai ɗanku na ɗauke da ciwon zuciya ne wanda ya kai matakin ƙarshe da zai iya rasa ransa".

A tare Mai Martaba da Fulani Bingel suka mike, Fulani inbanda innalillahi wa'inna ilaihi razi'un babu abin da yake fita daga bakinta.

Anwar dai na gefe ya rasa abin da zai ce sosai yake jin tausayin Yarima Fudhal cikin ransa.

Doctor ya buɗe baki ya cigaba da faɗin.

"Ku zauna insha Allahu babu wata matsala munsamu dai mun dai-dai ta tsayuwar nunfashinsa, amma munaso musan dalilin daya haddasa masa wannan ciwon, sannan kuma munaso musan WACECE AYNUL-HAYAT?, da dukkan alamu soyayyartace ta jefashi cikin wannan yanayin?

sabida bakinsa babu abin da yake furtawa sai ita".

Anwar dake tsaye gefe neman guri yayi ya zauna yana mai lumshe idanuwansa da sukeyi masa zafi sosai, yanason yin magana amma ya gagara furta ko kalma ɗaya.

"Doctor ciwon ya jimane a jikinsa ?".

Cewar Fulani kenan tana mai goge kwallar dake kokarin zubo mata.

"E to a bincikenmu ciwon ya kai tsayin shekaru goma zuwa goma sha uku".

Shiru office din ya ɗauka naɗan wani lokaci kafin Anwar ya katse shirun da faɗin.

"Nasan dalilin ciwon nasa !".

Nan Anwar ya bawa Doctor labarin dalilin samun ciwon zuciyarsa ya kara da faɗin.

"Aynul-hayat da kaji yana faɗi itace yarinyar da yake so, kuma sonta ne dalilin tsanantar ciwon nasa".

Doctor yayi shiru tsayin wani lokaci suna kallonsa kafin ya fara rubuce-rubuce cikin file ya ɗago yana kallon Mai Martaba.

"Duk yanda za'ayi indai kuna son ɗanku to dole ne idan ya farka ya fara tozali da abin da ya sakashi a cikin wannan halin idan kuwa ba haka ba zan iya cewa sai dai kuyi hakuri da shi !".

Cikin fushi Mai Martaba ya mike yana faɗin.

"Kana nufin inje innemawa Magaji auren ɗiyar mutsiyata?, ina bazai yiyuba duk yanda zakuyi kuyi amma auren Magaji da wannan yarinyar bazan taɓa lamunta ba".

"Kayi hakuri Mai Martaba halin da yake ciki zamu duba..!".

"Dakata Doctor...! Ni bana magana biyu, ina roka masa Allah ya bashi lafiya amma aure babu shi da waccan yarinyar ko bayan raina".

Yana faɗin haka ya saka kai ya fice daga office ɗin, Anwar da Doctor suka bi bayansa da kallo, Fulani kuwa nan tayi zaune tana sharar kwalla.

*YARIMA FUDHAL*

Na
FIRDAUSI S.A (QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

SADAUKARWA:-Namesy Phirdausi Jeebour.

36

Doctor ya dawo da dubansa kansu Anwar tare da ajiyar zuciyar yana faɗin.

"Gaskiya Hajiya kusan yanda zakuyi Ku nemawa Yarima Fudhal abin da yake so, domin yin hakanne kaɗai zai iya taimakawa wajen cetonsa daga halin da yake ciki sai kuma addu'a wadda ita yafi buƙata a halin yanzu".

Anwar ne yayi ƙarfin halin faɗin.

"Zamuyi ƙoƙarin ganin munshawo kan Mai Martaba insha Allahu, yanzu zamu iya zuwa mu ganshi?".

"A a sai dai ko zuwa gobe idan Allah ya kaimu munga yanda yanayin jikin nasa zai kasance, yanzu zaku iya tafiya gida".

Ya kai maganar yana mai miƙewa domin fita daga office ɗin, Anwar da Hajiya suka take masa baya.

Sai da ya kai Hajiya gida sannan ya wuce gidansu.

Tun kafin Hajiyarsu Fudhal ta dawo labarin ciwon Fudhal ya baza cikin gidan, tana Shiga falonta aka fara zuwa gaisuwa tare da gamba tambayar jikin Fudhal.

Ɓangaren Fulani Sokoto kuwa bazaka iya tantance halin da take ciki ba farin ciki ko baƙin ciki ?, amma anawa hashashen zan iya cewa Fulani Sokoto farin ciki ne fal cikin ranta akan ciwon Fudhal domin tana ganin kamar mutuwa zaiyi idan kuwa babu fudhal magajin sarauta dole Yarima Jaleel ne , sai dai tsananin damuwar da Yarima Jaleel ya jefata shike danne farin cikin da take ciki.

Mai Martaba kuwa ranar ko fada bai zauna ba idan banda safa da marwa babu abin da yake a falonsa, a wannan halin ne Fulani Bingel ta taddashi ta nemi guri ta zauna shima ya zauna ba tare da kowanne daga cikinsu ya furta ko kallama ɗaya ba.

Daga can Fulani Bingel ta katse shirun tana faɗin.

"Amma ina ganin kamar hukuncin daka yanke akan ɗanka yayi tsauri, kada ka zamo ɗaya daga cikin iyaye masu tauye haƙƙin ƴaƴansu daya rataya a wuyansu, kasan dai Magaji yaro ne mai ladabi da biyayya Wanda baya tsallake dukkan dokar da muka kafa masa, amma ya kamata sau ɗaya dai shima ka bashi dama ya samu farin cikinsa, kamar yanda ya kasance yana faranta mana tsayin shekarun, kayi hakuri idan na faɗi kalma ɗaya data ɓata maka rai ka gafarce ni na barka lafiya".

Fulani ta miƙe tana mai ficewa daga ɗakin, tabar Mai Martaba nan zaune kamar ta jona masa wutar lantarki, a can kasan zuciyarsa yasan gaskiya ta faɗa sai dai shi bayajin a ransa zai iya

jure haɗa zuri'a da jinin talaka".

Al'amarin Yarima Jaleel kuwa ranar wuni yayi a ɗaki baiko leƙo waje ba inbanda bankawa Kansa kayan maye babu abin da yake yi ya zama tamkar wani mahaukaci hakan yasaka bai San wainar da ake toyawa ba a cikin gidan.

" Wai Hajiya mai yasa Magaji ba zai iya haƙura da yarinyar nan bane?, tunda Abba ma baya so sai kace dole?".

Cewar Sa'ida kenan, Aunty Sadiya dake zaune gefe tana shirya 'yan biyunta tayi murmushi kafin ta bata amsa.

"Kema dai Sa'ida kamar baki san al'amarin so ba?, ko kaɗan bana ganin laifin Magaji ina tausayawa rayuwarsa sosai wallahi, Abba mahaifine agaremu amma shine da laifi daya hakura anyi auren nan da duk hakan bata kay ba da nasan babu wanda zai san Magaji nada ciwon Zuciya".

"Ni kuwa kinsan abin da yake bani mamaki Aunty Sadiya?".

"Aa".

"Cewa da akai sanadin ciwon akan matsalarsa da iyayenta ne, abin da yafaru tsayin shekaru dasu ka wuce sai kuma gashi ya mace akan son ɗiyarsu".

"Babu wani abin mamaki da ikon Allah Sa'ida, domin Allah baya yafe laifin wani akan wani, mahaifinku yayi kuskure Sosai awancen lokacin sakayyace kawai take bibiyarmu amma har yanzu ya gaza fahimtar hakan, ".

Fulani Bingel ta bata amsa tana mai share kwallar dake kokarin zubowa daga befan idonta, Jalilah dake zaune gefe tana jinsu tana son cewa wani abu amma babu dama, hakanne ya sanyata fashewa da kuka musamman idan ta tuna irin ƙiyayyar da suke masa su da mahaifiyarsu sai gashi shine yafi kowa damuwa da ciwonta.

Mikewa tayi da gudu ta fice daga falon ta nufi part ɗinsu tana Shiga kai tsaye ɗakinta ta wuce ta faɗa kan gado tana mai cigaba da rera kukanta sai da tayi kuka mai isarta kafin ta mike ta shige toilet ta wanko fuska ta dawo tana mai zama gefan katifarta tayi ta gumi tana aikin tuananin neman mafita akan wannan al'amarin.

A can ƙasan zuciyarta tana son warwarewa Abban nasu wata sarkakiya sai dai tana gudun jawa mahaifiyarsu tsana a gun Mai Martaba da kuma yan'uwansu tare da tsoron yanda Mai Martaba zai ɗauki batun.

Tun da aka kwantar da Yarima Fudhal ko dan yatsansa baya iya motsawa domin baima San a duniyar da yake ba, yana rayene amma kamar matacce ban-bancinsa da matacce ɗaya ne shine numfashi ko numfashinma ta computer dake gefansa ne kawai zaka kalla kasan yana da rai.

Ranar dasu Aunty Sadiya sukaje babu wanda baiyi kuka ba cikinsu musamman Jalilah rungumeshi tayi tana aikin kuka har sai da aka janyeta.

Ranar suna dawowa basu wuce ko inaba sai part din Abbansu domin su roƙeshi ya sauko daga dokin naƙin da ya hau, amma fafur yaƙi daga ƙarshema korarsu yayi dukansu suna kuka suka baro falon nasa, sai bayan fitarsu kuma jikinsa yayi sanyi sosai hardai daya tuna maganar Aunty Sadiya ta ƙarshe kafin ya koresu.

"Abba kayi hakuri dan Allah bawai munzo ne akan dole ka yarda Magaji ya auri wacce baka so ba, munzone akan ka taimaka kaje ka ganshi koda sauɗayane domin yana bukatar addu'arku sosai, ya kamata ka janye daga fushin da kake da shi ko yasamu wani sassaucin na ciwon nasa, sabida fushin iyaye babbar masifa ce ga ɗansu".

"Bayan haka Abba ka gafarce ni abisa abin da zan fada yanzu duk da nasan dole maganar zata ɓata maka rai".

Shiru tayi naɗan wani lokaci kanta a ƙasa kafin ta cigaba da faɗin.

"Abba mene dalilinka naƙin talaka haka?, talaka baya da gata aduniya ne?, shin talaka ba mutum bane kamar kowa?, Shifa Ubangiji babu ruwansa da talaka ko mai kuɗi, sarki ko malami shugaban kasa ko gwamna yaro ko babba duk ɗaya suke a wajen Allah ban bancinsu kawai shine Wanda yafi tsoransa, Abba kasani shifa arziki da mulki ba madogara bane domin ko babu mutuwa akwai tsufa Abba, a matsayinka na shugaba idan baka kyautatawa al'ummar da kake mulkaba taya kai ma zakayi tunani Allah zai kyautata maka, Abba......".

"Ke...! Dakata kinfi ni sanin haka ne?, ko kuwa kinaso ki nunamin kinfini sanin ya kamata, Fudhal ɗa nane nike da iko inyanke dukkan hukuncin da naga dama akansa, Ku tashi Ku

ɓacemin da gani sha-shan yara kawai...".

Yana zuwa nan ya runtse ido sosai yaji ransa na suya da ɗaci akan abin da ya aikatawa ƴaƴan nasa, sai dai shima baya da masaniya akan dalilin da yasa yake musu hakan, amma har ga Allah yasan gaskiya ta faɗa.

"Mene dalilina akan tauyewa ƴaƴana haƙƙin abin da suke so?".

"Son zuciya...!".

Ya bawa kansa amsa, girgiza kai yayi cike da takaici, yana daga idonsa kasan carpet yayi to zali da wata takadda yasa hannu ya ɗauka ya buɗe a hankali rubutu ya gani ciki da bayan takaddar, haka kawai yaji aransa ya kamata ya karanta domin ya ji abin da ta kusa.

*YARIMA FUDHAL*

Na
FIRDAUSI S. A (QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

SADAUKARWA:-NAMESY PHIRDAUSY JEEBOUR.

37

Ga abin da wasiƙar ta ƙunsa.

"Assalamu alaikum.

Abba ina mai baka haƙuri akan abin da zan faɗa bana fatan ko kalma ɗaya tasanyaka fushi sai dai fatan ka fahimce ni, kayi hakuri Abba ka yafewa Fudhal kasa ni shi dan Adam ajizine baya da masaniya akan abin da zai aikata domin komai ya faru ga bawa dama can rubutacce ne, Abba ni na sani dukkan abin da yake faruwa tsakanin Fudhal da Jaleel akan Gimbiya Safiya wallahi Abba sa hannun maƙiya ne kayi haƙuri ka fahimci ko wanne daga cikin su ka daure kaje ka dubo Fudhal kaga halin da yake ciki bawai ina faɗin ka amince masa da auren wacce baka so ba a'a fatana kaje kaga halin da yake ciki may be zaka iya sanin hukuncin da zaka yanke akan haka.

BISSALAM".

Sarki Ubaiyd ya karanta wasiƙar kusan sau biyar tare da shafe tsayin lokuta yana jujjuya wasiƙar sosai jikinsa yayi la'asar, yayin da ƙasan zuciyarsa ke azalzalarsa da ƙin yarda da batun sai dai yayi nasarar yaƙar kasan zuciyartasa ɗari bisa ɗari.

WASHE GARI

Washe gari tun misalin ƙarfe bakwai Fulani Bingel da Fulani sokoto suka shirya domin zuwa dubo halin da Yarima Fudhal yake ciki.

Jalilah ma ba'abarta a baya ba, domin da kanta ta Shiga kitchent ta ɗanyi masa girki mai ruwa-ruwa yanda mara lafiya zai iya ci.

Fulani Bingel ta dubeta sai faman tiri tiri take da kwandon kayan abinci guntun murmushi tayi kafin ta dafa ka faɗarta.

"Jalilah girki ki kayi masa ne?".

" E Hajiya ".

"Ayya baki San haryanzu bai dawo haiyacinsa ba?, baya cin komai Jalilah mai da abincin kizo mutafi".

Takai maganar dai-dai sanda driver yayi parking a gabansu suka shiga Jalilah kuma ta bawa

ɗaya daga cikin dogarawan dake yawo a farfajiyar gidan kwandon kayan abincin ta shige mota itama suka tafi.

Ko da suka isa asibitin can suka tadda Aunty Sadiya tuni ta jima da zuwa ma, Aunty Sa'ida ce sai bayan da sukaje sannan ta je ita ma.

'Yan dubiya ne suka fara sallama daga wannan ya fita sai kaga wasu sun shigo duk da cewa ba'a aganinsa sai dai ka leka ta glass ɗin windown ɗakin da yake kwance kamar gawa ansanya masa oxygen babu wani abu dake motsi a jikinsa sai saitin zuciyarsa da ake iya ganin bugawarta ya rame sosai kai kace yayi shekaru irin biyun nan a kwance.

Mai Martaba na kishingiɗe bisa kusun Jakadiyya tayi sallama a ruɗe ta shiga tana mai zubewa kasa tare da faɗin.

"Mai Martaba Yarima Jaleel fa na daf da rasa hankalinsa yayi Marisa sosai Yallaɓai...!".

Mai Martaba miƙewa yayi bai jira karashan maganarba kai tsaye ya fice daga ɗakin Jakadiyya ta biyo bayansa da sauri.

Tunda yasa kafa falonsa yake cin karo da kwalaban giya da karan sigari dakin inbanda wari babu abin da yake yi, Yarima Jaleel na kwance sharkaf tsakar ɗakin sai amai ne ke fita daga bakinsa mai warin tsiya.

Juyowa yayi yana duban Jakadiyya yace.

"Asamu a gyarashi akaishi a sibiti".

Yana faɗin hakan ya fice daga ɗakin ya koma part ɗinsa.

"Wacce irin ƙaddara ce wannan?, mene ya jamin hakan?".

Mai Martaba ya faɗa cikin ransa tare da cigaba da zaga falon, kafin ya shige bedroom ɗinsa domin shiryawa.

Ana isa da Yarima Jaleel asibiti shima kai tsaye emergency aka nufa dashi.

Suna zaune sai ganin faɗowarsa cikin ɗakin kawai sukayi, binsu yayi da kallo ɗaya bayan ɗaya kafin ya sauke idonsa kan Yarima Fudhal dake can kwance, karasawa yayi jikin win windown yana kare masa kallo sosai tausayin ɗan nasa ya kamashi take yaji zuciyarsa ta karye jiyayi ba zai iya jurar rasa ƴayansa maza har biyu ba waɗanɗa sune magada a bayansa.

Duban Anwar yayi dake zaune kan wata farar kujera.

"Ka same ni a waje".

Ya Sakai ya fice Anwar yabi bayansa da sauri.

A office ɗin Doctor ya taddashi anayi masa bayani kan batun Yarima Jaleel.

Bayan ya gaishe dasu Mai Martaba yace ya zauna suka cigaba da maganarsu.

"Yanzu wanne halin yake ciki to?".

"E to yanzu dai munyi masa allurar bacci sai idan ya samu relief ya farka zamu San abinyi domin ya bugu ne sosai har kwayoyin da yake sha sunfara barazanar taba masa kwakwalwa".

Mai Martaba yayi shiru tsayin wasu lokuta kafin ya buɗe baki yana mai cigaba da faɗin.

"Ya batun Magaji kuma?, yaushe ne zai farfaɗo?".

"Jikinsa alhamdulillahi ana samun nasara sosai, zai iya farkawa nan da kwana hudu ko biyar idan zuciyar tasa taɗan samu relief sai dai abu guda ɗaya, duk yanda za'ayi dole ne idan ya farka ya fara sanya ido akan abin da yafi so idan ba hakaba za'a iya samun matsala domin ciwon zuciyar tasa ya taka matakin ƙarshe na rayuwa ko mutuwa?".

"Karka damu insha Allah zamu San abinyi".

Doctor ya mike ya fice daga office ɗin domin zuwa duba wasu patients nasa ya barsu nan suna tattaunawa da Anwar.

Mai Martaba ya gyara zama yana mai duban Anwar tare da cewa.

"Anwar...!, Ina so ka bani labari akan yarinyar da Magaji yake so bana so ka ɓoyemin komai dan Allah".

Fudhal ya gyaɗa kai alamun ya fahimta nan ya kwashe komai tun daga farko har ƙarshe bai ɓoye masa komai ba ya sanarmasa.

Mai Martaba ya da ɗe tsayin wani lokaci yana gyaɗa kai tare da jinjinawa al'amarin jikinsa yayi sanyi ainun.

"Haƙƙina nane innemawa Magaji auren yarinyar da yake so...!".

Anwar duban Mai Martaba yahauyi baki galala cike da murna da farin ciki amma daya tuna ankusa bikinta sai jikinsa yayi sanyi da ƙyar ya iya ɗaga harshensa ya furta.

"Abba ankusa bikinta fa !, Inajin baifi nan da sati guda ba".

"Kada ka damu zansan abinyi insha Allah Magaji ne mijinta".

Anwar yaɗanyi yaƙe kawai tare da sauke ajiyar zuciya ba tare da yayi yinƙurin sake cewa komai ba.

*7:2pm*

Bayan sallar maghriba misalin ƙarfe bakwai da mintuna biyu Umman Aynu da Babanta suna zaune tsakar gidansu suna hira tare da tattauna yanda zasu tafi da al'amuran bikin ɗiyarta tasu tilo.

Aynu na cikin ɗaki kwance kan tabarma kanta na bisa pillow tayi ruf da ciki kai kace bacci take, amma azahirin gaskiya idonta biyu ba zaka tabbatar da hakan bama sai ka lura da kai hannunta da take kan fuskarta tana share kwallar dake taruwa cikin idonta lokaci zuwa lokaci.

Har cikin ranta bata jin son auren nan nata da za'ayi a cikin ranta ba tajin zata iya rayuwa da kowa idan ba Yarima Fudhal ba.

Sallama suka jiyo ƙofar gida Baban Aynu ya sanya takalmansa ya fita domin ganin mai sallamar.

Dogarawan Sarki Ubaiyd ya gani tsaye bakin ƙofar gidan suka gaisa tare da faɗin.

"Sarki Ubayd na da buƙatar ganinka a dai-dai wannan lokaci".

"To...! Lafiya dai ko?".

"Koma dai menene idan kaje za kaji".

Ɗaya daga cikin su ya bashi amsa, Baban Aynu ya gyaɗa kai tare da faɗin.

"Bari inshiga ciki insanarwa iyalina".

Yana shiga ciki bai ƙarasa inda Umman take zaune ba yahau faɗin.

"Zanje gidan Sarki yana nemana yanzu zan dawo".

Tsaye Umma ta miƙe tana faɗin.

"Allah yasa dai lafiya?".

"Amin bari inje inji".

Ya fice ya barta nan tsaye, Aynu ta fito da sauri domin jin me yake faruwa?.

Suna tafiya basu tsaya ko ina ba sai ƙofar falon Mai Martaba sukayi sallama ya basu izini su shiga.

Suna sanya ƙafa Baban Aynu sakar baki yayi yana kallon falon tare da aiyana irin dukiyar da aka kashe a ciki, suka sunkuya tare da kwasar gaisuwa Mai martaba dake zaune bisa ɗaya daga cikin kujerun dake falon ya amsa tare da basu umarnin su basu guri, ba musu kowa ya fice falon ya rage daga Baban Aynu sai Mai Martaba kawai.

Gyaran murya Mai Martaba yayi tare da gyara zama kafin ya bude baki ya fara magana.

"Nasan zakaji mamaki sosai da kiranka da nayi a dai-dai wannan lokaci, hakan ta faru ne sabida kafiya da naci irin na yaran zamani".

Yaɗanyi shiru na wani lokaci kafin ya cigaba da magana.

"Ni Sarki Ubaiyd ɗana yaga iri a gidanka yana so, ina fatan zan samu ?, domin aurar da 'ya a babban gida irin wannan wane zai ƙi?".

"Ni zanƙi...!".

Baban Aynu ya bashi amsa bai jira mai zaice ba ya cigaba da faɗin.

"Iri na anriga anshuka harya fidda  kai nan da ranar juma'a mai zuwa za'ayi girbinsa zuwa gidan daya dace da ita damu iyayenta".

A fusace Mai Martaba ya dubeshi.

"Har ni kamata na nemi alfarma a wajeka ka iya buɗe baki kace a'a...! Da matsayina da mulki na waye kai?, mai kataka?".

"Ni talaka ne kuma miskini,  ban taki komai ba sai alkhairi, kayi hakuri amma bazanyi magana biyu inzamo karamin mutum ba ƴata dai aurenta za'ayi ina roƙawa ɗanka samun wacce ta tawa

a wajen Allah  na barka lafiya".

Baban Aynu ya miƙe ya fita daga ɗakin cike da ɓacin rai da takaici, shi kuwa Mai Martaba kasa ko motsi yayi sabida ƙuncin da yake ji a cikin ransa, yau rana ta farko a rayuwarsa ya but buƙaci abu bai samu ba, abin da ko da kuɗi zai siya dukiyarsa bazata taba girgiza ba, amma yau talaka ya shigo gidansa har falonsa ya iya kallon tsabar idonsa ya gaya masa magana.

"Mene ya jawo hakan?".

"Fudhal Kaine sila...!".

Yayi maganar a fili tare da miƙewa tsaye ya na faman safa da marwa a cikin falon.

*YARIMA FUDHAL*

Na
FIRDAUSI S.A (QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

SADAUKARWA:-Namesy Phirdausy Jeebour.

Faram-faram Baban Aynu ya shigo gida fuskarsa babu yabo babu fallasa, amma duk wanda ya sanshi ya kuma san yanayinsa yana ganinsa  zai san yana tare da bacin rai.

Umma da Aynu suna zaune inda yabarsu cike da fargaba sai ganinsa sukayi ya faɗo cikin gidan da sauri suka miƙe Umma na tambayar.

"Lafiya Baban Aynu?".

Neman guri yayi ya zauna suma suka zauna tun da yayi tagumi ya shafe tsayin lokuta kafin ya iya motsa harshensa ya bawa Umma amsar tambayar da tayi masa.

"Akan ƴata har akeson nunamin iko da kudi da mulki, na godewa Allah da yasa bikin kwanaki ƙalilan ya rage da bansan abin da zasu zomin da shi ba".

Nan dai ya kwashe dukkan abin da ya faru  tsakaninsa da Sarki ya sanarmusu, Umma shiru tayi ba tare da ta iya furta komai ba, Aynu kuwa fashewa tayi da kuka tamiƙe da gudu ta shige ɗaki.

***

"Assalamu alaikum barkanku da yamma".

Anwar ya faɗa a dai-dai lokacin da yayi parking motarsa gefan wani shagon da wasu samari uku suke zaune  kan benci.

"Yauwa barka dai".

Samarin suka amsa cikin haɗa baki.

Anwar ya sake dubansu tare da jefa musu tambaya.

"Dan Allah tambaya nake, gidansu wani ana ce masa Ya Sayyadi Umar a nan layin aka cemin

gidansu yake".

Ɗaya daga cikin samarin dake zaune bakin shagon yaɗan jinjina kai yana mai-maita.

"Ya Sayyadi Umar..! Ko wanda aka bashi wata yarinya Aynu bikin saura sati guda ko?".

"E shi nake nufi".

Anwar ya basu amsa.

"To ai gida a can ƙasan layin nan yake zaka ganshi flat mai bluen ƙofa".

"OK nagode sosai sai anjima".

Anwar yaja motarsa ya wuce su zuwa inda sukayi masa kwatancen.

Yana parking motar kofar gidan ya fito tare da jingina jikin motar yana waigen neman yaron da zai aika.

Can sai ga wani yaro da bai wuce shekaru bakwai ba ya taho yana gara taya da niyar shiga gidan, Anwar ya tsai da shi yana faɗin.

"Zonan dan Allah".

Yaron babu musu ya tako zuwa inda Anwar yake tsaye yana faɗin.

"Gani".

Anwar ya dafa kafaɗar yaron kafin yace.

"Dan Allah idan ka shiga kace ana sallama da Ya Sayyadi Umar".

Yaron ya amsa da "To".

Ya juya ya shige cikin gidan.

Ya shafe tsayin mintuna goma kafin yaron ya fito ya bashi amsar.

"Wai yace yana zuwa".

Anwar yace.

"To nagode zoka karɓa".

Ya laluba aljihunsa babu chanji sai ɗari biyu ita ya miƙawa yaron fuskarsa cike da murmushina yana faɗin.

"Ga wannan kasayi sweet ko".

"Nagode sosai".

Yaron ya faɗa yana mai cigaba da gara tayarsa ya fice daga layin.

Kafin fitowar Ya Sayyadi sai da Anwar ya kuma bata tsayin mintuna goma, can sai gashi ya leƙo yana dube-duben ganin waye ke sallama da shi domin ko kaɗan bai kawo Anwar bane a ransa, dan zai iya cewa ya mance da fuskarsa, sai dai yana tunanin kamar ya taɓa ganinsa.

Ganin haka ne ya sanya Anwar ƙarasawa wajensa da sauri cikin sallama, Ya Sayyadi ya amsa tare da mika masa hannu sukayi musabiha.

Anwar ya buɗe baki a hankali ya fara magana.

"Ni sunana Anwar nasan baka shaida ni ba, amma ni nakasance abokine kuma amini ga Yarima Fudhal".

Ya Sayyadi ya faɗa ɗa murmushinsa tare da sake bashi hannu suka gaisa yace.

"To mu shiga daga ciki mana?".

Anwar babu musu yabi bayansa har zuwa cikin ɗakinsa dake soro(zaure), ya bashi guri ya

zauna tare da kawo masa ruwa mai sanyi yasha.

"Ya Fudhal ɗin yana lafiya ƙalau ko?".

"E to lafiya ba lafiya ba, domin yanzuma sanadin halin da yake ciki ne ya kawo ni wajenka".

Ya Sayyadi ya gyara zama yana faɗin.

"To Allah yasa muji alkhairi ina sauraronka".

"E to gaskiya bazan iya furta komai ba a halin yanzu alfarma ɗaya zannema a wajenka dan Allah dan Annabi inaso ka bini yanzu zuwa asibiti".

"Amma mai zamuyi a asibiti kuma?".

"Babu komai kawai ina sone kaje kaga halin da dan uwanka musulmi yake ciki wato Fudhal".

"Ban fahimci maganarka ba, wai meke faruwa ne?".

"Koma mene ka kwantar da hankalinka insha Allah idan mukaje zaka fahimta".

Ya Sayyadi Umar yayi shiru na wani lokaci yana kallon Anwar kafin yace.

"Shikenan tashi muje".

Anwar ya miƙe suka fito Ya Sayyadi ya rufo ƙofar ɗakinnasa, ya shiga cikin gidan sukayi sallama da mutanan gidan ya fito zuwa waje, Anwar ya kunna motar suka shiga yaja suka fice daga layin.

Bai yi parking motar a ko ina ba sai cikin harabar asibin a parking space ya kashe motar suka fito, Ya Sayyadi kawai bin Anwar yake a baya tare da 'yan kalle-kallensa har suka isa wani ɗaki Anwar yasa hannu ya murda murfin ƙofar tare da turawa suka sanya kai zuwa cikin ɗakin.

Durƙusawa sukayi suna gaishe dasu Hajiya da Aunty Sadiya dake zaune cikin ɗakin suka amsa fuskarsu babu yabo babu fallasa tare da bin Ya Sayyadi da kallo domin basu San waye ba sun ɗauka ko abokin Anwar ɗinne.

A tare suka miƙe suka ƙarasa bakin gadon da Yarima Fudhal yake kwance domin yanzu anfito da shi mai makon da, da ake ganinsa ta window.

Ya Sayyadi ya jima yana jero masa addu'o'in samun lafiya kamar yanda Manzo Annabi Muhammad (S.A.W) ya koyar damu cewa.

(Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya kasance idan ya ziyarci mara lafiya sai yace masa;

لاَ بَأْسَ طَهُورٌ إِنْ شَاءَ اللهُ .

La ba'asa tahoorun in sha'al-lah.

Ba komai, tsarkaka ce in Allah ya yarda.

أَسْأَلُ اللهَ الْعَظِيمُ، رَبَّ الْعَرْشِ الْعَظِيمِ أَنْ يَشْفِيكَ .(سبع مرات)

Asalul-lahal-'azeem rabbal-'arshil-'azeem an yashfeek (7).
Ina rokon Allah mai girma, Ubangijin Al'arshi mai girma, ya warkar da kai. (sau bakwa).

Manzon Allah, tsira da aminci su tabbata a gare shi, ya ce; "Babu wani bawa Musulmi da zai ziyarci mara lafiya wanda ajalinsa bai riga ya zo ba, sannan ya faɗi wannan (addu'a) sau bakwai face ya sami lafiya)".

(Allahu akbar ya Allah kasa mu dace kasa mukasance masu koyi da koyarwar Annabi ka kara mana sonsa da ƙaunarsa Amin).

Ya sayyadi yayi musu sallama ya fito daga ɗakin Anwar ya biyo bayansa.

A zaune ya taddashi kan wani benci a wajen asibitin shima Anwar ya nemi gurin ya zauna.

"Amma har tsawon wanne lokaci ya ɗauka bashi da lafiya ne?".

Anwar yaɗan dubeshi kaɗan kafin ya bashi amsa.

"Kwana huɗu kenan".

"Kwana huɗu?, amma kamar yayi shekara akwance, me yake damunsa ne?".

Ya Sayyadi ya sake jefawa Anwar tambaya.

"Ciwon SO ne"?.

"So kuma?".

"E mana kana mamaki ne?".

"A a kawai dai nake ganin kamar akwai ciwon da yaja masa hakan bayan Soyayyar".

"E yana fama da ciwon zuciya gaskiya Wanda ya takama matakin ƙarshe na rayuwa ko mutuwa".

"Subhanallahi to a bashi abin da yake so mana".

Anwar yayi murmushi kaɗan kafin yace.

"Wannan kuma aikin kane, Kaine kake da haƙƙin yin hakan domin abin da ya mutu akan sonsa yana wajenka".

"Kana nufin Aynu yake so?".

"E nasan kasan da hakan ai".

Ya Sayyadi shiru yayi yana kallon Anwar ba tare da ya kuma cewa komai ba, can ya nisa yace.

"Zaka iya mai da ni gida, ko in tafi".

"A a mai zai hana?, ni na ɗauko ka ai, tashi muje in mai da kai".

Ya Sayyadi ya miƙe suka taka har  zuwa Inda sukai parking motar suka buɗe suka shiga Anwar yaja suka fita daga cikin harabar asibitin.

Suna tafiya akan titi shiru babu mai cewa da wani komai, Anwar ne yaɗan dubi Ya Sayyadi ta gefan ido kafin ya buɗe baki ya fara faɗin.

"Zan roƙi alfarma a gareka nazo na ɗauke kane badon komai ba illa kaga abin da zan faɗa maka da idanunka domin ganin ya kori ji inji bahaushe, yanzu wuƙa da nama suna hannunka nasan cewa Allah ke rayawa kuma shi yake matarwa idan lokacin mutuwar mutum yayi babu Wanda ya isa ya ƙara masa ko second ɗaya, kamar yanda Idan lokacin mutuwar mutum bai yiba babu Wanda ya isa ya kashe shi, amma kasan cewa komai yana da dalilinsa da kuma sila Fudhal baki ɗaya ya ta'allaka rayuwarsa akan Aynu ne rasa Aynu a cikin rayuwarsa kamar Fudhal ya rasa rayuwarsa ne, wallahi Allah shine shaida da kuma ni Fudhal nason Aynu fiye da rayuwarsa a iya sanina da ganina ban tana ganin mutumin dake son abin da yake so kamar Yarima Fudhal   ba...!".

Ya katse maganar dai-dai sanda yayi parking kofar gidannasu, Anwar ya sake duban Ya Sayyadin yana mai cigaba da faɗin.

"Ka taimaki Fudhal dan Allah ka ceto rayuwarsa nasan ka fahimci abin da nake nufi".

"Zanyi tunanin akan hakan, nagode sosai ka gaida gida Allah ya ƙara masa lafiya".

Abin da yace kenan ya fice daga motar, Anwar ya amsa da
"Amin" yana mai bin bayansa da kallo, aransa yana addu'ar Allah yasa abin da yake ƙoƙarin yi ya tabbata yasa kuma ya fahimci abin da yake so ya fahimta.

*YARIMA FUDHAL*

Na
FIRDAUSI S.A (QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

SADAUKARWA:- Namesy Phirdausy Jeebour.

39

***

Al'amarin ciwon Yarima Fudhal da Yarima Jaleel sai dai addu'a ba zaka iya cire guda ba a cikinsu wanda yafi sauƙi.

Yarima Jaleel tsayin sati biyu kenan ya zama kamar wani zautacce sai dai a yi masa allurar bacci data sake shi kuwa inya farka ya dinga sambatu da buge-buge kenan har sai Doctor ya zo ya sake yi masa wata allurar.

Fulani Sokoto ita ce a wajen Yarima Jaleel sai sauran 'yan aikinta da masu zuwa dubiya.

Fulani Bingel kuwa dukkan yaran gidan sun tare a wajen jinyar Yarima Fudhal duk da cewa suna zuwa dubo Jaleel lokaci zuwa lokaci.

Sarki Ubaiyd baki ɗaya abin duniya ya ishe shi yara biyu, duk suna kwance rai a hannun Allah ! kuma duka waɗanda yake ganin sune magada a bayansa kullum ba shi da aiki Wanda ya wuce tuanani da neman mafita.

Shi kanshi yasan mafita ɗaya ce akan ciwon Fudhal yaje ya nemawa Fudhal auren Aynu amma kash hausawa nacewa (Girman kai rawanin tsiya).
Tsananin girman kai da isa, ba zasu barshi yaje ga wadanda yake ganin su maƙas-ƙantane a gareshi ba.

"Wai Hajiya Mai Martaba ba shi da wani na gaba da shi ne?".

Anwar dake zaune gaban Fulani Bingel yake tambayarta.

"Akwai mana !, Amma me yasa kake tambaya?".

"E to gani nayi gaskiya ya kamata a san abinyi tun da wuri, yanzu haka zamu zuba ido akan ciwon Magaji ne?".

Fulani Bingel tayi shiru tsayin lokaci kafin ta buƊe baki ta bashi amsar tambayarsa.

"Kayi gaskiya Anwar amma sai dai banajin Magaji Saif zai yarda yazo nan garin har yayiwa ƙaninsa sarki Ubaiyd wata magana mai daɗi".

"Waye Magaji Saif kuma?".

Suka haɗa baki dukansu wajen tambayar Mahaifiyartasu domin tun farkon tambayar da Anwar yayi mata suka mai da hankali kacokan a kan Fulani Bingel.

"Magaji Saif yaya ne ga Mahaifinku Uwa ɗaya Uba ɗaya, sai dai abin da ya shiga tsakaninsu tsayin shekaru shine yayi sanadiyyar raba zumuncin dake tsakanin Mahaifannaku.

"Mene ya shiga tsakaninsu Hajiya?".

Wannan karon Aunty Sadiya ce tayi tambayar.

Ajiyar zuciya Fulani tayi kaɗan kafin ta fara magana.

*MUSAB-BABIN GABARSU*

"Abin da ya haddasa gaba tsakanin Mahaifannaku akan abu biyu ne na farko nice na biyu kuma al'amarin sarauta ne".

"Ni 'yar asalin garin Bingel ce haifaffiyar can wata rana Mahaifinku da Yayansa sun ziyarci garin namu tare da iyayensu domin halartar ɗaurin auren ɗan sarkin garin wato Yayana, a wannan lokaci ne a cikin hidimar bikin muka fara haɗuwa da Mahaifinku ya baiyanamin abin da ke ƙarƙashin zuciyarsa da sunan yana sona, duk da ban amince ba car lokacin sabida kunya amma washe garin ranar na baiyanawa ƙawata kuma ta sameshi ta bashi amarsa".

"A ranar ne kuma Yayansa shima yazo min da irin batun da Mahaifinku yazo min da shi, sai dai

ban amince ba anan take na baiyana masa cewa ni Ubaiyd nake so, tun a wannan lokaci faɗa ya fara shiga tsakaninsu saɓanin da ayanda suke Mahaifannaku suna son junansu tare da girmama tsakaninsu haka kuma Mahaifinku yanajin maganar Yayansa".

"Yazo masa da batun cewa sai dai ya haƙura ya bar masa ni ai shine gaba da shi, shi kuma yace bazai yiyu ba hakan ne ya haddasa faɗa atsakaninsu har suka koma gida babu mai yiwa wani magana domin Magaji Saif yafi Sarki Ubaiyd tsananin fushi da zuciya".

"Ana cikin wannan hatsaniyarne kuma Kakanku ya kwanta ciwon ajali cikin kwanaki biyu yace ga garinku nan, lokacin munzo gaisuwa a ranar majalisa ta zauna domin tan-tance wanda zai zamo Magaji a tsakaninsu , Magaji Saif yayi magana kan cewa".

"Indai shine za'a bawa sarauta to dole ne Sarki Ubaiyd ya haƙura da aure na ya barmasa ko kuma ya fita yabar garin, shi kuma Mahaifinku yace bazai yarda ba ananma sai da sukayi faɗa haka aka tashi ba tare da samun mafita ba".

"Sai dai kuma abin da kowa bai sani ba a daren 'yan majalisa sun sake zama domin kwance wannan ƙullin dake tsakanin iyayenku sunyi shawara kancewa Mahaifinku za'a bawa sarauta tare da aurena inyaso Magaji Saif a bashi waziri domin gudun matsala sabida sun San muddun suka bawa Magaji Saif sarauta duk yanda zasu so bazasu iya hanashi muzanta Sarki Ubaiyd ba, domin irin kalaman da yayi sun San zai aikata fin haka dan baya magana ya sake ta, shi kaifi ɗaya ne koda kuwa zai rasa ransa".

"A washe garin ranar aka haɗa aurena da Mahaifinku tare da naɗin sarauta da kuma sadakar ukun Kakan ku, nan take Magaji Saif yace baya son wazircin kuma daga ranar Shiba haifaf-fan garin nan ba ne, kada Wanda yace ma ya taɓa saninsa a duniya daga nan ya fice yabar garin bamu sake jin labarin saba sai lokacin da aka fara maganar batun auren Magaji da Gimbiya Safiyya mukaji cewar yana zaune a Sokoto".

Shiru ɗakin ya dauka tsayin daƙiƙu masu yawa kafin Anwar ya nisa yana mai faɗin.

"Insha Allahu zamu sami nasara, zanje innemeshi zai dawo gida cikin farin ciki kuma zasu manta gabar da suke da yardar Allah".

"Allah yasa ya ɗora ka akansa, domin shi kaɗai ne nake ganin a duniya Wanda zai iya sanya Sarki Ubaiyd yayi, kuma shine kaɗai zai iya hanashi ya hanu, sai dai kuma meye fa'idar sako

shi a zancen?".

Anwar yaɗanyi murmushi.

"Hajiya kenan kin mance yau saura 2days ayi bikin Aynu kuma duk yanda naso Mai Martaba yaje ya roƙesu yaƙi, duk wata hanya da zanbi insawa Fudhal farin ciki nabi amma babu nasara sai dai inaji a raina wannan ce kaɗai nasararmu in Allah yaso".

Fulani Bingel ta murmusa tare da faɗin.

"Allah yayi maka albarka Anwar ya baka abin da kake so duniya da lahira lallai ka cika aboki kuma amini na gari Ubangiji ne kaɗai zai iya yi maka sakaiya akan abin alkhairin da kake aikatawa domin mu kuwa bamu da abin da zamu saka maka".

"Hajiya kibar faɗin haka ai Fudhal a guna dan uwane na jini zan iyayin abin da yafi hakama akansa kedai kawai ki tayani da addu'a".

"Insha Allahu kada ka damu da wannan".

Anwar ya sanya kai ya fita daga ɗakin yayin da suka biyoshi dukkanninsu da addu'ar fatan alkhairi.

****

Tun ranar da Ya Sayyadi Umar yaje ya dubo Yarima Fudhal ya dawo baki daya ya gaza samun nutsuwa da kwanciyar hankali a tattare da shi, ji yake kamar yana shirin aikata bab-ban kuskure ne tare dayin aikin dana sani, sai dai ƙasan zuciyarta na tausarsa da cewa shimafa yana sonta taya zai iya haƙura ya bawa wani?.

Hakan yasa yake samun ƙwarin gwiwa tare daji aransa bazai taɓa iyayin SADAKAR SOYAYYA ba.

Shi kaɗaine a motarsa yake driven yayin da ya sanya kira'ar sudais a motar yana tuƙi yana bi

hankalinsa kwance kai kace babu abin da yake damunsa a duniya, sai dai ƙasan zuciyarta cunkuce take da tarin damuwa da tunanin abin da zaije ya tarad duk da cewa yana yiwa kansa fatan alkhairi tare da saran samun nasara domin yasan aikin alkhairi yake shirin aikatawa bare kuma al'amari na zumunci Allah zai bashi nasara.

Ko da ya isa cikin Sokoto birnin shehu ya shafe tsayin a wanni hudu yana fafutuwar neman Magaji Saif kafin Allah ya haɗashi da wani al'amajiri mai wanki da guga shine yace ya sanshi ai shi yake bawa wanki da guga duk sati, gidansa a can (kalan baina) yake yazo suje ya rakashi.

Haka suka tafi yaron na nunawa Anwar hanya shi kuma yana bi har zuwa bakin gate ɗin wani tamfatse-tsen gida sukayi hon gateman ya buɗe ƙofar wangagememan gate din gidan suka sanya kai.

Almajirin yace wa Mai gadi ya sanarwa Alhaji yayi baƙo, ba musu Mai gadin ya wuce cikin gidan da sauri domin sanarwa ahaji dake yasan almajirin sosai, mintuna kaɗan sai gashi ya dawo tare da amsar su shiga yana jiransu.

Su Anwar suka sanya kai zuwa cikin gidan, shi dai Anwar kallon gidan kawai yake domin yasan ko a turai da yayi karatu bai taɓa ganin gida mai girma da haɗuwa kamar wannan gidan ba, faɗin haduwar gidanma ƙauyanci ne sai dai masu karatu ku ƙiyassata a cikin ranku.

Yana zaune falo kan wata luntsumemiyar kujera 'yar ubansu shaddar dake sanye jikinsa ita kanta kukan kuɗi take bare kuma azo batun takalmi da hula zuwa uwa uba agogon hannunsa, yana zaune a hannunsa kuma news paper ce yake karanta sukayi sallama ya ɗago kai cike da fara'a yana mai amsa musu.

Tsan-tsan kamar Sarki Ubaiyd da Anwar yagani a tare da fuskar Magaji Saif shine abin da ya daure masa kai ainun ya kuma tabbatar tabbas wannan shine Magaji Saif yayan Sarki Ubaiyd.

Suka gaisa Anwar yayiwa almajirin godiya tare da alkhairi mai yawa ya tashi ya tafi.

Yana fita Magaji Saif yabi Anwar da kallo yana faɗin.

"Sai dai ban shaida fuskarka ba, ko zaka iya yimin bayanin waye kai?, mene kuma ya kawoka gidan nan?".

Anwar yayi murmushi kafin yace.

"Abu mai sauƙi dama hakance ta kawo ni".

Nan take Anwar ya fara bashi amsar tambayarsa dalla-dalla tare da faɗin abin da ya kawoshi da kuma dalilin zuwansa.

Magaji Saif ya haɗe girar sama data ƙasa tamkar bashi ne yake murmushi ba yanzu sai kace an aiko masa da saƙon mutuwarsa haka ya miƙe tsaye yana mai mid zuwa wajen Anwar tuni hantar cikin Anwar tahau kaɗawa tsoro ya ziyarceshi take ya fara karanto addu'a cikin ransa domin ya gama hasko irin cin mutunci da tozarcin da zai fuskanta yau a hannun Magaji Saif.

KOMA DAI MENENE KU BIYO NI........! Smile kuna raina fa.

Nagode sosai da sosai da ɗunbin tarin addu'arku a agare ni Allah ya biyaku amin.

*YARIMA FUDHAL*

Na
FIRDAUSI S.A (QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

SADAUKARWA:- Namesy Phirdausy Jeebour.

39

***

Al'amarin ciwon Yarima Fudhal da Yarima Jaleel sai dai addu'a ba zaka iya cire guda ba a cikinsu wanda yafi sauƙi.

Yarima Jaleel tsayin sati biyu kenan ya zama kamar wani zautacce sai dai a yi masa allurar bacci data sake shi kuwa inya farka ya dinga sambatu da buge-buge kenan har sai Doctor ya zo ya sake yi masa wata allurar.

Fulani Sokoto ita ce a wajen Yarima Jaleel sai sauran 'yan aikinta da masu zuwa dubiya.

Fulani Bingel kuwa dukkan yaran gidan sun tare a wajen jinyar Yarima Fudhal duk da cewa suna zuwa dubo Jaleel lokaci zuwa lokaci.

Sarki Ubaiyd baki ɗaya abin duniya ya ishe shi yara biyu, duk suna kwance rai a hannun Allah ! kuma duka waɗanda yake ganin sune magada a bayansa kullum ba shi da aiki Wanda ya wuce tuanani da neman mafita.

Shi kanshi yasan mafita ɗaya ce akan ciwon Fudhal yaje ya nemawa Fudhal auren Aynu amma kash hausawa nacewa (Girman kai rawanin tsiya).
Tsananin girman kai da isa, ba zasu barshi yaje ga wadanda yake ganin su maƙas-ƙantane a gareshi ba.

"Wai Hajiya Mai Martaba ba shi da wani na gaba da shi ne?".

Anwar dake zaune gaban Fulani Bingel yake tambayarta.

"Akwai mana !, Amma me yasa kake tambaya?".

"E to gani nayi gaskiya ya kamata a san abinyi tun da wuri, yanzu haka zamu zuba ido akan ciwon Magaji ne?".

Fulani Bingel tayi shiru tsayin lokaci kafin ta buƊe baki ta bashi amsar tambayarsa.

"Kayi gaskiya Anwar amma sai dai banajin Magaji Saif zai yarda yazo nan garin har yayiwa ƙaninsa sarki Ubaiyd wata magana mai daɗi".

"Waye Magaji Saif kuma?".

Suka haɗa baki dukansu wajen tambayar Mahaifiyartasu domin tun farkon tambayar da Anwar yayi mata suka mai da hankali kacokan a kan Fulani Bingel.

"Magaji Saif yaya ne ga Mahaifinku Uwa ɗaya Uba ɗaya, sai dai abin da ya shiga tsakaninsu tsayin shekaru shine yayi sanadiyyar raba zumuncin dake tsakanin Mahaifannaku.

"Mene ya shiga tsakaninsu Hajiya?".

Wannan karon Aunty Sadiya ce tayi tambayar.

Ajiyar zuciya Fulani tayi kaɗan kafin ta fara magana.

*MUSAB-BABIN GABARSU*

"Abin da ya haddasa gaba tsakanin Mahaifannaku akan abu biyu ne na farko nice na biyu kuma al'amarin sarauta ne".

"Ni 'yar asalin garin Bingel ce haifaffiyar can wata rana Mahaifinku da Yayansa sun ziyarci garin namu tare da iyayensu domin halartar ɗaurin auren ɗan sarkin garin wato Yayana, a wannan lokaci ne a cikin hidimar bikin muka fara haɗuwa da Mahaifinku ya baiyanamin abin da ke ƙarƙashin zuciyarsa da sunan yana sona, duk da ban amince ba car lokacin sabida kunya amma washe garin ranar na baiyanawa ƙawata kuma ta sameshi ta bashi amarsa".

"A ranar ne kuma Yayansa shima yazo min da irin batun da Mahaifinku yazo min da shi, sai dai ban amince ba anan take na baiyana masa cewa ni Ubaiyd nake so, tun a wannan lokaci faɗa ya fara shiga tsakaninsu saɓanin da ayanda suke Mahaifannaku suna son junansu tare da girmama tsakaninsu haka kuma Mahaifinku yanajin maganar Yayansa".

"Yazo masa da batun cewa sai dai ya haƙura ya bar masa ni ai shine gaba da shi, shi kuma yace bazai yiyu ba hakan ne ya haddasa faɗa atsakaninsu har suka koma gida babu mai yiwa wani magana domin Magaji Saif yafi Sarki Ubaiyd tsananin fushi da zuciya".

"Ana cikin wannan hatsaniyarne kuma Kakanku ya kwanta ciwon ajali cikin kwanaki biyu yace ga garinku nan, lokacin munzo gaisuwa a ranar majalisa ta zauna domin tan-tance wanda zai zamo Magaji a tsakaninsu , Magaji Saif yayi magana kan cewa".

"Indai shine za'a bawa sarauta to dole ne Sarki Ubaiyd ya haƙura da aure na ya barmasa ko kuma ya fita yabar garin, shi kuma Mahaifinku yace bazai yarda ba ananma sai da sukayi faɗa haka aka tashi ba tare da samun mafita ba".

"Sai dai kuma abin da kowa bai sani ba a daren 'yan majalisa sun sake zama domin kwance wannan ƙullin dake tsakanin iyayenku sunyi shawara kancewa Mahaifinku za'a bawa sarauta tare da aurena inyaso Magaji Saif a bashi waziri domin gudun matsala sabida sun San muddun suka bawa Magaji Saif sarauta duk yanda zasu so bazasu iya hanashi muzanta Sarki Ubaiyd ba, domin irin kalaman da yayi sun San zai aikata fin haka dan baya magana ya sake ta, shi kaifi ɗaya ne koda kuwa zai rasa ransa".

"A washe garin ranar aka haɗa aurena da Mahaifinku tare da naɗin sarauta da kuma sadakar ukun Kakan ku, nan take Magaji Saif yace baya son wazircin kuma daga ranar Shiba haifaf-fan garin nan ba ne, kada Wanda yace ma ya taɓa saninsa a duniya daga nan ya fice yabar garin bamu sake jin labarin saba sai lokacin da aka fara maganar batun auren Magaji da Gimbiya Safiyya mukaji cewar yana zaune a Sokoto".

Shiru ɗakin ya dauka tsayin daƙiƙu masu yawa kafin Anwar ya nisa yana mai faɗin.

"Insha Allahu zamu sami nasara, zanje innemeshi zai dawo gida cikin farin ciki kuma zasu manta gabar da suke da yardar Allah".

"Allah yasa ya ɗora ka akansa, domin shi kaɗai ne nake ganin a duniya Wanda zai iya sanya Sarki Ubaiyd yayi, kuma shine kaɗai zai iya hanashi ya hanu, sai dai kuma meye fa'idar sako shi a zancen?".

Anwar yaɗanyi murmushi.

"Hajiya kenan kin mance yau saura 2days ayi bikin Aynu kuma duk yanda naso Mai Martaba yaje ya roƙesu yaƙi, duk wata hanya da zanbi insawa Fudhal farin ciki nabi amma babu nasara sai dai inaji a raina wannan ce kaɗai nasararmu in Allah yaso".

Fulani Bingel ta murmusa tare da faɗin.

"Allah yayi maka albarka Anwar ya baka abin da kake so duniya da lahira lallai ka cika aboki kuma amini na gari Ubangiji ne kaɗai zai iya yi maka sakaiya akan abin alkhairin da kake aikatawa domin mu kuwa bamu da abin da zamu saka maka".

"Hajiya kibar faɗin haka ai Fudhal a guna dan uwane na jini zan iyayin abin da yafi hakama akansa kedai kawai ki tayani da addu'a".

"Insha Allahu kada ka damu da wannan".

Anwar ya sanya kai ya fita daga ɗakin yayin da suka biyoshi dukkanninsu da addu'ar fatan alkhairi.

****

Tun ranar da Ya Sayyadi Umar yaje ya dubo Yarima Fudhal ya dawo baki daya ya gaza samun nutsuwa da kwanciyar hankali a tattare da shi, ji yake kamar yana shirin aikata bab-ban kuskure ne tare dayin aikin dana sani, sai dai ƙasan zuciyarta na tausarsa da cewa shimafa yana sonta taya zai iya haƙura ya bawa wani?.

Hakan yasa yake samun ƙwarin gwiwa tare daji aransa bazai taɓa iyayin SADAKAR SOYAYYA ba.

Shi kaɗaine a motarsa yake driven yayin da ya sanya kira'ar sudais a motar yana tuƙi yana bi hankalinsa kwance kai kace babu abin da yake damunsa a duniya, sai dai ƙasan zuciyarta cunkuce take da tarin damuwa da tunanin abin da zaije ya tarad duk da cewa yana yiwa kansa fatan alkhairi tare da saran samun nasara domin yasan aikin alkhairi yake shirin aikatawa bare kuma al'amari na zumunci Allah zai bashi nasara.

Ko da ya isa cikin Sokoto birnin shehu ya shafe tsayin a wanni hudu yana fafutuwar neman Magaji Saif kafin Allah ya haɗashi da wani al'amajiri mai wanki da guga shine yace ya sanshi ai shi yake bawa wanki da guga duk sati, gidansa a can (kalan baina) yake yazo suje ya rakashi.

Haka suka tafi yaron na nunawa Anwar hanya shi kuma yana bi har zuwa bakin gate ɗin wani tamfatse-tsen gida sukayi hon gateman ya buɗe ƙofar wangagememan gate din gidan suka sanya kai.

Almajirin yace wa Mai gadi ya sanarwa Alhaji yayi baƙo, ba musu Mai gadin ya wuce cikin gidan da sauri domin sanarwa ahaji dake  yasan almajirin sosai, mintuna kaɗan sai gashi ya dawo tare da amsar su shiga yana jiransu.

Su Anwar suka sanya kai zuwa cikin gidan, shi dai Anwar kallon gidan kawai yake domin yasan ko a turai da yayi karatu bai taɓa ganin gida mai girma da haɗuwa kamar wannan gidan ba, faɗin haduwar gidanma ƙauyanci ne sai dai masu karatu ku ƙiyassata a cikin ranku.

Yana zaune falo kan wata luntsumemiyar  kujera 'yar ubansu shaddar dake sanye jikinsa ita kanta kukan kuɗi take bare kuma azo batun takalmi da hula zuwa uwa uba agogon hannunsa, yana zaune a hannunsa kuma news paper ce yake karanta sukayi sallama ya ɗago kai cike da fara'a yana mai amsa musu.

Tsan-tsan kamar Sarki Ubaiyd da Anwar yagani a tare da fuskar Magaji Saif shine abin da ya daure masa kai ainun ya kuma tabbatar tabbas wannan shine Magaji Saif yayan Sarki Ubaiyd.

Suka gaisa Anwar yayiwa almajirin godiya tare da alkhairi mai yawa ya tashi ya tafi.

Yana fita Magaji Saif yabi Anwar da kallo yana faɗin.

"Sai dai ban shaida fuskarka ba, ko zaka iya yimin bayanin waye kai?, mene kuma ya kawoka gidan nan?".

Anwar yayi murmushi kafin yace.

"Abu mai sauƙi dama hakance ta kawo ni".

Nan take Anwar ya fara bashi amsar tambayarsa dalla-dalla tare da faɗin abin da ya kawoshi da kuma dalilin zuwansa.

Magaji Saif ya haɗe girar sama data ƙasa tamkar bashi ne yake murmushi ba yanzu sai kace an aiko masa da saƙon mutuwarsa haka ya miƙe tsaye yana mai mid zuwa wajen Anwar tuni hantar cikin Anwar tahau kaɗawa tsoro ya ziyarceshi take ya fara karanto addu'a cikin ransa domin ya gama hasko irin cin mutunci da tozarcin da zai fuskanta yau a hannun Magaji Saif.

KOMA DAI MENENE KU BIYO NI........! Smile kuna raina fa.

Nagode sosai da sosai da ɗunbin tarin addu'arku a agare ni Allah ya biyaku amin.

*YARIMA FUDHAL*

Na
FIRDAUSI S.A (QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITWRS ASSOCIATION®

SADAUKARWA:-NAMESY PHURDAUSY JEEBOUR.

40

Ganin yanda Magaji Saif yake nufoshi, shine yayi sanadiyyar miƙewarsa tsaye a kasalance suna duban juna ido da ido amma duk da hakan Anwar baiyi ƙasa a gwiwa wajen cigaba da karonta addu'o'i ba a cikin ransa.

Har sai da Magaji Saif yazo daf da Anwar suka shafe tsayin lokuta suna kallon juna ko wannensu da abin da yake saƙawa cikin a cikin ransa.

Sai dai abin da Anwar yaga Magaji Saif ya aikata ne yayi sanadiyyar tsayawar wayoyen jikinsa da dena aiki take lantarkin dake sarrafasu ta ɗauke,   murza ido ya hauyi domin tabbatarwa

gaske ne ko a mafarki ne?, Magaji Saif ya rungume shi har yana ɗan bubbuga bayansa...!.

Maganar Magaji Saif  ita tayi sanadiyyar dai-daituwar kwakwalwarsa.

"Tabbas munyi kuskure a rayuwa nayi nadama bayan wani lokaci, ka sani yau tsayin shekaru ina zaman jirar ranar da zanga wani ya zo nemana, sai gashi Allah ya amsa roƙona a yau lallai dole inyi farin ciki tare da godewa Allah a yau ɗinnan".

Anwar dai sosoko yayi yana sauraransa, Magaji Saif ya janye jikinsa daga na Anwar fuskarsa cike da murmushi haɗe da hawayen farin ciki, ya cigaba da kallon fuskar Anwar.

Anwar yaɗanyi gyaran  murya tare da buɗe baki ya fara magana.

"Amma mai yasa baka je ka nemi ahalinka ba tare da neman gafararsu tasayin wannan lokaci ka zauna sai dai a zo a nemeka, ko kasan cewar Mahaifiyarku ta rasu?".

"Na sani...!"

Jin amsar daya bayar ya sanya Anwar sakar baki yana dubansa, Magaji Saif yayi murmushi tare da kama hannun Anwar ya zaunar da shi kan kujera shima ya koma Inda yake da ya zauna tsayin da ƙiƙu yana ƙarewa Anwar kallo kafin ya ci gaba da magana.

"Ina gudun wulakanci da tozarci ne shine yasa naƙi baiyana kaina a wajen ƙanina amma batun jana'idar Hajiyarmu tare dani akai hatta zaman makoki nayi dukkan wani motsi na gidan babu Wanda ban sani ba, sai dai abubuwa da yawa suna ɗauremin kai akan Ubaiyd".

Yaɗan ja numfashi kaɗan.

"Yaushe ne Ubaiyd yazama azzalumin sarki?, taya akai ya zama mai girman kai da izgili? tarbiyar iyayenmu babu wulakantar da ɗan adam, amma ina mamakin yanda akai Ubaiyd ya koyi wasu irin munanan halaye ya sanyawa kansa alhali nasan a da ba haka yake ba, ko kuma Sarautace ta koyamai hakan?".

Duk wannan tambayoyin da yake jerewa Anwar kawai kallonsa yake yana kuma sauraronsa.

"A sanda nabar gida na tafi ne tare da burin komai daren daɗewa sai na gaji mahaifinmu nayi sarauta, amma akan Ubaiyd naji na tsani sarauta indai haka sarauta take mai da mutum mai munanan halaye bazan taɓa addu'ar Allah ya sake bawa wani jinina ba kai ko barema domin wannan halayen sune matsayin kuɗin siyan wutar jahannama sune za suyi sanadiyyar sayar mana fushin Allah da Manzonsa...! UBAIYD.! UBAIYD..! UBAIYD...! Me yasa haka?, me yasa?".

Ya kai maganar cike da ƙaraji yana huci harda bugun centre table ɗin dake gabansa.

"Kayi hakuri Abba, amma nake ganin babu abin da yake sayawa ɗan Adam munanan halaye sai dai idan dama can halinsa ne dake ɓoye cikin ransa to idan mutum ya samu wata dama ko wani muƙami sai hakan ya dinga bashi ƙarfin gwiwar aikatawa tunda yana tunanin babu Wanda ya isa ya hanashi bare a taka masa burki".

Magaji Saif kai ya gyaɗa yana faɗin.

"Haka ne maganarka kayi gaskiya Anwar, yanzu ya jikin Fudhal?".

"Alhamdulillahi Abba".

"Masha Allah sai ka kwana anan zuwa gobe da safe idan Allah ya kaimu zan nemi hutu a in da nake aiki sai mu tafi can ɗin".

"OK Allah ya kaimu".

Anwar ya faɗa yana mai ƙarewa falon kallo duk hotunan Magaji Saif ne cike a falon ya baza ido iya bazawa baiga hoton ɗa ba bare na wata mace.

"Abba nace Yaran gidan sunyi tafiya ne?".

Anwar yayi tambayar dai-dai sanda Magaji Saif ya isa wajen freezer domin kawo wa Anwar ɗan lemo.

Magaji Saif yayi murmushi kawai ya ɗauko juice na kwali da cofi ya kawo gaban Anwar ya a jiye yana maganar.

"Babu kowa a gidan nan babu mace taya za'a samu yara?, daga ni sai kukuna sai mai gadi mukenan a gidan".

"Matarka mutuwa tayi ne Abba?".

Magaji Saif ya girgiza kai yana duban fuskar Anwar har lokacin murmushin dake kan fuskarsa bai ɗauke ba.

"Ban taɓa aure ba Anwar amma a kullum ina son yi, yanzu ga ɗaki can ka shiga kayi wanka ka huta anjima ka fito daining ni zan shiga ciki".

Ya miƙe yahau saman bene yabar Anwar nan zaune yana jujjuya maganar Magaji Saif.

"Ban taɓa aure ba Anwar amma a kullum ina son yi..!".

Ya sake mai-maita maganar.

"To amma mai yahanashi yi?, duk da gashi bai rasa komai ba a duniya, ko da yake aure nufi ne na Allah".

Yayi tambayarsa ya bawa kansa amsa.

Juice ɗin ya buɗe ya zuba a cofin yaɗan sha kaɗan kafin ya miƙe ya nufi ɗakin da Magaji Saif ya nuna masa.

Ɗakin komai akwai ciki hakan ba ƙaramin daɗi da mamaki yayiwa Anwar ba, kayansa ya cire ya faɗa toilet domin yin wanka.

Yana fitowa dama yayo alwala da yake lokacin sallar maghriba yayi ya sanya jallabiya yayi sallah yana idarwa ya jawo wayarsa yahau neman number Hajiyarsu Fudhal.

Kira ɗaya ta aga tare da sallama, Anwar ya amsa yana faɗin.

"Na samu gidansa Hajiya goben nan zamu taho tare da shi".

"Kana nufin kace ka sanar dashi komai amma ya yarda zai biyoka cikin sauƙi haka?".

"Hajiya kenan kin manta da ƙarfin fauwalawa Allah komai da addu'a kuma?".

"Hakane Allah ya kaimu goben lafiya muna zaman jiranku Allah ya kawo ku lafiya".

"Amin Hajiya ya jikin Fudhal fa?".

"Da sauƙi Anwar yau dai ansamu ya iya motsa yatsun hannunsa dana kafa amma bai buɗe ido ba".

"Kai..Amma naji daɗi wallahi idon ma da yardar Allah zai buɗe Allah ya ƙara lafiya".

"Amin ya Allah sai da safe".

Suka kashe wayar a tare yana ajiye wayar akayi knocking ya amsa a shigo.

Wani saurayi ya leƙo yana faɗin.

"Komai ready Yallaɓai na jiranka a daining".

"OK ganinan".

Saurayin na juyawa Anwar ya biyo bayansa.

Daining cike taf da abinci kala-kala haka suka ci suka ƙoshi sunayi suna hira jefi-jefi duka hiran akan Yarima Fudhal ne.

Magaji Saif yayi murmushi yana faɗin.

"Shi kuma sai da yaje ya ɗebo wannan zafin ran na banza ko?".

Anwar shima murmushin yayi ba tare da yace komai ba, suna gamawa Magaji Saif yayiwa Anwar sai da safe ya hau sama, shima Anwar ɗin bai wani zauna ba ya koma aki ya ɗan huta domin ya gaji.

*WASHE GARIN RANAR DA SAFE*

Hayaniyar ce tayi sanadiyyar ta shinsa daga baccin, yana buɗe ido yaga ashe gari ya waye time ɗin 8:20, dafe kai yayi tare da miƙewa daga kan gadon ya zuro ƙafarsa ya sauko ya nufi bakin windown ɗakin dan ganin hayaniyar tame ce take tashi haka?.

Jama'a ya gani cikin harabar gidan damƙam, Magaji Saif na zaune kan kujera gefansa kuma buhu ne na kuɗi sai kayan abinci katan-katan na taliya da makaroni indomie da couscous ga kuma manyan buhunan shinkafa nan ajiye yana ta rabawa mutanan Anwar abin ya ƙara ɗaure masa kai ya shafe tsayin lokuta yana kallo kafin ya shige toilet yayi wanka ya fito ya shirya ya fita daining ya tadda komai is ready yayi breakfast.
ya koma ɗaki ya duba ta window yaga babu kowa kamar anyi shara maganar da yaji ne ta bayansa yasa shi juyawa da sauri murmushi sukayi a tare Anwar ya durƙusa ya gaishe shi ya amsa tare da shafa kansa yana faɗin.

"Harka tashi ka shirya?".

"E nagama komai, Amma Abba zakka kayi ne?".

"A a alƙawari na cika".

"Alƙawari kuma na me fa?".

"Duk ranar da Allah ya kawo wani nawa na alƙawaranta cewa zanyi sadaka ta musamman domin nuna godiya ga Allah".

Anwar yayi murmushi tare da jin daɗin kyawawan halayen Magaji Saif har yana rayawa a cikin ransa dama ace shine ya haifi Yarima Fudhal.

Helloooo...!

Kuyi hkr da wannan sai gobe idan Allah yakaimu da rai da lafiya zaku jini insha Allah.

Byeee

*YARIMA FUDHAL*

Na
FIRDAUSI S.A (QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

SADAUKARWA:-NAMESY PHIRDAUSY JEEBOUR.

41

11:42am

Suka yi parking motarsu a parking space dake cikin harabar asibin.

Kai tsaye Anwar ya yi musu jagowa har zuwa cikin ɗakin da aka kwantar da Yarima Fudhal.

Lokacin Sarki Ubaiyd na zaune kan ɗaya daga cikin fararan kujerun dake ɗakin kansa na ƙasa Wanda hakanne zai tabbatar maka da cewar ya faɗa cikin wani zurfaffan tunani ne.

Gefe guda kuma Fulani Bingel ce tare dasu Aunty Sadiya sai ƴan biyunta dake kwance kan carpet ɗin ɗakin sunata haura-hauransu sunyi ɓulɓul abinsu gwanin ban sha'awa.

Anwar ne ya fara turo ƙofar ya shigo cike da sallama sannan Magaji Saif ya biyo bayansa.

Ba Fulani Bingel ba hatta Sarki Ubaiyd bai San sanda ya mƙe tsaye ba sabida jin muryar mutumin da ko a mafarki bai taɓa tunanin zai sake jin ta ba.

Sai kuma gashi yau har suna ido biyu da juna kallon kallo aka hauyi tsakanin Magaji Saif da Sarki Ubaiyd .

Abin da basu taɓa zata da tunani ba shine ya faru wato hawaye a cikin idanun Sarki Ubaiyd amma kuma sun kasa tan-tance shin na farin ciki ne kona me?.

Sarki Ubaiyd ya taka ƙafafuwansa cike da sassarfa har zuwa inda Magaji Saif yake tsaye baiyi wata-wata ba kawai ya rungume shi yana faɗin.

"Kaine Yaya?, a she zan sake ganinka?, a she da rabon  zamu sake ganawa a duniya?, kayi haƙuri ka gafarce ni nasan nayi kuskure a rayuwata...".

"Aa kabar faɗin haka.!".

Magaji Saif ya katse shi yana mai ci gaba da faɗin.

"Ni ne mai laifi kuma tuni nayi nadama na yafe maka fatana Allah ya yafemu baki ɗayanmu".

Ya kai maganar yana mai ɗan bub-buga bayan Sarki Ubaiyd.

Baki ɗayansu suka amsa da "Amin" kowanne daga cikin su yana matse kwallar data taru gefan idonsa.

Sarki Ubaiyd ya bawa Magaji Saif kujerar da yake zaune shi kuma ya nemi guri a ƙasan carpet ya zauna, Magaji Saif yayi nacin ya koma kan ɗaya daga cikin kujerun ya zauna amma yaƙi.

Nan aka gaggaisa Magaji Saif yana tambayar masu jiki kafin ya dawo da kallonsa kansu Fulani Bingel.

"Kudan bamu waje".

Ba musu dukansu suka fice suka bar Magaji Saif da Sarki Ubaiyd sai Yarima Fudhal Mara lafiya da yake can kan gado kwance.

Suna fita Magaji Saif ya dubi Sarki Ubaiyd ya fara magana cikin tattausan harshe ya kira sunansa.

"Ubaiyd..!".

Sarki Ubaiyd ya amsa.

"Na'am Yaya".

Magaji Saif ya ci gaba da maganarsa.

"Naji komai a bakin Anwar sai dai ka bani mamaki sosai Ubaiyd a ce kamarka kana aikata irin wannan abin da girmanka da komai da tunanika haba Ubaiyd ya kake nema giyar mulki tayi rinjaye akanka har kana neman salwantar da rayuwar jininka har guda biyu".

"Idan ka manta ni zan tuna maka, da talaka da mai kuđi basu da wani banbanci a gurin Allah sai Wanda yafi tsoron Allah ya inganta lahirarsa, bazan tsaya dogon surutu akanka ba domin kuskure ne anriga an aikata sai dai a kiyayi gaba".

"Sannan abin da ya kawo ni idan har na isa da kai kuma haryanzu ina nan a matsayin Yaya a gareka inaso a yau đin nan dani da kai zamuje gidansu yarinyar da Fudhal yake so ayi magana, kuma batun auren mata biyu ka a jiyeshi gefe shi kuma Jaleel shima a bashi wadda yake a zauna lafiya".

"Amma Yaya...!".

"A a Ubaiyd wannan Umarni ne ba shawara ba idan har kaji ka yarda to, idan kuma baka yarda ba zaka nunamin ban isa ba ga hanya nan yanzun nan zan tashi inkoma Inda na fito".

Sarki Ubaiyd yayi shiru tsayin wasu lokuta baice komai ba, haka shima Magaji Saif bai sake furta wata kalma ba ɗakin inbanda karar fanka dake tashi kaɗan-kɗan bakajin komai.

Ganin shirun yayi yawa ya sanya Magaji Saif miƙewa ya nufi bakin ƙofa zai fita ya murɗa hannun kofar zai buɗe Sarki Ubaiyd ya riƙo hannunsa cikin zafin nama yana faɗin.

"Kada ka tafi naji na amince zanyi dukkan abin da kace wallahi, ƴaƴana ai naka  ne kana da ikon zartar da kowanne irin hukuncin a kansu".

Magaji Saif yayi murmushin jin daɗi har ƙasan ransa ya koma ya zauna har a lokacin murmushin bai bar saman fuskarsa ba.

Ya cigaba da faɗin.

"Ka amince zamuje neman auren yarinyar yanzu?".

Sarki Ubaiyd ya gyaɗa kai ba tare da yace komai ba.

"Idan ta kama da ba da hakuri dole haka zaka bayar, duk wani girman kai da taƙamar mulki ka ajiye shi tun anan".

Nanma Sarki Ubaiyd kai ya gyaɗa alamun  ya a mince.

"To alhamdulillahi tashi muje".

Magaji Saif ya faɗa yana mai wucewa gaba domin fita daga ɗakin, Sarki Ubaiyd ya biyo bayansa.

A tare suka fito Inda su Anwar ke zaune zaman jiransu, Magaji Saif yace.

"Ku koma ciki Sadiya, kai kuma Anwar biyomu zuwa  parking space.

Ba musu Anwar ya biyo bayansu har zuwa bakin motarsa ya kunna Magaji Saif da Sarki Ubaiyd

suka shiga baya suka zauna Anwar ya shige wajen driven yaja motar suka fita daga cikin harabar asibitin.

Sai bayan sun hau titi sannna Anwar yake tambayar.

"Abba ina zamu je ne?".

"Gidansu yarinyar da Fudhal yake so zaka kaimu".

Magaji Saif ya bashi amsa, Anwar ya take burki da sauri ba tare daya sani ba domin jin abin da Magaji Saif ya faɗa.

"Subhanallahi..! Lafiya Anwar?".

Suka tambayeshi a tare.

"Babu komai burkinne yaɗan kwace mun".

***

Tsaye suke jikin bishiyar darbejiyar dake ƙofar gidansu Aynu, sun shafe tsayin lokuta bayan gaisuwa ba tare da ɗaya daga cikin su ya sake furta ko kalma ɗaya ba, ko wanne yana saƙe-saƙe cikin ransa.

Ya Sayyadi Umar shine ya katse shirun tare da yin gyaran murya kafin yace.

"Ya shirye-shirye kuma ya gajiya?".

Aynu taɗanyi murmushi tana mai bashi amsa.

"Alhamdullahi".

"Masha Allah, sai dai kamar akwai abin da  yake damunki duk naga kin rame sosai lafiya kuwa?".

"Lafiya ƙalau wallahi, kasan  zirga-zirga ma ta ishi mutum ya rame ya fita haiyacinsa".

Ya Sayyadi Umar ya gyaɗa kai kawai, amma a zahiri bai gamsu da amsar data bashi ba.

"Na tambaye ki Aynu".

"Uhm ina jinka".

"Ina so ki faɗamin tsakaninki da Allah kada ki ɓoyemin dukkan abin da yake cikin ranki".

"Insha Allah zanyi ƙoƙarin ganin na gaya maka gaskiya akan abin da nasani  akan dukkan abin da zaka tambaye ni".

"Masha Allah, Aynu dan Allah har yanzu a cikin ranki kina son Fudhal?".

Dammm gaban Aynu ya buga take taji ƙwalla na shirin zubowa daga idanuwanta tayi ƙoƙarin mai da ita tare da dai-daita nutsuwarta kafin tace.

"Amma me ya kawo wannan maganar?, koma zan so wani ai a dane yanzu dole kai zan so domin nan da ranar juma'a  kai zaka zamo miji agare ni".

Ya Sayyadi Umar yaɗanyi gajeren murmushi kafin yace.

"Haka ne maganarki shikenan Allah ya nuna mana ranar".

"Amin".

"Babu wani abu da kike buƙata ko?".

Aynu gyaɗa kai tayi ba tare data iya bashi amsa da bakinta ba.

Shiru ne ya sake ziyartar wajen tsayin lokaci Ya Sayyadi Umar na kallon Aynu yana karantar yanayinta yana son yi mata magana akan Fudhal sai dai ya rasa ta Inda zai fara, kuma yana fargabar yanda zata ɗauki maganar.

Har dai daga ƙarshe sukayi sallama ya tafi, tana tsaye har ya ɓacewa ganinta mai makon tayi gida sai ta wuce gidansu Zainab sabida gidansu jama'a bazata samu damar sakewa ba.

Tana shiga gidan suka gaisa da Baba Ta Sallah kai tsaye ɗakin Zainab ta wuce  ta faɗa kan katifa tahau rera kuma sosai tsananin son ganin Fudhal da tausayin halin da yake ciki yana taso

mata  har bata san sanda Zainab ta shigo ɗakin ba tana yi mata magana.

Aynu ta ɗago jajayen idanuwanta tana duban Zainab ba tare da tace komai ba, Zainab tazo ta zauna kusa da ita tare da dafa kafaɗarta tana faɗin.

"Haba Aynu har zuwa wanne lokaci ne zaki yi haƙuri ki danganawa Allah komai akan al'amarinki da Fudhal ne?".

"Bawai rashin dangana bane Zainab ina tausayawa halin da Fudhal ya shiga akai nane, shi kuma haka ƙaddararsa tazo  a kaina?, duk yanda naso daurewa zuciyata kasawa nake Zainab, wallahi inason sake ganin Fudhal ko da sau ɗaya ne a rayuwata, ina takaici tare da jin haushin kaina a kan abin da nayi masa nasan duk nice sila..!".

Takai maganar tana mai sake fashewa da kuka, Zainab ta dafa bayanta.

"Kiyi haƙuri Aynu kada ki ɗorawa kanki laifin abin da bake kika aikata ba, kisa a ranki haka Allah ya ƙaddarowa Fudhal kada kidinga ɗorawa kanki laifi kisa damuwa a ranki har tazo tajawo maki wani ciwon".

HELLO MY FANS

TEAMS AYNUL-FUDHAL

TEAMS AYNUL-UMAR

Nidai nace AYNUL......! Lol

ASHA KARATU LAFIYA SAI TOMORROW INSHA ALLAH.

BYEEE.

*YARIMA FUDHAL*

Na
FIRDAUSI S.A (QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

SADAUKARWA:-Namesy Phirdausy Jeebour.

42

Suna isa dai-dai kan layin gidan Anwar yayi parking motar suka fito suka taka da k'afafuwansu.

Tun da suka shiga layin Magaji Saif da Mai Martaba suke bin gidajen da kallo tunaninsu bai ta'ba kawowa akwai unguwar da talauci yayi k'atutuba irin wannan unguwar musamman Sarki Ubaiyd sai gashi yazo da k'afafuwansa nemawa kansa suruka a cikin unguwar da ko a cikin taswirar garin bai ta'ba tunanin akwai ta ba bare a taswirar kansa.

Suna isa k'ofar gidan Anwar ya nemi yaro ya aike shi domin yayi musu sallama da Baban Aynu.
Bayan mintuna kad'an yaron ya fito tare da fad'in.

"Wai ance yana zuwa".

Anwar ya zaro Naira d'ari a aljihun wandonsa ya bawa yaron tare da fad'in.

"Nagode kaji".

Yaron ya tafi cike da murna, bayan wani lokaci sai ga Baban Aynu ya fito domin ganin wad'anda ke sallama da shi, duk jikinsa ruwa da dukkan alamu fitowarsa kenan daga wanka.

Ganin Mai Martaba yasa shi fad'ad'a murmushinsa yana yad'in.

"Ashe kune ?, sannunku da zuwa bari in fito da tabarma ciki mutane sunyi yawa da mun shiga daga ciki.

Magaji Saif ne ya amsa da.

"Babu komai wallahi ".

Baban Aynu ya koma ciki Jim kad'an sai gashi d'auke da tabarma ya shimfid'a musu k'ark'ashin bishiyar darbejiyar suka zauna tare da gag-gaisawa, Magaji Saif ya bud'e baki ya fara magana.

"Nasan kayi mamakin ganinmu a dai-dai wannan lokaci, kuma nasan ni ba zaka shaida ni ba, ni sunana Magaji Saif yaya ne ga Sarki Ubaiyd na wannan gari, mun zone ba dan komai ba sai dan mu baka hak'uri akan abubuwan da suka faru, ka sani duk abin da yake faruwa bani da masaniya wallahi kasancewar na shafe tsayin shekaru bana garin nan, sai yau Allah ya dawo dani kuma ansanar dani komai hak'ik'a Ubaiyd ya biyewa son zuciya da giyar mulki ina fatan zaka gafarce mu?".

Baban Aynu yad'an gyara zama tare da gyaran murya.

"Babu komai wallahi dama can ban rik'e Sarki Ubaiyd acikin raina ba ko kad'an, kuma naji dad'i da kuka gane gaskiya dama anaso idan mutum yayi kuskure ya gane kuskurensa hakan yayi kyau nima na gode sosai".

Shiru ya gauraye wajen har nawasu tsayin lokuta kafin Magaji Saif ya ci gaba da magana.

"Sai dai kuma muna tafe ne da wata buk'ata mai girma ina fatan ba zaka duba abubuwan da suka faruwa ba a baya ba".

"Insha Allahu ai komai ya wuce wacce buk'ata ce wannan?".

Magaji Saif yad'anyi shiru kafin yace.

"Akan dai maganar yarinyarka da d'an namu ne Fudhal muna rok'onka ka dubi Allah ka dubi halin da d'anmu yake ciki ka taimaka ka bamu auren 'yarka".

Baban Aynu ya d'an girgiza kai.

"Amma da kadaina had'ani da Allah Magaji hak'ik'a kazo da batu mai girma kafin kuzo nan basu sanar maka cewa jibi wato ranar juma'a za'a d'aura auren Aynu ba?".

"Sun sanarmin amma ba wannan za'a duba ba halin da yaron yake ciki shine abin dubawa".

"E hakane amma sai dai kunzo a k'urar-ran lokaci bani da damar da zan iya yi muku wannan alfarmar kuyi hak'uri Allah ya bawa Fudhal lafiya ya kuma bashi wadda tafi Aynu".

"Amin".

Suka amsa Sarki Ubaiyd dake zaune gefe tun zuwansu ya kasa furta komai haka kawai yau yaji Baban Aynu yayi masa kwarjini sosai jin amsar da Baban Aynu ya bayar shine ya sanya shi bud'e baki da sauri yana fad'in.

"Nima bazanyi k'asa agwiwa ba wajen baka hak'uri ba, dan Allah ka ceci rayuwar d'ana ka bashi Aynu".

"Ai rayuwar d'anka na wajen Allah ba waje na ba, idan yaso ya rayu ko ya auri Aynu ko bai aurata ba tabbas zai rayu, haka kuma idan lokacinsa yayi koya aure ta Kobe aure ta ba tabbas zai mutu kama daina danganta rayuwar d'anka da Aynu, idan banyi kuskure ba zan iya cewa dukkan abin da ya faru da d'an ka Kaine babban mai laifi".

"Ka sani arziki da talauci babu abin da basa bayarwa a rayuwa ka inganta rayuwarka data iyalinka shine abu mafi ma'ana da mafita ".

"Ka sani bawai ina fad'a maka bane domin in rama abin da kaimin ko kusa wallahi, ina fad'ane kawai domin intuna maka da abin da ka mance".

"Allah gafururrahim ne idan yaso ya azurtaka babu Wanda ya isa ya hana, haka kuma idan yaso ka da talauci babu Wanda ya isa ya azurtaka, daraja dan Adam da girmamashi kowanne iri ne yana da fa'ida sosai domin Allah subhanahu wata'ala da kansa ya fad'a a cikin alk'ur'ani cewa.

"(WALAK'AD KARRAMNA BANIY ADAMA WAHAMALNAHUM FIL BARRI WAL BAHRI WARAZAK NAHUM MINAL 'DAYYIBATI WA FADDALNAHUM ALA KASIYRIM MIMMAN KALAK' NA TAFDIYLA)".

Ma'ana:-(Kuma lallene mun girmama d'an Adam kuma muka d'aukesu a cikin k'asa da teku, kuma muka azurtasu daga abubuwa masu dad'i, kuma muka fifitasu akan masu yawa daga wad'anda muka halitta fifitawa).

"Hak'ik'a wannnan ayar ko ita kad'ai ta isa mu girmama junanmu mu 'yan adam tare da mutun tawa , domin agurin Allah bamu da wani ban-banci duk abu d'aya ne mu bayi ne a gareshi dole ne mu bauta masa indai muna son dace wa da samun cikawa da imani, Allah ya yafemu baki d'aya abisa laifin da mukayi masa na fili da na b'oye".

"Amin".
Suka sake amsawa.

Sarki Ubaiyd baiyi k'asa a gwiwa ba ya matsa har Inda Baban Aynu ke zaune ya rik'o hannunsa yana fad'in.

"Mai kake so a duniya? Wanda zanyi maka da zai sanya ka bawa dana auren 'yarka, kud'i ko mulki? ka fad'i dukkan abin da kake so zanyi maka indai har zaka bawa Fudhal auren Aynu ko sarautar tawa kake buk'ata zan baka wallahi akan dai in rasa d'ana mafii soyuwa a cikin raina".

Baban Aynu ya girgiza kai yana mai k'arewa Sarki Ubaiyd kallo domin ya tabbatar da gaskiyar abin da yake fad'a, tabbas yaga tsan-tsan nadama sosai a idanun Sarki Ubaiyd, Baban Aynu yayi hamdala cikin ransa afili kuwa ya furta.

"Bana buk'atar komai naka Mai Martaba, sai dai abin da bakina ya furta d'azu har a yanzu shi d'in zai sake furtawa kayi hak'uri zan taya d'anka Fudhal addu'ar samun macen da tafi Aynu tare da fatan samun lafiyarsa s...!".

Maganar Baban Aynu ta katse a dai-dai sanda suka tsinkayi sallamar mutum a kusa dasu ko wannansu ya d'aga kai sama domin ganin mai Sallamar.

Ya Sayyadi Umar ne ya cire takalminsa ya nemi guri d'an nesa da su ya zauna akan tabarmar tare da gaishesu dukansu suka amsa.

Ya Sayyadi Umar ya bud'e baki zaiyi magana Baban Aynu yq katse shi da fad'in.

"Wannan shine yaron da zai aureta ai".

Magaji Saif da Sarki Ubaiyd sukabi Ya Sayyadi Umar da kallo.

Ya Sayyadi Umar yad'anyi gyaran murya.

"Baba daman nazo ne kan wata magana".

"To intaso kenan ".

"A a muyi maganar anan, dama maganar nan ne huruminta".

"To masha Allah ina jinka Mallam Umar".

Cewar Baban Aynu kenan yayin da dukansu suka bada a tension wajen Ya Sayyadi Umar domin jin abin da zai fad'a.

"Baba nasan zaku ji maganar da baku tab'a zata ba kuma bakuyi tsammani ba, na riga na yanke hakan kuma inaji a raina alkhairi ne yin hakan banajin zanyi kuskure ko kad'an, Baba tun ranar da abokin Fudhal yazo ya d'auke ni wato Anwar ya kaini na dubo Fudhal tun daga ranar zuciyata ta kasa samun nutsu inaji araina kamar nine na yiwa rayuwar Fudhal karan tsaye a yau inajin dad'i tare da godiya ga Allah har cikin raina zanyi abin da ba duk wani masoyi ne zai iya ba, bantab'a tunani ko ji araina zan iyayin sadakar soyayata ba amma ayau ni UMAR FARUK na SADAUKAR GA SOYAYYATA GA YARIMA FUDHAL, Ma'ana na barwa Fudhal Aynu ya aura

duniya da lahira ina fatan nima Allah yayi min zab'in mafificin alkhairi...;".

"Kai Umar..! Kasan me kake fad'a kuwa?".

"Na sani Baba.!, Idan banyi hakan bane banajin kona auri Aynu zuciyata zata zauna lafiya domin Aynu babu Wanda take so aduniya fiye da Fudhal ni nasan hakan, Aynu ta yarda zata aure ni ne kawai domin yin biyayya agareku amma bawai dan tana so naba".

"Amma Umar kana ganin hakan ya dace?".

"Sosai ma Baba kayi musu fatan alkhairi kawai, sai dai ina rok'on wata alfarma Baba".

"Ina jinka Umar".

"Kamar yanda aka sanya d'aurin auren nan banaso a fasa a d'aura auren Aynu wa Fudhal ranar juma'a dan Allah  Baba kayimin wan nan alk'awarin".

Baban Aynu yayi shiru tsayin lokaci yana kallon fuskar Ya Sayyadi Umar yama rasa abin da zaice domin ya Riga ya d'aure shi da jijiyoyin jikinsa akan dole yace.

"Nayi maka alk'awari Umar kamar yanda kace insha Allahu ranar juma'a za'a d'aura auren Fudhal wa Aynu bi iznillahi ta'alah, Allah yayi masa albarka yasa ka gama da duniya lafiya ya baka dukkan farin ciki duniya da lahira kamar yanda ka faranta rai kaima  ".

"Amin Baba babu komai ai".

Magaji Saif, Sarki Ubaiyd, Anwar sakar baki da hanci sukayi suna kallon Ya Sayyadi Umar tare da jinjinawa tsananin jarumtarsa wajen iya sadaukar ga soyayyarsa lokaci guda haka.

Fuskar Sarki Ubaiyd tuni ta jik'e da hawaye yama rasa mai zai cewa Ya Sayyadi Umar da k'yar dai ya iya furta.

"Mungode Umar Allah yayi maka albarka yayi maka sakayya kan abin da ka aikata na alkhairi nayi alk'awari dukkan abin da kake so a duniya ka fad'amin zanyi maka kada kaji nauyi ko kunya domin bani da abin da zan saka maka dashi nan duniya sai dai Allah ya saka maka".

Anwar kuwa mik'ewa tsaye yayi ya rungumeshi yana fad'in.

"Mungode.! Mungode..!! Mungode...! Sosai Umar bani da bakin da zan iya yi maka godiya kayi abin da wad'anda zasu iyayin hakan basu da yawa a duniya Allah ya baka wadda tafi Aynu Umar mungode".

"Amin ya Allah".

Magaji Saif kuwa murmushi kawai yake dokawa domin yama rasa bakin magana daga k'arshe dai yace.

"Babban albishir d'in da zan iya yimaka kawai shine ni Magaji Saif na bawa Umar auren Jalilah 'ya ga k'anina Sarki Ubaiyd sauran tukwicinka kuwa sai mun zauna".

Ba Ya Sayyadi Umar ba hatta Anwar da Baban Aynu basu san sanda murmushi ya kufce musu ba dan tsabar farin ciki da jindad'i jin wannan babban tukwici da Magaji Saif yayi masa, Sarki Ubaiyd kuwa girgiza kai kawai yake hawaye ne a fuskarsa amma kuma murmushi yake.

YAU DAI NASAN TUKWICINA NA MUSAMMAN NE AGAREKU *AYNUL-FUDHAL* INA JIRA NA CIKA MUKU BURIN KU YAU.

TO AYNUL-UMAR YA KOMA JALILAH-FARUK

KU KUMA WANNE IRIN TUKWICI ZAKU BANI INA JIRA

BYEE..!

*YARIMA FUDHAL*

NA
FIRDAUSI S.A(AURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

SADAUKARWA:-NAMESY PHIRDAUSY JEEBOUR.

43

Ya Sayyadi Umar ya durƙusa yayi godiya duk da cewar bai san wacece Jalilah ba? bai taɓa ganinta ba amma ba zai iya cewa baya so ba, a kan dole ya amince kenan da auren Jalilah?.

Su Mai Martaba sukayi addu'a tare da roƙon Allah ya sanyawa auren albarka Ya Sayyadi Umar yayi musu sallama ya tafi amma kafin ya tafi ya roƙesu akan kada asanarwa Aynu komai har sai anɗaura auren kuma ko wanne daga cikin su ya amince da wannan batun.

Sannan suma sukayiwa Baban Aynu sallama suka tafi kowa zuciyarsa cike fal da farin cikin wannan rana.

Suna komawa asibitin kai tsaye Magaji Saif da Sarki Ubaiyd office ɗin doctor suka nufa, Anwar kuwa ɗakin da Fudhal yake jinya ya nufa yana shiga su Hajiya da Aunty Sadiya suka tsare shi da tambayar abin da ya faru.

Bai wani tsaya tunanin komai ba ya sanar musu duk kan abin da ya faru zuciyar Fulani Bingel da Aunty Sadiya suka cika da farin ciki Sa'idah kuwa ba zaka iya shaida yanayin da take ciki ba farin ciki ne ko akasin hakan.

"Doctor ya jikin Fudhal ɗin kuwa?".

Cewar Magaji Saif kenan tare da tsare Doctor da idanuwa domin jin amsar da zai basu.

Ya cire farin glass ɗin dake manne bisa idonsa yana kallonsu fuskarsa wasai.

"Jikin Fudhal alhamdulillahi kullum yana ƙara samun lafiya may be nan da Friday muna saran farfaɗowarsa sai dai abin da nake ƙara tuna muku idan har ana son ɗorewar samuwar lafiyarsa dole ne idan ya farka ya fara sanya abin da yafi so a cikin idanunsa, amma idan aka samu akasin hakan ba zan iya cewa wani abu ba domin rayuwa da mutuwa duk na Allah ne amma

mudai fatanmu ya samu lafiya".

"Haka ne Doctor insha Allahu komai yazo ƙarshe ai, zai samu abin da yake so da yardar Allah".

Faɗin Sarki Ubaiyd kenan yana mai miƙewa domin fita daga office ɗin, sukayi musabiha suka fito kai tsaye ɗakin da Fudhal yake suka nufa domin ƙara dubo yanayin jikin nasa.

***

WASHE GARI

Baban Aynu na zaune ƙofar gida tare da muƙar-rabansa sai ga samari nata shigowa layin ɗauke da kayan abinci suna ajiyewa ƙofar gidan nasu Aynu.

Baban Aynu ya cika da mamaki sosai ya miƙe ya tari ɗaya daga cikin samarin.

"Yaro anya nan akace ku kawo kayan nan?".

"E nan ne Baba".

"To amma waye ya aiko ku?".

"Mai Martaba ne yace mu kawo nan ai muna tare da abokin Yarima Fudhal shine ya nuna mana gidan ma".

Daga nan Baban Aynu bai kuma cewa komai ba ya zuba ido kawai yana kallon yanda ake jere kayan abinci ƙofar gidansa Wanda har bayan biki sai sun shafe tsayin watanni shida basu nemi abinci ba.

Suna gama kawo wa Anwar ya ƙaraso zuwa inda Baban Aynu da mutanansa ke tsaye cirko-cirko ya durƙusa ya gaishe su, suka amsa .

"Amma Anwar irin wannan hidima haka?".

"Baba babu komai ai daga Mai Martaba ne wannan aiken yace a gaisheka".

"Ina amsawa Anwar kayimin godiya sosai, sai nazo da kaina".

"Babu komai Baba".

Ya kai maganar tare da zaro rafar yan ɗari biyar ya miƙawa Baban Aynu yana faɗin.

"Ga wannan yace kuɗin cefane ne".

"Bayan wadan nan kayan kuma?".

"E Baba ".

"To angode Allah ya saka da alkhairi".

Baki ɗaya ƴan gurin suka amsa da "Amin".

Su Aynu nacan gidan lalle da gyaran jiki anata fama wanda duk wannan abubuwan ƙoƙarin Zainab ne dan dai ta Aynu da babu abin da zatayi sabida abin da yake damunta kaɗai yasa baki ɗaya bata sha'awar komai ba kuma tajin farin ciki da wannan auren ko kaɗan ji take acikin ranta tamkar wannana auren yayiwa rayuwarta karan tsaye.

Damuwa da faɗuwar gaba sun tsananta agareta cikin kwanakin nan, hakan ne yasa baki ɗaya ta rame ta zama kamar wata mai ciwo, mutane sai cewa suke fargabar biki ce sai dai ita kai tasan abin da yake damunta.

A ranar da yammaci akayi walima kamar yanda suka tsara amarya tayi kyau sosai cikin wata doguwar riga pink data sha stone fari mai ratsin blue tayi rolling kanta da mayafin doguwar riga Wanda shima pink ne, ƙawar amarya kuma aminiya doguwar riga blue ta saka mai ratsin stone pink yayin da sauran al'umma sukayi shigar after dress baƙa maza kuma jallabiya abin gwanin ban sha'awa ankira malamai mata sunyi wa'azi sosai akan aure da zamantakewar rayuwa tayau da kullum, anci ansha a walimar abin da al'umma basu taɓa zata za'ayi ba a taron walimar shine ya faru.

Duk yanda Aynu taso su haɗu da angonta Ya Sayyadi Umar ƙi yayi sai taga kamar ma gudunta yake yi abin da ya ƙara dagula mata lissafi kenan ba ita bama hatta Zainab abin yaɗaure mata kai sai dai kawai tana ƙoƙarin kwantarwa da Aynun hankali ne amma a can ƙasan zuciyarta damuwace ita ma a cunkuce.

RANAR JUMA'A...!.

Bahaushe yace "Rana bata ƙarya sai dai uwar ɗiya taji kunya".

A ranar juma'a ƙarfe goma da rabi na safe za'a ɗaura auren.

Mai Martaba da Magaji Saif tare da muƙar-rabansu tun ƙarfe goma da ƴan mintuna suka halacci wajen ɗaurin auren kar kuso kuga gayyar jama'ar dake tare dasu wai danma auren yazo a ƙurarren lokaci.

Tuni unguwar ta kaure da kaɗe-kaɗe da bushe-bushe yara maza da mata sai gudu suke zuwa

cikin gidansu Aynu suna bada bayanin ɗaurin auren Aynu har dasu Sarkin garin Umman Aynu dake tasan komai sai dai kawai tayi murmushi sauran jama'a kuwa faɗi suke.
"Ohh auren Aynu da farin jini yake harda sarki yazo da kansa.

Su Aynu na can gidansu Zainab anata shirye-shirye ita kuwa ta shige cikin ɗaki ta kwanta kawai ita kanta ba zata iya cewa ga abin da yake damunta ba, Zainab ce ta dage mata har dai ta tashi ta hau shiri itama.

10:30Am

Goma da rabi dai-dai Baban Aynu ya fito cikin wata da kak-kiyar farar shadda hula da takalmin ƙafarsa ma duk farare ne wanda duk aikin magaji saif ne, aka ɗunguma baki ɗaya zuwa masallacin da za'a ɗaura auren.

Magaji Saif shine ya miƙa kuɗin sadakin Aynu dana jalilah Naira dubu hamsin hamsin tare da kuɗin aure shima dubu hamsin nan take aka ɗaura auren.

FUDHAL UBAIYD SALMAN

Da

AYNUL-HAYAT ABDALLAH

Da

UMAR FARUK KHALEEL

Tare da

JALILAH UBAIYD SALMAN

Kan sadaki dubu hamsin hamsin wanda duka Magaji Saif ne ya biya.

Abin da masu shela suka hau faɗi kenan take gurin ya kaure da kaɗe-kaɗe.

Mai Martaba dai Allah-Allah yake ayi agama komai sabida a yaune ake saran farkawar Fudhal yana gudun faruwar wani abun.

Mutanan da sukaje ɗaurin auren baki ɗaya saranda sukayi jin da wanda aka ɗaura auren sai sukaji tamkar kunnuwansu bai jiye musu dai-dai bane, sai da suka sake ji masu shela nata mai-maitawa nan fa kawunan kowa ya kulle masu farin ciki nayi akasin haka nayi.

Kanwar Zainab ce mai suna Jamila ta shiga gidan da gudu tana faɗin.

"Aunty kinsan da wa aka ɗaura auren Aunty Aynu?".

Zainab ta dubeta a gaggauce tana shirya Aynu.

"Dawa za'a ɗaura banda Ya Sayyadin mu".

Jamila tayi dariya.

"To baki canka ba Aynu dai da Yarima Fudhal aka ɗaura aurenta".

Zee tayi tsaki tana faɗin.

"Aikin banza aike kin shiga uku da ƙarya".

Jamila tayi kwafa taji haushin maganar Zee hakan yasa ta shiga ɗakin Baba ta Sallah ta ɗauko redio ɗinta ta kunna musu.

Jin abin da ake sanarwa a radio yasanya duk yan matan dake gidan kasa kunne domin tabbatar da a abin da suka fara ji da farko.

Ai ana sake mai-maitawa Zee ta rungume Aynu tana faɗin.

"Alhamdulillahi Aynu yau addu'armu ta karɓu kin zamto mata ga Fudhal mai yafi wannan daɗi?".

Aynu kuwa ta kasa furta komai illa ruwan hawaye dake bin fuskarta kona Mene oho?.

"Amma ya akayi abubuwa suka canja haka?".

Cewar Zee kenan harara Aynu ta jefa mata.

"Ta ina zan sani nima ".

Sukayi dariya tare da tafawa.

"Yanzu Ya Sayyadinmu ya zama angon Jalilah ƴa ga Sarki Ubaiyd, Fudhal ya auri Aynu? abin mamaki Allah mai yin yanda yaso".

Abin da sauran ƴan matan dake gidan suke faɗi kenan.

Zee tayi dariyar jin daɗi tana mai ƙarewa ƙawarta kuma aminiyarta kallo sosai taji daɗin

wannan al'amari kuma tana matuƙar taya Aynu murna da farin ciki.

Mai  Martaba kasa jurewa yayi har sai da yaja Baban Aynu gefe ya sanar dashi buƙatarsa da kuma abin da Doctor yace.

Baban Aynu shima ya amince domin yana ganin yanzu sune suke da iko da Aynu ba shi ba.

Mai Martaba yayi murna sosai da amincewar Baban Aynu.

Magaji Saif kuwa na can ya sanya samari sai jido akwatuna suke suna shiga dasu gidansu Aynu akwati goma sha biyu haka aka jeresu a filin tsakar gidansu Aynu, Umman Aynu da Baba ta Sallah ta sanar mata kayan da aka kawo tsabar farin ciki saita fashe da kuka abin da bata zataba abin da ko a mafarki bata taɓa kawowa ba wai Aynu ce yau ta zamto mata ga ɗan sarki jikan Sarki Allah mai yanda yaso da bayinsa.

Baban Aynu ya sanya aka kira masa su Aynu mintuna kaɗan sai gata tare da Zainab.

Ya sata cikin ɗakinsa ya sanar da ita komai sannan yace zata bi su Mai Martaba yanzu asibiti inyaso idan komai ya dai-daita zata dawo.

Aynu tace babu komai domin yasan dama ba zata taɓayi masa musu ba ya sanar da itane dama domin ya fidda ita daga cikin duhu ne.

Anwar shine yake driving yayin da Magaji Saif yake zaune kusa dashi a baya kuma Mai Martaba tare da wazirinsa.

Sai motarsu Aynu driver ne kawai yake ja sai Aynu da ita da Zainab kawai a motar domin ance babu wanda zai bisu sabida asibiti zasuje itama Zainab ɗin dan dai kawai kada a bar Aynu ita kaɗai ne ba zataji daɗi ba.

Tun da suka tafi basuyi parking ko ina ba sai cikin harabar asibitin a parking space.

Kai tsaye ɗakin da Fudhal yake jinya suka shiga Fulani Bingel da Aunty Sadiya suka taso cike da farin cikin ganin Aynu ita kuwa sai ta sanya kanta cikin mayafi sabida wata irin kunya da taji ta lulluɓeta.

Ta gaishesu tare da samun guri ta zauna ta takure waje ɗaya Zainab ma ta nemi guri kusa da ita ta zauna kowa ya amsa gaisuwarsu amma ban da Sa'ida dake ta cika tana batsewa.

Sai dai kuma babu wanda ya lura da hakan illa su Aynu.

*YARIMA FUDHAL*

NA
FIRDAUSI S.A (QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

SADAUKARWA:-NAMESY FIRDAUSY JEEBOR.

44

Babban ɗan yatsan ƙafarsa ne ya fara motsawa sai kuma leɓansa da yake buɗe shi a hankali alamun yana ƙoƙarin furta wani abu ne.

Anwar shine ya fara lura da hakan da sauri ya miƙe daga inda yake zaune ya nufi bakin gadon yana faɗin.

"Abba kamar ya farka fa?".

Da sauri dukansu suka mime suka ƙarasa bakin gadon a dai-dai sanda yake ta ƙoƙarin buɗe idanuwansa dishi-dishi ya fara ganinsu baya iya shaida ko suwaye hakan ne yasa shi mai da idonsa ya rufe kafin ya sake buɗewa yana ƙoƙarin ɗago ƙafafuwansa da yake ji sun zame masa tamkar dutse a jikinsa.

Da sauri Anwar ya fice daga ɗakin domin kirawo Doctor.

Yana fita Yarima Fudhal yana buɗe bakinsa sosai yana salati ya sake buɗe idanunsa akaro na biyu yana duban dukkan waɗanda ke tsaye jikin gadon domin jiran farfaɗowarsa.

Idonsa na gama wayewa ya fara binsu da kallo ɗaya bayan ɗaya alamun yanason tuna wani abu.

A dai-dai lokacin Anwar da Doctor suka shigo ɗakin, Doctor da Anwar suka miƙar da shi zaune tare da karashi jikin pillow.

Doctor ya lura da matso leɓansa da yake lokaci zuwa lokaci hakan ya sanya shi kara kunnensa dai-dai bakin sa.

"Ina AYNU?".

Kalmar da yaji ya furta kenan.

Doctor ya juyo yana duban su mai martaba dake ta sharar kwallar farin ciki.

"Tambaya yake ina Aynu".

Dukkansu suka juyar da kallonsu inda Aynu ke zaune kanta na ƙasa tana ta wasa da zoben hannunta.

Aunty Sadiya ta ƙarasa da sauri ta riko hannunta har zuwa jikin gadon ta tsai da ita tana mai kallon fuskar Fudhal.

Aynu dai kanta na ƙasa hannunta na rike da gefan karfan gadon tana murzawa ko kaɗan ta kasa ɗago kanta bare har ta iya kallon Fudhal.

Shi kuwa Fudhal ƙura mata ido kawai yayi babu ko kiftawa yana son gasgata abin da idanuwansa ke nuna mana ne, domin gani yake tamkar irin mafarkin daya saba yi ne a kullum.

Doctor yaɗan dafa kafaɗarsa yana faɗin.

"Ga Aynun taka nan".

Sannan ya juyo kansu Fulani Bingel yace.

"Kuɗan bashi ko da tea ne idan ya buƙaci wani abu bayan wannan zaku iya bashi".

Yana kaiwa nan ya fice daga ɗakin ya barsu.

Sarki Ubaiyd ya ƙarasa gefan gadon da Fudhal yake ya zauna tare da kallon ɗan nasa yana faɗin.

"Sannu ya jikin naka?".

Fudhal dai bai amsa ba illa kawai kallon Baban nasa da yake.

Sarki Ubaiyd ya ci gaba da faɗin.

"Ga Aynu nan yanzu ta zama taka halak malak, domin a yau ɗin nan aka ɗaura aureta da kai, tare da Amince wata da ta iyayenta".

Yarima Fudhal bai san sanda wani murmushi ya suɓuce masa ba sai a lokacin ya buɗe bakinsa da ƙyar yace.

"Amma Abba Umar ɗin ya yarda?".

"E mana shine yace ma ya barmaka ka aura, yanzu Umar surikinka ne domin Babanku Magaji Saif ya bashi auren Jalilah".

Yarima Fudhal yayi murmushi har sai da fararen haƙoransa suka baiyana, sai kuma yayi shiru tsayin lokaci yana nazarin maganar tare da kafe Aynu da ido.

"Abba tace ai bata so na".

Jin Kalmar da ya furta ya sanya Aynu ɗago kai da sauri ta dube shi tuni idanuwansu suka sarke da juna wani irin abu ya ziryaci Aynu tun daga babban ya tsan ƙafarta  har kwakwalwarta da sauri ta sauke kanta ƙasa domin ba zata iya jure kallonsa ba.

Yarima Fudhal yayi wani irin murmushi dana kasa gane fassarar sa  kafin ya mai da kallonsa kan Anwar yana faɗin.

"Zanyi brush".

Magaji Saif dake gefe ya taso da sauri ya kamashi kallon kallo aka hauyi tsakanin Fudhal da Magaji Saif Fudhal ya ƙarasa saukowa ya taka kafafuwansa bisa kasa, amma can ƙasan zuciyarsa cike take da tambayar.

"Waye wannan mai matukar kama da Abbansu sai dai kawai yafi Abbabsu girma".

Magaji Saif kamar yasan mai  FUDHAL yake tunani, murmushi ya ɗanyi kaɗan yace.

"Ni ne Magaji Saif da kaji Abbanku ya faɗa wato Yaya ga mahaifinku".

Yarima Fudhal yaɗanyi murmushi kaɗan tare da guam kai alamun gamsuwa da maganar Magaji Saif, Magaji Saif ya kamashi har toilet ya raka shi ya dawo.

Yarima Fudhal yayi brush ya fito ya zauna bakin gado, Aunty Sa'ida ta miƙo masa cofin tea ya karɓa yahau sha, yana sha yana duban Aynu dake zaune bisa tabarma ita da Zainab suna hira jefi-jefi murmushin da takeyi kaɗan-kaɗan shine abin da yafi komai Jan hankalinsa sosai  .

Abba dake zaune gefansa yana lura da yanayinsa shi kanshi sai yanzu ya ƙara tabbatarwa da irin ƙaunar da ɗansa kewa Aynu.

Gyaran murya ya ɗanyi kafin yace.

"Hajiya ku shirya ke dasu  Sadiya muje gida a ɗauko masa abin da yake ɓukata sai driver ya dawo daku sabida ni yau muna da meeting".

Magaji Saif yayi caraf yace.

"Sai mu tafi tare dama zanje wani waje nima, Anwar da su Aynu sai su zauna kafin su Hajiyar su dawo sai Anwar ɗin sai ya mai dasu gida".

Haɗa kayansu Aunty Sa'ida tahauyi  Yarima Fudhal na zaune gefan gadon baice dasu komai ba, domin tun da kowa dama yasan halinsa da rashin son yin magana bare kuma yanzu.

Suna gama haɗawa sukayi masa sallama tare da fatan Allah yakara masa lafiya suka fice suka tafi.

Suna fita Anwar ya koma inda Mai martaba ya tashi ya dubi Fudhal cike da murmushi yana faɗin.

"Mutumina yaufa buri ya cika gaka ga Aynunka ya kamata mu Baku waje ku gaisa domin naga alamun kuna buƙatar hakan".

Yarima Fudhal murmushi kawai yayi ba tare daya bashi amsa ba.

Anwar ya dubi Zainab.

"Muɗan basu waje Zainab su gaisa ko".

Aynu tayi saurin faɗin.

"Aa ku zauna wallahi a hakanma zamu gaisa".

Tayi maganar ba tare data ɗago kanta ba.

Anwar ya dubi Yarima Fudhal daya Kafe Aynu da ido kawai, yayi murmushi yana mai bata amsar.

"Idan ke bakya buƙata mijinki na buƙatar hakan, tashi mu fita Zainab".

Zainab babu musu ta miƙe tana dariya suka fice daga ɗakin, suka bar Yarima Fudhal da Aynu.

Tsayin lokaci ɗakin yayi shiru tamkar babu mutane a cikin ɗakin, sai can Fudhal yayi ƙarfin halin faɗin.

"Zo nan Aynu".

Ba musu ta miƙe ta tako har zuwa inda yake zaune gefan gado ta tsaya a gefansa ba tare data dube shi ba.

"Babu gaisuwa bare tambayar ya jikin nawa ko haryanzu kina jin haushi nane?".

"A a, ya jikin naka?, Allah kara sauki".

Takai maganar cikin siririyar muryarta.

Yarima Fudhal yayi murmushi yace.

"Bana buƙata sai da na roka?".

"Aa kafinnayi ne ka rigani tambay...!".

Kafin takai ƙarshen maganar sai ji tayi ya kamo hannunta ya haɗa da nata, da sauri ta ɗago kai suka hada ido ya sakar mata wani irin tsadaddan murmushi wanda itama bata san sanda ta mayar masa da Martani ba tare da yin ƙasa da kanta.

Yarima Fudhal ya jawo ta zuwa dai-dai inda yake zaune gefan gado suna fuskantar juna ita na tsaye.

"Na tambaye ki mana Aynu.!".

"Har yanzu kina sona kuwa?".

Aynu ta ɗago kai da niyar bashi amsa sai dai kuma taji nauyinsa game da kunyarsa sun lulluɓeta ta sakeyin ƙasa da kanta.

Tattausan hannunsa ya sanya ya ɗago haɓarta tare da kafeta da idanuwansa mai sanya wanda yake kallonsa jin kasala.

Aynu kasa juran kallon nasa tayi ta rintse idonta gam, Yarima Fudhal yayi ƴar dariya kaɗan.

"Wai duk kunyata kike ji haka?".

Bata bashi amsa ba haka kuma bata buɗe idon ba.

Fudhal ya saki haɓarta ya sake kamo hannunta da hannunsa duka biyun yariƙe yana kallon zanan Jan lallan da fulawan da akayi mata.

"Kai amma yayi kyau flawer ɗin yakai hannun nata bakinsa ya sunbata, Aynu ta janye hannunta da sauri tana kallonsa sai kuma ta sake sauke idanuwanta kasa.

Yarima Fudhal bai kuma cewa komai ba ya jawo pillow ya kwanta abinsa ya barta nan tsaye, tsayin lokaci a haka.

Aynu na ɗago kai taganshi kwance abinsa idanunsa a rufe yanayin yanda yake fid da numfashi ne ya tabbatar mata da yayi bacci sosai abin ya bata mamaki ƴan mintuna kaɗan amma ace yayi bacci?, sai kuma ta tuna ai bashi sa lafiya ne.

Ƙarasawa tayi dai-dai kansa ta gyara masa pillow ɗin tare da ɗora masa hannunsa dake miƙe kan gado bisa ƙirjinsa ba tayi aune ba sai jinta tayi ta faɗa kan ƙirjin nasa da sauri ta zaro ido waje sabida tsorata da tayi.

Yarima Fudhal ya sanya dariya.

"Ba kyaso inga kwalliyar in yaba ne?".

Kai kawai ta girgizama masa alamun Aa tana kici-kicin kwace hannun amma ta kasa sabida irin riƙon da yayi mata, turo ƙofar da akayi ne yasa ta samu damar janye hannun nata tana duban mai shigowar.

Anwar ne tare da Doctor suka shigo.

Yarima Fudhal yaja guntun tsaki tare da kau da kai gefe, Anwar yayi murmushi kawai, Aynu kuwa kunyace ta lulluɓeta taji kamar ƙasa ta tsage ta shige.

Doctor ya tambayi jikin nasa tare da dubashi sosai ya juyo kan Aynu yana faɗin.

"Ya kamata a dinga bashi Magani akan lokaci sabida gujewa samun matsala".

Aynu ta gyaɗa kai dai-dai sanda Zainab ta shigo ita ma ta nemi guri ta zauna, Doctor na gama duba shi zai fita kenan su Hajiya sukayi sallama suka shigo ɗauke da kulolin abinci da kayan Fudhal.

Aunty Sadiya ce ta buɗe baki tana tambayarsa mai zai ci yanzu?.

Ya bata amsa da faɗin.

"Ko mene ma bani inci".

Ta koma kan kulolin tahau zubo masa makaroni da miya taji naman rago, tare da tsiyaya masa lemo a cofi.

Ta kai masa gabansa ta ajiye.

A hankali ya ɗauki cokali yahau ci jefi-jefi yana kai kallonsa kan Aynu shi kan shi ya rasa dalilin da yasa ya kasa daina kallonta haka kawai yake jin daɗin kallon nata duk da ita bata sanma yanayi ba hirarsu kawai suke da Zainab.

"Ku tashi muje in mai daku gida ko?".

Cewar Anwar kenan yana mai miƙewa daga kan kujerar da yake zaune, Yarima Fudhal najin haka ya ajiye spoon din dake hannunsa take yaji ya ƙoshi ya ture abincin gefe.

Suka miƙe tare da yiwa Hajiya da Aunty Sadiya sallama, sannan suka ƙarasa inda Fudhal yake zaune sukayi masa sallama tare da faɗin.

"Allah ya ƙara lafiya".

Wanda duk Zainab ce take maganar Aynu kunya ta hanata ko ɗaga kai.

Haka suka fice daga ɗakin koda sau ɗaya Aynu bata kuma bari sun haɗa ido da Yarima Fudhal ba, shi kuwa abin da ya ƙara baƙanta masa rai kenan take yaji zaman asibitin ma baki ɗaya ya gundure shi.

*YARIMA FUDHAL*

NA
FIRDAUSY S.A (QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

SADAUKARWA:-NAMESY FIRDAUSY JEEBOR.

45

Zaune take cikin lambun dake farfajiyar gidansu akan wata tat-tausar darduma gefanta matane su biyar zagaye da ita ga kayan mar-mari kala-kala ajiye a gabanta.

Ƴan matan sai hira suke mata na ban nishaɗi tana dariya can ta ɗan bata rai tana duban su dukansu suka sha jikin jikinsu.

Tsaki ta ɗanyi tana mai duban matar dake gefan hannun damarta.

"Ku bani shawara Jummai akan batun aurena da Yarima Jaleel mana".

Wacce aka kira da Jummai ta gyara zama tare da rissinawa.

"Haba Gimbiya aike kanki kinsan yanzu kin wuce ajin Yarima Fudhal, Yarima Jaleel shine wanda yafi dacewa dake a wannan lokaci, sabida ba girmanki bane ba kuma ajinki bane ace ki auri mai mata matarma Baiwa gaskiya da ance kin ci baya".

"Yanzu kuna ganin aurena da Jaleel shine yafi?".

"Sosai kuwa ranki ya daɗe".

Sukayi maganar cikin haɗa baki, Gimbiya Safiyya tayi murmushi wanda har sai da fararen haƙoranta suka baiyana waje.

"Kuce ingayawa Babana na amince kenan?".

"E mana".

Suka sake bata amsa.

Gimbiya Safiyya tamiƙe da sauri ta nufi cikin gida suka take mata baya.

***

"Ladidi duk laifin kine wallahi kece kika haddasamin wannan masifar.!".

"Kamarya Hajiya?, ai bokan da kansa yace sawun Yarima Jaleel aka kai bana Yarima Fudhal ba, kinga kenan laifin na wanda ya ɗebo sawun ne bana wanda ya kai ba".

Fulani Sokoto tayi shiru tsayin lokaci tana kallon Ladidi kafin tayi ajiyar zuciya tace.

"Yanzu kenan meye abin yi?".

"Mene kuwa abin yi?, Yarima Fudhal dai ya samu abin da yake so, Yarima Jaleel ma haka, Gimbiya Jalilah kuma an ɗaura mata malamin islamiyya, ke ya kamata ki yanke wannan hukuncin Hajiya ba ni ba".

Fulani sokoto tayi tsaki mai tsayi tana huci.

"Ni auren Jalilah da wancan faƙirin shine yafi komai ɗaga min hankali wallahi taya zan samu a wargaza komai idan yaso maji da matsalar Fudhal da Jaleel".

"To ki kira shi awaya muji mana".

Fulani Sokoto ta janyo wayarta dake gefanta tahau dad-dan nawa alamun tana neman layin nasa, ringing biyu ya ɗaga tare da ƙunduma wani ashar itama Fulanin ta mayar masa kamar yanda yayi kafin ya kece da wata irin dariya yana faɗin.

"Basai kin faɗa ba munsan komai ai sun sanar damu".

"To annemo mafita akan matsalar?".

"Aure dai mutu ka raba ne babu yanda za'ayi mu iya raba auren, kuma zan faɗa miki abu guda ɗaya muddun kika matsa akan raba auren to tabbas zaki mutu..!".

Dammm gaban Fulani ya buga ta saki wayar ta faɗi bisa carpet ɗin tsakar falon tana duban Ladidi, Ladidi tayi saurin ɗaukan wayar tana faɗin.

"Lafiya Hajiya?".

Da ƙyar Fulani Sokoto tayi ƙarfin halin faɗin.

"Yace aure babu rabuwa kuma idan muka matsa akan raba auren tabbas zan mutu".

Ladidi taja tsaki.

"To kuma Sai ki yarda da abinda da yafaɗa?, yanzu hakama kawai gani yayi bazai iya aikin ba shiyasa yace dake haka, kawai tun da abin hakane mu canja wani malamin kawai".

Fulani Sokoto shiru tayi tsayin lokaci tana nazari kafin ta gyaɗa kai.

"Kuma maganarki akwai ƙamshin gaskiya fa, dannima kwanakin nan naga aikinsa baya tafiya yanda ya kamata yanzu wajenwa kike ganin zamu je?".

"E to akwai wani acan kauyen SAMU NAKA ance shima aikinsa kamar yanda wuƙa inaga muje muji mai zaice shima".

"Yanzu yaushe zaki je?".

"Yanzuma idan kin bani dama sai in tafi inyaso gobe na dawo da safe".

"Ai hausawa sunce da zafi-zafi akan daki ƙarfe ungo wannan maza kije".

Ta miƙo mata rafar ' yan ɗari biyar-biyar, Ladidi tayi godiya ta miƙe tare da ficewa daga cikin ɗakin.

"Sannu Jaleel ya jikin naka?".

"Da sauƙi Abba sai dai ciwon ciki yana takuramin sosai cikin kwanakin nan".

"OK Allah ya ƙara lafiya, ai likita yace babu wata matsala indai kana shan magani cikin ƙa'ida zai dai na".

"To zan kiyaye Abba".

Magaji Saifa dake gefe ya dubeshi tare da faɗin.

"Wani babban albishir zan maka yanzu amma sai kayimin alƙawarin ba zaka kuma shan wani abin maye ba".

"Nayi alkwari wallahi bazan kuma sha ba".

Magaji Saif da Sarki Ubaiyd sukayi murmushi

"Kasan dai mahimmancin alƙawari dai?".

"Na sani Abba kuma zan kiyaye".

Magaji Saif yayi murmushi a karo na biyu tare da dafa kafaɗar Yarima Jaleel kafin yace.

"An sanya ranar auren ka da Safiyya Sati mai zuwa idan ka fito daga asibiti".

Take wani sanyin daɗi ya lulluɓe Jaleel bai san sanda ya rungume Magaji Saif ba yana godiya har da guntun hawayensa.

Sun jima sosai suna hira kafin su koma ɗakin Yarima Fudhal suka barshi daga shi sai Jalilah domin Fulani Sokoto bata dawo ba.

Yana zaune gefan gado yayi shiru can gefe kuma su Hajiya ne da Aunty Sa'ida yau Aunty Sadiya bata zo ba sabida anjima kaɗan da yamma zasuje ɗaukan amaryar Fudhal wato Aynu amma shi Fudhal bai san da hakan ba.

Magaji Saif ya dubeshi yana faɗin.

"Yadai Fudhal tunanin me kake kuma?".

Fudhal yayi murmushi.

"Babu komai Kawu".

Murmushin sukayi dukansu yace.

"Yau dai muna fatan Doctor zai sallameka mu huta da mita kullum akan angaji da zaman asibiti".

"Kawu ai gani nayi na warke sumul mai kuma zanyi anan?".

"Gaskiyarka babu abin da zakayi kuwa".

Yakai maganar tare da ƴar dariya.

Doctor ne ya shigo a bayansa Anwar ne suka gaisa Anwar ya nemi guri ya zauna yayin da Doctor yahau duba Fudhal har sai da ya gama sannan ya dubi su Sarki Ubaiyd yace.

"Ga takardar sallama nan akula da maganinsa kuma sosai, Jaleel ma inaga zuwa gobe zamu sallameshi".

Wani irin daɗi ne ya lulluɓe Fudhal har sai da farin cikinsa ya kasa ɓoyuwa.

Tuni Aunty Sa'ida da Hajiya suka miƙe suka hau haɗa kayansu, Anwar na kaiwa mota yana sakawa har sai da suka gama kaf sannan suka fita zuwa harabar asibitin.

Anwar ne yayi driven ɗinsu Hajiya da Fudhal, su Abba kuma driver ne ya ɗaukesu.

Suna dosar layin suka fara jin kaɗe-kaɗe da bushe-bushe na tashi na murnar dawowar Yarima Fudhal.

Gidan cike dam-ƙam da al'umma sai kaiwa da komowa suke haka suka yi ta ratsa mutane ana gaishesu suna amsawa har zuwa cikin fada Sarki Ubaiyd ya zauna Anwar da Fudhal suka wuce ciki zuwa ɗakin Fudhal.

Suna shiga kai tsaye Fudhal toilet ya nufa domin ya watsa ruwa yana fitowa yahau shiri cikin wata da kakkiyar farar shadda wadda tasha aikin zare light blue hular kansa da takalminsa har zuwa agogonsa duk light blue ne ba karamin kyau yayi ba a wannan lokacin.

Anwar dai na kallonsa bai ce masa komai ba har sai da yagama sannan ya dube shi yace.

"Wai ina zaka haka kake ta faman shiri?".

Yarima Fudhal ya ɗan tsaya daga fesa turaren da yake ya dubi Anwar yana bashi amsa.

"Ina zanje wanda ya wuce wajen mata ta,".

Anwar ya sanya dariya yana faɗin.

"Tab..ai tuni ka makaro domin yanzu haka ana kan hanyar zuwa kaita gidan Aunty Sadiya ne.

Yarima Fudhal ya ajiye kwalbar turaren ya juyo gaba ɗayansa yana duban Anwar.

"Mai zatayi a gidan Aunty Sadiya kuma?".

"Wannan sai dai ka tambayi Hajiya kuma itace ta bada wannan umarnin".

Yarima Fudhal yayi tsaki  take wata irin gajiya ta ziyarce taking yayi wurgi da hularsa bisa katifa ya cire babbar rigar ya wurgar ya nemi guri kan katifar ya kwanta.

Anwar ya bishi da kallo kawai abin sosai ya bashi dariya amma sai dai ya kanne domin sanin halin mutumin nasa.

Har akai kiran sallar maghriba yana nan kwance shi bai ma san sanda Anwar ya fice daga ɗakin ba sai da ya buɗe idonsa sannan yaga baya nan.

Miƙewa yayi yayo alwala yayi sallah ya ɓata tsayin lokaci azaune yana addu'o'i tare da godewa Allah.

Can ya miƙe ya nufi inda babbar rigarsa take ya sanya ya mai da hularsa ya sake feshe jikinsa

da turaruka ya ɗauki wayarsa ya kunna tare da key din mota ya fice daga gidan.

Akan hanya ya kira Anwar yana tambayarsa yana ina?, gashi nan zuwa, Anwar ya bashi amsa da yana gidansu Saima, tsaki Fudhal yaja yana faɗin.

"Da maghribar nan me zakayi mata me zatayi maka?".

Dariya sosai Anwar yasa ka yana faɗin.

"Idan kazo zan baka wannan amsar ".

Ya kashe wayar, Fudhal ya ajiye wayar a gefansa yana mai ci gaba da kallon titi tuƙinsa yake a nutse yayinda kira'ar sudes ke tashi kaɗan-kaɗan cikin motar.

Yana isa bakin gate yayi parking motarsa ya fito ya knocking ƙofar gidan mai gadin ya leƙo ganin Fudhal yasanya shi buɗewa da sauri domin ya sanshi sosai.

Yana shiga ya kirashi yazo mintuna biyar sai gasu sun fito a tare da ka gansu kaga waɗanda suka jiƙe a mayen so da kaunar junansu.

Duk da Saima yanzu Anwar take so kuma take burin aure Amma ganin Fudhal bai hana ƙirjinta bugawa ba sosai taga yayi mata kwarjini fiye da koyaushe haibarsa ta ƙaru wani irin sihirtaccen kyau na bayyana a jikinsa ganin kallon da take masa ya sanya shi kau da kai yana murmushi ya dubi Anwar.

"Sai ka janyota jin gulma kuma?".

Saima tayi ƙarfin halin yin siririyar dariya, Anwar yace.

"To meye a ciki ?, abin da nan da sati muma zamu angwance gara tasan irin matsayinta a wajena tun yanzu".

Yarima Fudhal ya gyaɗa kai kawai yana faɗin.

"Baka koya mata gaisuwa ba kenan?".

Saima tayi saurin faɗin.

"Barka da dare".

"Riƙe gaisuwarki bana buƙata".

"Kaga mallam sauri fa nake ka sallameta mu tafi kawai".

Saima ta danne ɓacin ranta kawai domin tasan halin Fudhal shi ba abin damuwarsa bane disga mutum gaban kowa, hakan kuma ko a takalminsa bare abin ya dameshi kai da akayiwa sai dai haushi ya kashe ka.

Anwar yace.

"Ai munyi sallama dama zuwa tayi ku gaisa kawai".

"OK mutafi to muna bata time, nagode Saima ki gaida su Mama".

Abin da yace kenan yana mai kama hanya ya fice daga cikin harabar gidan, Anwar yabi bayansa yana ɗagowa Saima hannu itama ta mayar masa da martani.

Anwar ne yayi driven nasu har zuwa ƙofar gidan Aunty Sadiya yana parking Yarima Fudhal ya fice daga motar baiko jira Anwar ɗin ba.

Gidan shiru kamar babu kowa sai da yayi sallama kusan sau biyar daga bakin ƙofar falon sannan Aunty Sadiya dake can saman mijinta ta sauko tana amsa masa.

Ya shigo tare da neman guri kan kujera ya zauna yana tambayarta ƴan biyu.

"Suna ɗaki sunyi bacci ne".

Anwar yayi sallama ya shigo yana faɗin.

"Nagode Fudhal".

Ya juya gun Aunty Sadiya suka gaisa Fudhal dai baice komai ba illa baza ido kawai da yake can dai ya kasa haƙuri yace.

"Ina Aynu take ne?".

Dubanshi Aunty Sadiya tayi tana faɗin.

"Ganin Aynu ba yanzu ba".

"Kamarya ba Yanzu ba?".

"E mana umarmi aka bani".

"Nasanma wasa kike nidai dan Allah tana ina?"

"Allah ba wasa ba, umarnin Hajiya da Abba ne".

"Ya Allah..!"

Yarima Fudhal ya furta yana mai dafe kai.

"Sai yaushe to ?".

"Sai nan da sati wato randa za'a kawo matar Jaleel ranar za'a kai maka taka kai ma".

Tsaki yaja mai tsayi tare da kwafa.

"Amma dai gaskiya ba'amin adalci ba inason ganin Aynu wallahi Aunty".

"Sai dai fa kayi haƙuri aikin gama ya gama".

Yarima Fudhal yayi shiru yana duban Aunty Sadiya da Anwar kawai yama rasa mai zai ce.

*YARIMA FUDHAL*

NA
FIRDAUSY S.A (QURRATUL-AYN).

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®

SADAUKARWA:-NAMESY FIRDAUSY JEEBOR.

Nacin duniyar nan Yarima Fudhal yayi amma Aunty Sadiya tace bata san zancen ba, a kan dole suka tattara suka bar gidan ba tare daya samu ganin Aynu ba zuciyarsa ta cika fam da haushi.

Hakan yasa duk surutun da Anwar ke tayi masa a mota bai kulashi ba domin sosai yau haushin kowama yake ji gani yake kamar ba sonsa suke ba.

Har suka isa gida Yarima Fudhal bai kula Anwar ba haka Anwar ɗin yayi masa sallama ya wuce gida domin shi al'amarin Fudhal ma dariya yake bashi, idan yana abu wani time ɗin sai kaga kamar wani ƙaramin yaron goye.

Anwar na fita Yarima Fudhal ya rage kayan jikinsa ya shige toilet domin watsa ruwa sabida wani irin zafi da yake ji a lokacin, daya fito kaya ya nema marasa nauyi ya saka ya fice daga part ɗinsu zuwa part ɗin Hajiyarsu wato Fulani Bingel.

Da sallamarsa ya shiga falon babu kowa ciki illa Hajiyartasu dake zaune tana kallon tashar Zee world, ta jiyo cikin fara'a tana amsa masa sallamar.

Yarima Fudhal ya ƙarasa inda take zaune ya zauna a ƙasa kusa da ƙafafuwanta yana faɗin.

"Barka da dare Hajiya?".

"Muna lafiya, ya ƙarin ƙarfin jikin naka?".

"Alhamdulillahi".

"Masha Allah..!, Ina kaje ne na shiga wajen naka baka nan?".

"E munɗan fita nida Anwar ne".

"Fita kuma?, daga fitowarka daga asibitin haka FUDHAL ai ka bari kaɗan ƙara murmurewa ko?".

Fudhal murmushi kawai yayi ba tare da yace komai ba ya mai da kansa kan TV yana kalla, amma a zahiri ba kallon yake ba baki ɗaya tunaninsa ya tafi akan neman mafita wajen ganin Aynu.

Can dai ya motsa ya dubi Hajiyar wadda itama shi take kallo domin tun shigowarsa taga alamun akwai abin da yake son faɗi amma kuma ya kasa furtawa.

Hajiya tace.

"Yadai Magaji akwai wata matsala ne?".

Yarima Fudhal ya gyara zama yace.

"Ammmm..dama..dama".

"Kayi magana mana inajinka".

Yarima Fudhal ya ɗan dubi Hajiya yau baki ɗaya wata irin kunyarta yake ji haɗe da jin nauyinta amma haka ya daure ya sake buɗe bakin yace.

"Kan maganar Aynu ce Hajiya, naje gidan Aunty Sadiya tace wai...!".

Sai kuma yayi shiru ba tare daya iya ƙarasawa ba, Hajiya tayi murmushinsu na manya tace.

"E nasan abin da kake son cewa, kayi haƙuri har zuwa sanda aka yanke kaji?".

Yarima Fudhal ya gyaɗa kai kawai ba tare daya iya cewa komai ba, domin bai zaci wannan amsar daga bakin Hajiyartasa ba.

Haka yayi mata sallama ya koma part ɗinsu ranar ko kaɗan kasa cin abinci yayi sabida shi gani yake tamkar gidan Aunty Sadiya babu tsaro za'a iya zuwa a ɗauke masa Aynu.

***

RANA BATA ƘARYA...!.

Cikin satin nan kullum sai Fudhal yaje gidan Aunty Sadiya amma Allah bai sanya idanuwansa sunga Aynu ba ko da sau ɗaya, gani yakema kamar kawai faɗa akayi Aynu bata gidan.

Rana ɗayane suka kusan haɗuwa.

Ana ijibi ɗaurin auren su jaleel ranar ta shiga kitchen ɗin Aunty Sadiya domin ta ɗora ruwan wanka sun ɗauke nepa tana ɗorawa shi kuma ya shigo kitchen ɗin neman cofi.

Inda Allah ya taimake ta tayi saurin tsugunawa dake irin kitchen ɗin nan ne mai kanta a tsakiya, kuma bai wani tsaya dube-dube ba yana ɗauka ya fice.

Ranar kusan awanta uku a kitchen  tana jira ya tafi har sai da Allah ya taimaketa akayi masa waya ya tashi ya fice daga falon aikuwa da gudu ta ɗauko ruwan zafin ta shige ɗaki domin itama bala'in nauyinsa takeji gani take ba zata iya haɗa ido da shi ba.

RANAR JUMA'A DA MISALIN 2:00.

Bayan saukowa daga masallaci aka d'aura auren.

JALEEL DA GIMBIYA SAFIYYA

ANWAR DA SAIMA.

Ɗaurin auren yayi jama'a sosai, Fudhal tamkar shine aka ɗaurawa auren a lokacin, shigarsu iri ɗaya sukayi dukansu su ukun bluen yadi wanda yasha aiki irin na sarauta.

Daka kallesu dole su birgeka hardai Fudhal da Jaleel dasu ke matuƙar kama tamkar ƴan biyu ga kayan ya amshesu sosai duk da shima Anwar ɗin ba baya ba wajen kyau da haiba.

Da dare aka fara hayaniyar kai amare gidajensu, Jaleel da Fudhal dama tuni an gyare musu part ɗinsu nanne za'a kawo musu amaren, Anwar shi kuwa gida ya gina guda acan ƙasan layin gidansu gidane mai kyau da tsari.

Sai da aka ɗauko amaryar Anwar aka kaita gidanta sannan aka wuce ɗaukan nasu Fudhal mutane kaso uku aka rabu wasu suka tafi ɗaukan amaryar Fudhal wasu kuma ɗauko ta Jaleel domin ta baro sokoto tana nan gidan Yayan Babanta, sai kuma wasu suka tafi kai amarya Jalilah wadda tasha kwalliya da alkyabba sai buga kamshi take.

Gidan da Magaji Saif ya danƙawa Mallam Umar nanne aka kai Jalilah gidan sosai ya haɗu dai-dai zaman mutum ɗaya.

Fulani Sokoto ranar tayi kuka mutane sun ɗauka kodan rabuwa da ɗiyarta ta ne, amma a zahiri ba hakan ba ne baƙin ciki ne kawai ace wai ƴarta kamar Jalilah itace yau za'a kai gidan wani baƙirin mutum kuma malamin islamiyya da bai aje komai ba bare ya bayar.

Babu yanda ba tayi da Jalilah ba akan tace bata so amma ƙememe Jalilah ta to she kunnuwanta akan taji ta gani zatayi biyayya ga mahaifanta domin ita yanzu ba zata ce bata son mahaifitarta ba sai dai baki ɗaya halayenta sun cire mata arai, gashi bata da bakin maganar da zata iya yi mata maganar da dazata fahimta.

Sai dai kullum tazo ta ƙaraci bambamin faɗanta ta fita, amma Jalilah bata taɓa zuwa tayiwa Mai Martaba zancen Mallam Umar ba tun ranar da suka kirata suka sanar da ita anɗaura mata aure ko kan bata ji wani ciwon a ranta ba, addu'ama ta dingayi Allah yasa mijin ya sota itama ta soshi suyi zaman lafiya da amana sosai Mai martaba da Magaji Saif sunji daɗin biyayyar Jalilah akansu musamman Magaji Saif da kokaɗan baiyi tunanin hakan ba.

To taya kuma yanzu tashi ɗaya zataje tace musu bata so?, bayan sun bata dukkan nin yardarsu

da amincewarta.

DARE
9:30.

Misalin ƙarfe tara da rabi na dare aka kawo amaren gidan Sarki Ubaiyd, Gimbiya Safiyya da Aynu tuni gidan ya rincaɓe da guɗar ƴan kawo amare sai kusan 11 dai-dai sannan kowa ya watse aka bar Amare da ƙawayensu kawai.

A dai-dai lokacin ne angwaye sukayi sallama abokan Yarima Fudhal suka rakashi part ɗin sa na Jaleel ma sukayi part ɗin Jaleel.

Zee na idar da sallah sukayi sallama tayi maza ta naɗe shinfiɗar tana tsokanar wani Mukhtar abokin Fudhal dake ta san shi sosai.

Shi kuwa gogan naka sai faman kwaɗa murmushi yake idanuwansa kafe kan Aynu dake zaune tsakiyar gado kanta lulluɓe da mayafi.

Nan dai akayi siyan baki cikin raha da nishaɗi tare da yi musu nasiha angwaye sukayi musu sallama suka tafi tare da ƙawaye amarya Aynu tariƙe hannun Zee ƙam wai a dole ba zata tafi ta barta ba da ƙyar ta lallaɓeta ta fizge hannun suka tafi.

Haka suma sauran angwaye anyi siyan baki lafiya kowannensu angwayen sunyi musu nasiha sosai mai ratsa jiki kafin kowa ya watse dakin ya rage sai amarya da ango kawai.

Suna fita Yarima Fudhal ya matso inda Aynu ke zaune suna fuskantar juna yasa hannu ya janye mayafin dake kanta fuskarta ta baiyana a fili sai yaga Aynun kamar ba wadda ya sani ba.

Sosai yau kyawunta ya fito fiye da koyaushe duk da ruwan hawaye dake kan kuncinta sai yaga hakan ba ƙaramin yi mata kyau yayi ba ga kuma uwa uba kamshin turarenta daketa dokar masa hanci.

Tattausan hannunsa yasan ya ya ɗago fuskarta suna kallon juna Aynu ce tayi saurin sauke kai ƙasa yayin da hawaye ya cigaba da bin kuncinta.

Hannu yasa ya sake ɗago fuskarta akaro na biyu yana mai share mata hawayen yace.

"Mene na kuka kuma, ko bakya farin ciki da wannan ranar ne?".

Aynu shiru tayi kawai ganin bata da niyar bashi amsa yasa shi faɗin.

"Kina da alwala?".

Kai ta gyaɗa alamun E amma acan ƙasan zuciyarta fargaba ce fal ciki.

Yarima Fudhal ya miƙe tare da cire babbar rigar dake jikinsa ya shige toilet mintuna kaɗan sai gashi ya dawo jikinsa duk ruwa da alamun alwala yayi.

Ya buɗe wardrobe ya ɗauko abin sallah ya shimfiɗa sanann ya sake buɗe wani murfin jikin wardrobe ɗin ya ɗauko mata hijab ya miƙa mata Aynu ta karɓa cike da mamakin hijab ɗin waye ya bata?.

Shi yayi musu limanci suna idarwa Yarima Fudhal ya shafe tsayin lokaci yana addu'a kafin yayi sallama ya kama kanta yayi mata addu'a sosai sannan ya dubeta ya fara yi mata tambayoyi akan addininta kamar yanda yazo a koyarwar addinin musulunci, tana bashi amsa dai-dai da abin da ta sani.

Sosai Yarima yaji daɗin yanda Aynu tasan addini domin shi a rayuwarsa yana son mutum wanda ya san addininsa bare kuma matarsa uwar ƴaƴansa.

Suna gamawa yajawo ledar dake gabansa ya buɗe da ƙwalan kajini kwala-kwala guda biyu aciki sai Freeshyo manya-manya suma guda biyu gefe guda kuma kilishi ne sai tashin kamshi yake.

Yarima Fudhal ya miƙe ya fito zuwa falo kai tsaye kitchen ya nufa ya ɗauko musu plat da kofuna ya dawo, da kanshi ya zuba musu freesh ɗin ya juye kilushin a plat tare da kazar.

Ya yago yakai mata bakinta takau da kai, sai da taga ya ɓata rai sannan takarɓa tana ci a hankali sosai yanda take cin kazar ya tafi da imaninsa ya shagala a kallonta, sai da ya tabbatar ta ƙoshi sannan shima yaci yana gamawa ya kwashe komai ya kai kichen.

Yanda ya barta haka ya tadda ita murmushi yayi kawai ya nufi wardrobe ya ɗauko wata sleepingdress ya miƙa mata ya juya yahau cire kayansa Aynu ta ɗauke kanta da sauri yayi murmushi domin yana kallonta.

Toilet ya faɗa da dukkan nin alamu wanka zaiyi Aynu najin ya shiga tayi maza ta cire kayanta ta ɗauki rigar zaya saka taganta guntuwa iya gwiwa gata shara-shara tsaki tayi aranta tana faɗin bazata iya sawa ba.

Ajiyeta tayi gefe ta mai da kayanta ta koma can ƙarshen gado ta kwanta tare da lullubɓe jikinta da bargo.

Ko da yafito yaga rigar a gefe kallonta ya tsayayi kawai sai kuma yaga ashe tayi bacci dariya ya ɗanyi mai sauti ya ƙarasa jikin mirrow ya shafa mai tare da feshe jikinsa da tuararuwa sannan shima ya ɗauki wani boxer nasa ya saka yahaye gefan gadon ya kwanta tare da janyo Aynu.

Firgigit ta farka Jin antaɓata yanda ta farka ya bashi dariya sosai amma ya kanne yana faɗin.

"Ki rage kayan jikin ki zakifi jindadin baccin zafi ake fa".

Aynu ta takura waje ɗaya kawai tana sauraronsa murmushi ya sakeyi tare da matsawa inda take ya dafa kafaɗarta da hannu biyu yace.

"Duk wannan tsoron na meye?, ki kwantar da hankalinki babu abin da zanyi miki wallahi kin yarda da ni?".

Aynu ta gyaɗa kai alamun E.

"OK idan Kin yarda dani da gaske jeki canja kayan naki, idan kuma rigar batayi miki ba ki duba cikin wardrobe ki ɗauki wata duk kayanki ne cike kinji?".

"To"

Abin da tace kenan tana mai saukowa daga kan gadon Yarima Fudhal yabita da kallo, shi yanda take nuna jin tsoransa ma dariya yake bashi sosai.

*YARIMA FUDHAL*

NA
QURRATUL-AYN.

NAGARTA WRITER'S ASSOCIATION®.

SADAUKARWA:-NAMESY FIRDAUSY JEEBOR.

47

Wardrobe ɗin ta buɗe ta dubo wata riga mai ɗan dama-dama ta shige toilet ta saka sai kuma ta kasa fitowa hakan yasa ta ɗaura zaninta akai tare da yafo mayafinta ta fito a hankali ta koma gadon ta kwanta dan tunaninta yayi bacci domin ta ɓata tsayin lokaci a toilet ɗin kafin ta fito.

Shi kuwa yana jinta yana kuma kallonta duk da duhun dake ɗakin dariyarsa kawai yake ciki-ciki.

7:00am

Bata tashi farkawa ba sai ƙarfe bakwai dai-dai da a gogon ɗakin ya buga ta buɗe ido taga haske garin miƙa tayi tare da salati ta ganta lulluɓe da bargo daga ita sai rigar baccin data saka kanta ko ɗan kwali babu bare kuma zanin data san ta ɗaura akan rigar da mayafin data naɗe kanta dashi damm gabanta ya faɗi ta dafe kai tare da salati.

Miƙewa tayi da sauri ta ziro ƙafafuwansa ƙasa ta zauna bakin gadon tana sauraron taji ko yana toilet, jin shirun da taji yayi yawa ya sata miƙewa ta nufi bakin toilet ɗin da niyar bugawa sai kuma taga ƙofar ta buɗe ta leƙa taga babu kowa ajiyar zuciya tayi tana mai cigaba da tunanin abin da ya faru jiya amma ta gaza tuna komai tun daga kwanciyarta kan gado bacci ya ɗauketa bata tuna komai bayan nan.

Ganin tana ɓata lokaci da yawa ya sata shigewa toilet ɗin domin yin wanka tare da alwala.

Ko da ta fito sai gani tayi an yaye zanin gadon an bar shimfiɗar haka ta taka zuwa bakin gadon cike da mamaki jin hayaniyar da tayi a bakin ƙofar dakin ya sanyawata juyawa da sauri.

Su Larai ta gani su uku tsaye bakin ƙofar suna wani cika da batsewa batayi aune ba sai ji tayi sunja hannunta sunyi waje da ita tana turjewa tana komai, bata tashi ganinta ako ina ba sai filin tsakar gidan tana ɗaga idonta ta ganta tsakiyar mutanen gidan kowa na kallonta tayi saurin takure jikinta sabida daga ita sai rigar baccin dake jikinsa kawai aka fito da ita.

"Me kike wani jin kunya bayan kin riga kin gama zubar da mutunci tun a waje, Gimbiya Safiyya dai ta ciri tuta domin ta kawo budurcinta gidan mijinta, sai dai ba muyi zaton Yarima fanko zai

aura ba?".

Cewar Larai kenan, Fulani Sokoto dake tsaye gefe tayi dariya tare da ƙarewa Aynu kallo.

"Waya san ma ina aka shiga aka fita?, domin ni dama tunda Fudhal ya nace nasan ba lafiya ba da walakin goro a miya".

Tuni sauran bayin gidan suka hau salati da sallallami, zuwan Fulani Bingel wajen ya sanyasu da katawa suna duban ta domin jin mai zata ce.

"Meye haka kukeyi kuma?".

"Babu komai surukarki dai ta zubar da mutunci da ƙimarta Larai nuna mata".

Larai ta buɗe farin bedsheet ɗin tana nunawa Fulani Bingel, Fulani Bingel ta dafe kai cike da takaici ta girgiza kai tana faɗin.

"Wai har yaushe ne za'a bar wannan mummunar al'adar ne?".

"Babu rana kam".

Cewar Fulani Sokoto kenan tana wani cika da batsewa, Larai ta buɗe bedsheet ɗin ɗakin Gimbiya Safiyya tuni aka hau ihu da murna gurin ya kacame kowa na tofa albarkacin bakinsa a kan Aynu ita kuwa tuni fuskarta ta jiƙe da ruwan hawaye sai shash-sheƙar kuka take.

Tsawar fudhal da sukaji ne ya sanyasu yin shiru tsaye gefansa kuma Anwar ne kallo ɗaya zakayi masa kasan ransa a ɓace yake sosai, takawa yayi har zuwa inda Aynu ke tsaye a takure tana shash-sheƙar kuka sai ji tayi kawai anyi sama da ita ta buɗe ido da sauri sai ganinta tayi ɗauke a hannun Fudhal tayi maza ta sake runtse idonta yayin da hawayen ya cigaba da bin kuncinta.

Bai ajiyeta ko ina ba sai kan gado ya kwantar da ita tare da janyo bargo ya rufa mata sabida ganin da yayi tana kakkarwa, yasa hannu ya share mata hawayen har alokacin bata buɗe idon ba.

Su kuwa suna ganin ya ɗauke ta tuni kowa ya kama gabansa Fulani Bingel tayi murmushi kawai itama ta bar wajen.

Fudhal na fita bai zame ko ina ba sai ɓangaren Fulani Sokoto ya sameta ita dasu Larai anata mai da zance da dariya  tsawa ya daka musu yana duban Larai tare da faɗin.

"Ka da in sake ganin ki cikin gidan nan, ki tattara ki fice kafin in dawo".

Bai jira mai zasu ce ba ya fice daga falon Fulani Sokoto ta bishi da kallo kawai Larai kuwa tuni ta fara tsima tare da hawaye tace.

"Kin gani ko?, Hajiya abin da nayi gudu kenan".

"Kefa sokuwa ce wallahi Larai shi ai ba shi da iko kan bayina kamar yanda bani da iko akan nasu kwantar da hankalinki babu inda zaki je".

Yarima Fudhal ya wuce part ɗin Hajiyarsu ya sameta tare da su Anwar zama yayi tare da gaisheta bai kuma faɗin komai ba yayi shiru kowai can dai ya buɗe baki yace.

"Wai Hajiya ba zakuyi magana adaina wannan mummunar al'adar ba?".

"Taya za'a daina Magaji?, abu ya samo asali tun kaka da kakanni mu da muka zo yanzu meye namu a ciki?".

Yarima Fudhal yaja guntun tsaki cikin ransa yana mai mid ba tare da yace komai ba suka fito tare da Anwar.

A hanya  Anwar ke faɗin.

"Ai duk abin da ya faru laifinka ne fa Fudhal kasan al'adar gidan nan taya zakayi sake har hakan ta faru?".

Yarima Fudhal yaja dogon tsaki yana duban Anwar.

"Kai nifa ba wannan ne a gabana ba, akwai dalilin da yasa ni yin hakan kawai".

"Kamar ya..! Mene dalilin kuma?".

Yarima Fudhal ya tsaya daga tafiyar da yake yana duban Anwar tare da faɗin.

"Ina so in tabbatar wa da Aynu irin son da nake mata, ni zan iya zama da ita har a bada ba tare da wani abu ya shiga tsakaninmu ba".

Anwar ya bi Yarima da kallon takaici yama rasa mai zaice masa can dai yace.

"Hmmm ayi dai mu gani?".

"Zaku gani kuwa".

Fudhal ya bashi amsa suka ci gaba da tafiya suna zuwa kofar part ɗin su Fudhal sukayi sallama Anwar ya tafi gida shi kuma ya shige wajen sa.

Inda ya barta nan ya sameta sai faman takurewa take ya taka inda take kwance da sauri ya taɓa goshinta da wuyanta zafi sosai alamu fever ya kamata.

Yaye bargon yayi tare da miƙewa zuwa gaban mirrow ya dauko man shafawa ya ajiye gefan gadon sannan ya koma jikin wardrobe ya buɗe ya ɗauko mata doguwar riga yellow mai ratsin baƙi ya ajiye gefe, Aynu na kallonsa ya ɗago da ita ya ɗorata bisa ƙafarsa yahau shafa mata man sai da ya gama sannan ya shiga kici-kici zare mata rigar zai sanya mata mai ɗan kauri ta rintse idonta sosai dai-dai sanda taji ya janye rigar daga jikinta.

Sai da yagama sannan ya dubeta da murmushi yace.

"Buɗe idon sarkin tsoro, kinci abinci kuwa?".

Kai ta girgiza alamun a'a kwantar da ita ya sake yi ya fice daga ɗakin da sauri.

Mintuna kaɗan ya dawo hannunsa ɗauke da jug cike da kunun gyaɗa da soyayyar wainar kwai a plat ya ajiye gefe ya zauna sosai kan gadon ya ɗagota yana mai bata kunun akan dole taci badan ranta naso ba, sai da taƙoshi sosai sannan ya bata magani ya mai da ita ya kwantar ya

faɗa toilet domin yin wanka.

***

Saima zaune bisaaya daga cikin kujerun falonta daya sha kayan alatu kala-kala tana kallonta cikin nishaɗi dajin daɗi Anwar yayi sallama ta amsa cike da fara'a tana faɗin.

"Sannu da zuwa" taanyi hug nasa  ya nemi guri ya zauna ita kuma ta fara gabatar masa da kayan abinci kala-kala tana faɗin.

"Na dai san cikinka ɗauke yake da yunwa".

"Kamar kin sani wallahi yau munsha yawo sosai da Fudhal danma na matsa dole abincin matata zan ci, sukayi dariya baki ɗayansu.

Tun randa aka kai Jalilah atsayin matar Ya Sayyadi Umar yayi amanna da irin halaccin da iyayenta sukayi masa ya karɓi Jalilah matsayin mata a gareshi hannu bibbiyu, sun fahimci juna sosai a daren duk da cewa Jalilan bata magana.

Ya Sayyadi Umar kuma yaci alwashin insha Allah zai nema mata Maganii duk a inda yake, domin tashi ɗaya yaji sonta fiye da yanda yaso Aynu domin Jalilah ma ba bayaba wajen  Iadabi da biyayya da sanin ya kamata ga uwa uba kyau domin zai iya cewa tafi Aynu kyau sabida jikinta a goge yake kuma ita fara ce.

(Tofa..! Masoyan Aynu shin kunyarda da batun Ya Sayyadi Jalilah tafi Aynu kyau kuwa?, kodai ya faɗa ne kawai domin ya rasata?).

*******

Aynu ce keta faman shige da fice domin haɗa musu kayan kalacin safe, Yarima Fudhal na zaune kan carpet da system a gabansa amma baki ɗaya hankalinsa nakan Aynu can dai ya kasa daurewa tana zuwa zata wuce domin shiga bedroom ɗinsu zata ɗauko wani abi yayi saurin janyota ta faɗo jikinsa Aynu ta rufe idonta da sauri domin bala'in kunyarsa take ji sosai.

"Buɗe idonki ki kalle ni".

Sake rintse idon tayi Fudhal yayi murmushi ya cikata daga riƙon da yayi mata yana faɗin.

"Wai har yaushe ne zaki daina jin kunya ta ne?".

Aynu ta miƙe da sauri tana murguɗa masa baki ta shige bedroom ɗin da gudu ya biyo ta yana faɗin.

"Idan na kamaki zakiyi bayani".

Basu tsaya ko ina ba sai kan gado, Fudhal ya hau yi mata wasa mai matuƙar rikitarwa kullum shi aikinsa kenan sai dai yayi wasa da ita son ransa ya rabu da ita , ita abin nasa har ya fara bata tsoro har Zee na faɗin ko ba shi da lafiya ne?.

BAYAN WATA ƊAYA...!.

°°°°

Yauma kamar yanda ya saba ya shafe tsayin lokuta yana wasa da ita kafin ya sauko daga kan gadon yana faɗin.

"Zoki gani Aynu".

Ta matso da sauri domin ta tsorata ta ɗauka wani abin ne.

Wani ɗan akwati taga ya miƙo mata yana buɗewa zobe ne ya baiyana a ciki sai walwali yake dan kyau.

Murmushi tayi tasa hannu ta karɓa cike da murna.

Yarima Fudhal shima murmushin yayi ya cire zoben daga cikin akwatin ya kamo hannunta ya sanya mata tare da yin kiss ɗin hannun yana faɗin.

"Mai yasa kike gayawa Zee har yanzu babu abin da ya shiga tsakanin mu?".

Aynu ta rufe idonta cike da kunya yasa hannunsa ya janye hannuwan nata suna duban juna yace.

"Nayi hakanne kawai ba dan rashin lafiya ba, kawai inason tabbatar miki da irin son da nake miki, wallahi Aynu zan iya ƙare tsayin rayuwa a tare dake ba tare da wani abu ya shiga tsakanimu ba sabida soyayya ta dake gaskiya ce amma...!".

Aynu ce tasanya tattausan hannunta ta to she masa baki kanta na ƙasa take faɗin.

"Na yarda wallahi Yarima, na yarda da son da kake min ba sai ka rantse ba duniyama ta shaida ba ni ba, ina Sonka kuma zan cigaba da sonka har ƙarshen rayuwa..!".

Kaiii...nima fa gaskiya aradu na antaya kogin soyayyar YARIMA FUDHAL kodai sakin Aynu zansa ayi ni a antaya ni lolll.

Wannan page ɗin nakine SHAFA'ATU UMAR inayinki nima irin sosai ɗinnan wallahi.

[12/12, 12:04 PM] NANAH FIRDAUSI😍😍❤️❤️😜: *YARIMA FUDHAL*

NA
QURRATUL-AYN.

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®.

SADAUKARWA:-NAMESY FIRDAUSY JEEBOR.

48.

BAYAN WATA UKU.

Kwance yake bisa doguwar kujera dake cikin falonnasu lokaci-lokaci yana ɗan riƙe cikinsa dakeyi masa ciwo, Safiyya na zaune can gefe hankalinta na kan TV ko kaɗan bata lura ba sai kawai ganin sa tayi ya faɗo kan carpet da sauri ta miƙe ta ƙarasa wajen sa tana faɗin.

"Lafiya Jaleel mai yake damunka?".

Shi dai ya riƙe ƙam faɗi yake a hankali.

"Cikina.! Wayyo ciki na..!".

Safiyya ta miƙe da gudu ta nufi wajen Fulani Sokoto a ruɗe ta shiga faɗon tana faɗa mata halin da Jaleel yake ciki da sauri sukayo waje zuwa ɓangaren su Safiyyan.

Shi kuwa sai faman malelekuwa yake yana ihun cikinsa suka ƙarasa kansa tuni Safiyya ta fara kuka Larai ce dake biye dasu ta sake ficewa a guje zuwa wajen Sarkin gida ta faɗa masa halin da ake ciki tuni ya nufi fada domin sanarwa sarki Ubaiyd.

Sarki Ubaiyd yace a fito dashi a kai shi asibiti, Magaji Saif dake zaune yamiƙe da sauri suka nufi cikin gidan tun zuwansa har yanzu bai koma ba Sokoto ba Sarki Ubaiyd yaƙi bari ya tafi.

Sarkin gida ne ya tallafoshi tare da Magaji Saif Safiyya ta biyosu tana kuka aka ce ta zauna Fulani Sokoto da Magaji Saif sune suka tafi kai shi asibitin.

Tuni ciwon Jaleel ya baza cikin gidan.

Yarima Fudhal kuwa basu san wainar da ake toyawa ba domin ko buɗe faɗonsu ba suyi ba ranar duk da cewa suna zaune faɗon.

Aynu na bisa cinyar Fudhal akwance shi kuwa ya dage wai tsifar kai yake mata Zee zata zo tayi mata kitso, suna hirarsu jefi-jefi cikin so da ƙauna abin dai abin sha'awa, bugun ƙofar faɗon da aka hau yine yasa Fudhal miƙewa yana faɗin.

"Waye?".

"Jakadiya ce".

Ta bashi amsa ya buɗe yana faɗin.

"Yadai lafiya kuwa?".

"Babu lafiya ranka ya daɗe, Fulani ce tace a gaya maka ka shirya zaka kaita asibiti yanzu aka tafi kai Jaleel".

"Jaleel kuma..! Mai ya sameshi?".

"Ciwon cikinsa ne ya tashi".

Yarima Fudhal yaɗan dafe kai kafin yace.

"Ina zuwa bari in shirya".

Jakadiyya ta koma shi kuma ya juya cikin falon yace da Aynu.

"Bari inyi wanka asibiti zamu".

Dake Aynu taji komai to kawai tace ya shige cikin bedroom dinsu ya barta nan falon tana cigaba da tsifarta.

Mintuna kaɗan sai gashi ya fito cikin sauri harya shirya yayi mata sallama ya fice zuwa part ɗin Hajiyartasu.

Ko da yaje ta shirya shikaɗai kawai take jira, yana shiga suka fito suka nufi inda motar take suka shige Fudhal yaja suka tafi.

Suna isa asibitin suka tadda Fulani Sokoto zaune gefe tayi jugum Magaji Saif na tsaye sai faman zarya yake, Hajiya ta nemi guri ta zauna Fudhal ya karasa inda Magaji Saif yake tsaye yana faɗin.

"Ina Jaleel ɗin?".

"Yana emergency".

"OK".

Abin da Fudhal yace kenan ya nufi ɗakin shima, domin asibitinsa ne kuma shine babban Doctor.

Bayan shigarsa sun shafe tsayin a wanni kafin su Fudhal su fito wujuga-wujuga dasu ya kalli Magaji Saif yace.

"Yana buƙatar akawo masa Safiyya".

"Me yasa wani abu ya sameshi ne".

"Aa adai kawotan tukunna".

Magaji Saif ya dubi driver yace.

"Yi maza kaje ka ɗauko Safiyya".

Driver ya miƙe da sauri ya fice domin cika umarnin Magaji Saif.

Yarima Fudhal ya koma cikin ɗakin da Jaleel yake ya zauna kawai yayi tagumi yana kallon halin da dan'uwannasa yake ciki.

Lokaci-lokaci yana duba agogon hannunsa yana jira yaga zuwansu Safiyya.

Magaji Saif ya buga ƙofar ɗakin Yarima Fudhal ya share kwallar dake kawo masa ya miƙe ya fita zuwa wajen har da Aynu ya gani tsaye ta biyo Safiyya.

Fudhal yace.

"Zaku iya shiga dukkan ku".

Ai kuwa tuni suka ɗure cikin ɗakin zuwa inda Jaleel ke kwance bisa gado abin tausayi.

Ya riƙe cikin sosai Safiyya tariƙo hannunsa tana faɗin .

"Sannu Allah ƙara sauƙi".

Jaleel ya juya yana kallonta hawaye nabin kuncinsa ya buɗe baki a hankali yace.

"Kiyi haƙuri Safiyya, ki kulamin da abin da yake cikin ki, ni bana da tabbacin zanga abin da zaki haifomin amma inaso ki kulamin da tarbiyarsa a hannunki, bana so ɗana ya taso hannun Mahaifiyarmu domin ina jin tsoron kada ta bashi irin tarbiyar data bamu ni da ƙanwata...!".

Yakai maganar yana mai kallon idon Fulani Sokoto dake tsaye gefe kunya duk ta cikata da maganar da Jaleel yake.

"Momy kece duk silar halin da nake ciki a yanzu kuma kece silar rasa bakin Jalilah duk nasan wannan, na tabbatar bada ban mugun nufinki nason halaka Fudhal da son a dole ni ne zanyi sarauta ba da duk hakan bata faruwa ba".

"Yanzu gashi tsananin son kanki mai yaja mana Momy?".

Magaji Saif ne ya ƙarasa wajen sa ya rufe bakinsa yana faɗin.

"Aa Jaleel mahaifiyarkuce fa kada kace haka ka yafe mata dukkan abin da tayimaka kaji domin nasan tayine cikin kuskure ka yafe mata na roƙeka wannan alfarmar".

Kai ya gyaɗa alamun to, yana duban Magaji Saif ya buɗe baki a hankali yace.

"Na yafe mata".

Yakai maganar da murmushi akan fuskarsa, ya sake ɗaga harshe yana salati sai gani sukayi

idonsa ya kafe akan Mahaifiyartasa har lokacin murmushin bai ɗauke daga kan fuskarsa ba.

Yarima Fudhal dake tsaye bakin ƙofa yana kallonsa sai yayi maza ya juya masa baya yana share kwalla, bai aune ba saijin mutum yayi a jikinsa yana shash-sheƙar kuka ya buɗe ido yaga ashe Aynu ce ƙara rungumeta yayi sosai yana share mata hawayen.

"Jaleel...!".

Kowa ya ɗago kai ya mai da dubansa inda sukaji ankira sunan Jaleel Magaji Saif dake rufe idanunsa tare da Jan mayafin dake kan gadon ya karasa lullbeshi yana duban wacce ke magana.

Jalilah ce tsaye bakin ƙofa tayi maganar kowa ya bita da kallo itama sai take kallon kan nata domin jin maganar tayi kamar ba daga bakinta take fita ba.

Ƙarasawa tayi da gudu ta buɗe mayafin da aka lulluɓe Jaleel dashi ganin da tayi baya numfashi hakan ya ƙara tabbatar mata da cewar ya mutu kenan?.

Da baya ta koma ta zube ƙasa tana rusar kuka Hajiyarsu Fudhal ta dafata tana faɗin.

"Kuyi hakuri Jalilah ba kuka zakuyi masa ba addu'a zakiyi masa kinji".

Jalilah ta share hawayenta tana yiwa Mahaifiyarsu Fulani Sokoto wani irin kallon tsana.

Fulani sokoto dake tsaye ƙame gefe ta kasa ɗaga harshenta tayi magana idonta ya bushe ƙam babu ko kwalla kukan zuci kawai take.

Jalilah ta ƙarasa wajenta tana kuka take faɗin.

"Kin gani ko Momy?, kin gani kinyi silar rasa ɗan'uwa na da munanan halayenki akan duniya kin zaɓi Jaleel ya mutu...!".

"Ba Jaleel aka zaɓa ba..! Ke aka zaba ki mutu..! kuma tabbas zaki mutu domin burin mahaifiyarku shine, ta raba auren ki da Umar ta raba Jaleel Safiyya ta raba Aynu da Fudhal

inyaso Fudhal ya auri Safiyya Jaleel kuma zai zama Magaji a bayan Mahaifinku".

Larai na kaiwa nan ta kece da wata irin mahaukaciyar dariya tana mai cigaba da faɗin.

"Boka yace dole akai ruhin Jalilah indai kina so Jaleel yayi sarauta inda dama ma sai a kashe Fudhal ko Hajiya haka kikace ai yanzu zanje infaɗa masa".

Saita kama rawa a wajen kowa jikinsa sai yayi sanyi aka mai da hankali wajen bin Fulani Sokoto da kallo Jalilah kuwa tuni ta yanke jiki ta faɗi ƙasa, Fudhal yazo ya ɗauke ta aka kaita can wani ɗaki domin taimakon gaggawa, ita kuma Larai yasa akayi waje da ita.

Domin tone-tone take tayi na irin abubuwan da suka dinga shiryawa Yarima Fudhal amma sai abin ya dinga komawa kan Yarima Jaleel.

Safiyya zaman daɓaro tayi tana risgar kukar rashin mijinta ga kuma wanna mugun jin da kunnuwanta suka jiye mata akan Momynsu Jaleel.

"Yanzu da tuni nine acikin wannan halin?, da tuni nike neman mata da shaye-shaye, Allah yajikanka Jaleel yanzu ga abin da shaye-shayen yaja maka ya illata kayan cikin ka har yayi sanadiyyar rasa ranka".

Yarima Fudhal keta wannan zancen aransa domin babu wanda yasan abin da yayi sanadiyyar mutuwar Jaleel da gashi dai sauran likitocin da sukayi masa aiki, kuma Fudhal ne ya gargaɗesu akan kasa su faɗa, sabida gujewa halin da zai shiga idan yaji tare da ƴan uwansa sai kuma gashi mai aukuwa ta auku.

ALLAH KENAN..! AISHI BA AZZALUMIN BAYINSA BANE, SUN MANTA DA CEWA YANA GANINSU,KUMA YANA JINSU, SUN MANTA DA CEWAR IDAN BABU DUNIYA AKWAI LAHIRA, ALLAH KASA MU DACE KASA MUFI ƘARFIN ZUCIYARMU AMIN.
[12/12, 12:28 PM] NANAH FIRDAUSI😍😍❤️❤️😜: *YARIMA FUDHAL*

NA
QURRATUL-AYN.

NAGARTA WRITERS ASSOCIATION®.

SADAUKARWA:-NANESY FIRDAUSI JEBOR.

49.

Nan dai aka fice da gawar Jaleel aka tafi kai shi gida domin ayi masa wanka akaishi makwancinsa.

Gimbiya Safiyya tayi kuka iya kuka domin iya kacin kwanakinta da Jaleel sun shaƙu fiye da tunanin duk inda tunanin mutum zai kai.

Magaji Saif kuwa hankalina gaza kwanciya yayi daga abin da Larai ta faɗa hakan yasa yana fita daga asibiti bai wuce gida ba sai wajen wani malami da yasani masanin fiƙihu sosai ya zaiyane masa dukkan abin da ake ciki, malamin yace idan da dama suje yaga Jalilah .

Babu musu Magaji Saif ya ɗauki Malam har cikin ɗakin da Jalilah ke kwance asibitin suna shiga malamin ya ƙare mata kallo yace.

"Tabbas gaskiya suka faɗa, amma ka kwantar da hankalinki insha Allahu babu abin da zai faru daga gareta".

Malamin ya nemi guri ya zauna ya buɗe alqur'ani ya fara karantawa Magaji Saif ya nemi guri ya zauna, malamin ya shafe kusan awa guda yana karatun kafin ya rufe Qur'an ɗin ya buɗe jakarsa ya ɗauko wani ruwan rubutu ya nufi inda Jalilah take kwance ya zuwa rubutun a hannunsa ya yarfa mata sau uku saiga wani Koran hayaƙi na fita daga jikinta yana gama fita ya kuma watsa mata tayi wata irin atishawa tare da ajiyar zuciya.

Malamin ya dubi Magaji Saif yace.

"Insha Allah babu abin da zai faru, sai dai a gaya mata ta dage da azkar da tsayuwar dare tare da yawaita salati ga Annabi Muhammad (S. A.W)".

"Domin da yawanmu mu mutane muna shagala da duniya sosai mu manta abin da Allah da Manzonsa sukace, waɗannan abubuwa dana lissafa ba karamar kariya bace garemu, ga kuma dumbin lada da zamu samu bayan wannan ta dalilin yinsu sai ka ka samu aljana Allah dai yasa mu dace".

"Amin ya Allah".

"Mungode sosai malam muje in ajiyeka gida zan wuce jana'izar Yayanta ne anata jirana".

"Aa muje tare mana, inyaso na koma ni kaɗai".

Ko da suka isa anyi masa wanka da komai, su kawai ake jira suna zuwa aka sallaceshi aka ɗaukeshi zuwa gidansa na gaskiya gidan da dukkan wani mai rai dole ne sai ya shige shi.

Su Zee dasu Baba ta Sallah Umman Aynu da Babanta duk tawowa sukayi gidan domin zaman makoki, Aynu tayi kuka sosai da mutuwar Jaleel, Fudhal kuwa zan iya cewa yafi kowa damuwa musamman inya tuna ata dalilin ƙiyayyarsa da Fulani Sokoto keyi masa ya rasa ransa yakanji duniyar tayi masa zafi sosai danma ana tausarsa sabida shima Gawa taƙi rami ne.

Har Jaleel ya cika kwana uku amma Fulani Sokoto bata umm bata um-um, Jalilah ta warke garas abinta sai dai baki ɗaya ta bar part ɗin Mahaifiyarta ta koma wajen Hajiyarsu Fudhal, Hajiya tayita yi mata faɗa akan ta daina fushi da mahaifiyarta sai dai kawai tace.

"Ni ba fushi nake da ita ba kawai banajin daɗin ganin halin da take ciki ne".

Har akayi sadakar bakwai kowa ya watse ranar Magaji Saif ya shirya meeting da dare baki ɗaya mutanan gidan kafin masu aure su tafi gida.

Magaji Saif yayi musu masiha sosai nasiha mai ratsa zuciya babu Wanda bai yi kuka ba a wajen musamman ma Jalilah wanda duk nasihar akanta ne sabida fushin da take ga mahaifiyarta take aka sanya ta ta nemi gafarta duk da cewa Fulanin bata magana.

Taro ya watse cikin jin daɗi sosai duk da cewar mutuwar Jaleel ta zame musu wani babban giɓi a garesu amma nasihar Magaji Saif yasanya zuciyoyinsu samun nutsuwa da hakuri tare da salama.

***

BAYAN WASU WATANNI.

Gimbiya Safiyya ta haifi ɗanta namiji an sanya masa sunan Yarima Jaleel, ba'ayi wani taron suna ba sabida yanda haihuwar yaron da sunan da aka saka yake tunawa da dukkan ƴan gidan rasuwar Jaleel, shiyasa Mai Martaba yace babu taron da za'ayi azo a zauna ana faman koke-koke, yasa aka ɗauki Safiyya aka kai gida domin tayi wanka a gida.

Al'amarin Fulani Sokoto sai abin da yaƙaru yanzu bata magana ko kaɗan sai dai kawai ido, ɓangarenta ya ɓaɓe yanzu duk taron jama'ar nan babu sai ƴan ragowar masuyi mata shara da ɗan goge-goge, idan ka ganta yanzu a bar tausayi tayi wani irin baƙi da rama kwalliyarnan duk babu, danma Jalilah na zuwa lokaci-lokaci dubata.

Yanzu kuma gashi cikin Jalilah ya tsufa sai dai Aynu ita ke zuwa kullum tayi mata dukkan abin da take buƙata ta dawo part ɗinta.

Yanzu tsakanin Saima da Aynu wani zumunci ake mai ƙarfi Saima ta ƙara tabbatarwa Yarima Fudhal na Aynu ne dole dukkan mata su haƙura duk da irin ƙaunar da suke masa kuwa, domin shi babu wata mace dake gabansa wacce ta wuce Aynu.

Ansanya bikin Zee wata huɗu masu zuwa tare da wani malamin makarantar primary dake can

ƙasan unguwarsu, murna agun Aynu ba zata faɗu ba domin dama ita burinta ayanzu bai wuce taga auren Zee ba.

Magaji Saif wani danƙareren gida ya bawa iyayen Aynu suka koma ya buɗewa Babanta ƙaton shago cike da kayan masarufi yana siyarwa.

Ashe a rasuwar Yarima Jalil Magaji Saif yaga Babarsu Zee yaji tayi masa zai iya aurenta kasancewar Mahaifinsu Zee ya daɗe da rasuwa tun suna yara kuma ba ta sakeyin wani auren ba sai yanzu da Magaji Saif ya ganta ya koma nace aurenta zaiyi.

Nan da nan aka sanya aure sati biyu masu zuwa tare da taimakon shawarwarin Umman Aynu domin da Baba ta Sallah ƙin amincewa tayi sai da Umman Aynu tayi ta mata nasiha sannan tace ta amince ya turo.

Anyi bikin girma da karamci Baba ta Sallah ta tare a cikin gidansu Magaji Saif wato gidan sarauta Aynu ba ƙaramin daɗi hakan yayi mata ba yanzu gata ga nata a kusa ai dole tafi kowa jin daɗi, gashi bikin Zee ma anan za'ayi sabida baki ɗaya suka dawo gidan ko yaushe Aynu na tare da Zee suna bawa juna shawarwari a tattare da su.

Yarima Fudhal ya mai da hankali sosai kan aikinsa, idan ya dawo kuma yakan zaunar da Aynu yana koya mata abubuwan da bata sani ba na addini da na boko ganin tayi zurfi sosai shi kuma aiki ya sakoshi gaba yanzu ya yanke hukuncin samo mata mai yi mata lesson kafin ya sanyata School, domin so yake kafin ta shiga tasan komai data shiga akaita SS 2 ko 3 sabida tayi exam nan da nan ta wuce university.

Hakan ba ƙaramin daɗi yake yi mata ba kullum ta zauna labarin kenan makaranta Zee tace.

"Nifa labarin skull ɗin nan ya fara isa ta mudai kawai muji labarin 'yan takwaye".

Aynu tayi dariya yana faɗin.

"Ba yanzu ba sai mum morewa amarcinmu".

Suka sanya dariya baki ɗayansu, Yarima Fudhal dake tsaye bakin ƙofa yayi sallam tafi nawa basu ji shi ba suna hira shima dariyar yayi.

Dariyar tasa sukaji suka juya Zee tace.

"Au ashe kana tsaye?".

"E mana duk inajin hiran taku ai".

Sukayi dariya dukansu Zee tayi musu sallama ta fice, Yarima Fudhal ya riƙo Aynu tare da rungumeta yace.

"Nima fa inason yaran nan da zaki ce ba yanzu ba so nakema tashin farko ki haifamin ƴan uku".

Aynu ta zaro ido waje.

"Haba dai uku ƙaramata dani ina laifin ɗayan ma".

"Ohh kinaso kema kenan?".

Aynu ta sanya kanta cikin ƙirjinta alamun kunya.

Dariya yayi yana mai kai bakinsa cikin kunnenta yace.

"Zo muje in baki yau tunda kin shirya".

Aynu sai ji tayi ya ɗauke ta cak sai other room

ALHAMDULILLAHI....!.

Nan muka kawo ƙarshen wannan book mai suna YARIMA FUDHAL.

Abin da muka faɗa dai-dai Allah yasa ya amfani al'umma, wanda mukayi kuskure kuma Allah ya gafarta mana amin.

GODIYATA A GAREKU.

Mungode sosai sosai abisa ƙoƙarinku agaremu na ganin ci gaban kungiyarmu Allah ya saka da alkhairi ya biya Ku amin.

MaryamulAbdul Kwaiseh

Adda Benaxer
Hauwa m. Jebo.
Aunty lubie mai tafsir.
Firdausi sodangi.

WANNAN BOOK SADAUKARWANE AGAREKI DUKA.

NAMESY :-FIRDAUSY JEEBOR

ALLAH YA BAR ƘAUNA.

MASOYANA.

A ko ina kuke ina miƙo gaisuwata tare da ɗumbin ƙaunarku nima kamar yanda kuke nunamin.

Zaku ji cigaban book ɗin YARIMA FUDHAL cikin BOOK mai zuwa muku nan da wani lokaci mai suna ZUCIYA DA HAWAYE wanda Document zai zo muku basai kun jira post ba.
An dauko wannan littafi daga shafin www.dlhausanovels.com.ng ku ziyarci shafin na www.dlhausanovels.com.ng domin samun kayatattun littatafan hausa kama daga kan na yake yake dana soyayya

Marubuci ko marubuciya zasu iya turo mana da littatafansu mu dora masu a shafinmu kyauta don masoyansu su rika Downloading a online,

Sannan marubuta zasu iya turo mana da tarihin rahuwarsu da tarihin rubutunsu, dama sharhin littatafansu don masoyansu su gani kuma su karu da hakan
Domin turo mana da littafi ko tarihin rayuwar marubuci ko marubuciya sai ayi mana magana ta whatssap da wannan nambar +2348140419490

A lura dakyau - kyauta muke saka littafi a shafinmu bama amsan ko sisin marubuci, duk wanda ya amshi kudinku da sunanmu babu ruwanmu,

Alura dakyau - manazarta bama tura littafi ta private ku dena binmu private kuna neman mu tura maku littafi, duk mai bukatar littafi yaje website namu

Alura da kyau - Littatfanmu suna fitowa cikin manhajoji uku ne PDF,TXT da DOC amman munfi amfani da PDF da TXT masu amfani da wayar android ko tablet ko computer zai fi kyau ku riga dauko PDF da DOC

Masu amfani da kananan wayoyi java ko mara java TXT zakuna zaba don shine daidai wayarku

This hausa novel was uploaded and downloaded from www.dlhausanovels.com.ng
You can download more hausa novels there
Also you can send us your novel to upload it in our website for your fans to download it online
It is free we do not charge for uploading novel
Also if you are an Author be it online or Non online you can send us your biography including your book summary,commentary and others via this number +2348140419490 its free we do not charge for our services

Note that - we do not charge for our services we uploaded novels and posted biography free, any person that collect your money in our name is your fault do not blame us

Note that - pls readers stop calling us and be asking us to send you a novels we are not sending

novels through whatssap or private our novels is public at any day, any time you can visits our site and download it

Note that - our ebooks came as PDF,TXT or DOC format but the popular format are PDF or TXT, those with android or tablet or pc we suggest you to download PDF or DOC
those with java phone or non-java phone we recommend you to download TXT

—

NAGODE BYEEE.